[1/1, 14:07] Nrs Zainab A S: ALKAWARI BAYAN RAI SHIMFIDA

Na sha tambayar kaina mai ya sa wasu mutane, ko ko in ce Hausawa, ke daukar matsalar banbancin kabilanci, addini da al'ada da matukar zafi, har hakan ya shafi rayuwar yaron da aka haifa?

A ganina duk auren da aka gina a matsayin aure na addini, aka kuma bi ka’idar da addini ya shimfida wajen yin sa aure ne, da ya cancanci a karbe shi kamar sauran aurarraki, a kuma karbi dan da amana kamar sauran 'ya'ya ba tare da la’akari da wadannan banbance-banbancen ba. Amma ni ba haka bane a tunani da ra'ayin dangin mahaifina ba.

Ni dai na taso da tabbacin Baffa Jibir ne kadai ke so na. Bani da kamar Baffa. Don haka har kullum nake kara bin shi da addu'ar tsahon rai da lafiya dauwamammiya.

Ba wai Baffa ne kadai nake da shi a duniya ba, a'ah, ina da kannen Uba, wadanda ban san da sunan da zan kira su ba. Sai dai in ce tsana da tsangwamar da suke yi min, yana da nasaba ne daga mahaifiyata da su ke ce dan'uwan su ya guje su a dalilinta.

Duk da haka ina jin dadin rayuwar tawa a hakan. Rayuwar 'talle’ ba? Idan an dawo makaranta. Yo me ya kai ta dadi a wajen yaron karkara? Abubuwa iri daban-daban babu wanda Inna Laminde ba ta dora mini.Tun daga kan dafaffiyar gurjiya, rogo, dafaffen makani, kumurci, soyayyar gyada (marau-marau), tubis-tubis da dangogin su. Da abin ya ci gaba ne aka koma dafaffen kwai. Babu kuma abin da Inna za ta dora min ban siyar na kawo mata cikakkun kudi da faranti ba.

Don haka Inna take tsammanin ko wani maqarqashiya nake da shi na samun ciniki? Ta sha cewa, loko ake ja na ayi min juye a bani kudi, koko ta ce maza ke ja na zaure. Wanda a zahiri ba haka bane, mutanen gari kadai ke so na,a sabili da banbancin kalar fata da gashin kaina.Wanda ya banbanta da nasu. Don haka ne sau tari suke rububin sayen abin hannu na.

Babu yadda Baffa bai yi da ita akan ta dena dora min tallan nan ba, sai ta ce, kudin kayan aurena nake tarawa da kaina. Idan ba haka ba uban wa nake tsammanin zai yi min kayan dakin? Baffa bai da 'ya mace, kuma ba zai fara a kaina ba.

Yo meye amfanin diya mace a karkara? Idan ba ta yi talla ta samo abubuwa guda biyu ba? Mijin aure da kudin kayan daki? Ko ita ta haifi mace iyakacin gatan da za ta

yi mata ke nan. Amma kullum Baffa ya ce, ba ta yi dai-dai ba, don ana son a goranta mata cewa ni din ba 'yarta ba ce.

Iyayen nawa na so na, suka watsar dani suka haure? Don haka idan ba a gode mata ba, to ba za a kushe mata ba.

Baffa kan ce "Amma sabida Allah Laminde, ba ki ganin hakan ya tauye karatun muhammadiyyarta?" Sai ta ce

"Idan ba za ka gode min ba, to ka dauke ta ka kaita duk duniyar da kake tunanin dai-dai ne da rayuwarta!".

Sai ya murmusa ya koma ba ta hakuri. Don daga ni har shi bamu da wata powerin dai akan Inna Laminde ne.

****

"Gafara dai! Gafara dai!! Ko masu gidan basa nan ne?"

Daga can kuryar daki Laminde ta amsa, "Muna nan, karaso ciki Hajiya Hajara".

Ta ce "Dadina da ke Laminde daukar murya".

Ta yi murmushi, a dai-dai lokacin da ta rage tsawon ta don shigowa dakin wanda ke dauke da'yar kankanuwar kofa, tun irin ginin nan na iyayenmu da kakanninmu.

Laminde ta ce "Mutanan birni ke nan, ashe talaka na ganin ku?"

Ta ce "Sai idan talakan bai so ba".

Ta zauna bisa tabarmar karaunin da ke shimfide tsakar dakin suka soma gaisawa, gaisuwa irin ta kanwar miji da matar wa da suka dade ba su ga juna ba.

Dai-dai lokacin na dawo, duk kafafuna sunyi futuk. Na aje farantin na karasa dakin da sallama, don in mikawa Inna cinikinta na kwan zabbi da na sayar tas. Zuwa lokacin zuciyata fari kal take, don na tabbatar yau zan samu abinci in ci in koshi, tun

da na sai da kwan duka. Gobe kuma ranar fita da gasara ne, wadda kuma ba kasafai nake sayarwa duka ba.

A tsarin Inna Laminde kuma, iya yawan cinikina, iya yawan abincina.

Har kasa na tsuguna ina mikawa Inna kudi, ba tare da na lura da Yaya Hajara da ke zaune a gefe ba. Ba ta karbi kudin ba ta bi ni da kallo, kana ta jinjina kai cikin takaici, ta ce "Lanto!".Na ce "Na'am Inna".

Ta kama kunnuwana duka ta murde iya karfinta, ta ce "Har yaushe ne?

Kullum ina gaya miki in za ki fita tallan nan ki dinga daura zanin arziki kin ki., kin nacewa wannan kodadden bambalastan, kina min bakin ciki kada ki samo min wanda zai kawar da ke. To ni na gaji, da rikon mai kama da maraya, komi na yi a ce ban yi dai-dai ba, ko kin ki, ko kin so, aure zan sa ubanki ya yi miki in huta. Allah ya gani na gaji, na yi iya bakin kokari na".

Ban tanka ba, har ta gama sababin ta uffan ban ce mata ba. '”Bace min da gani, tun ban yi kwallon albarka da ke ba". Ko kafin ta idasa maganar ta, tuni na wuce, don na san kadan da aikinta.

Kicin na wuce na samu abincina an rufe da faifai. Nan na zauna akan dutsen da Inna ke amfani da shi wajen girki, na soma cin abincin, danwake ne da mai da yaji, an yayyanka tumatir da albasa a kai. Na tsince albasar na zubar, kana na soma ci.

Daga nan inda nake ina jiyo sauran bala'in Inna, duk akan rikon mai kama da marainiya da aka dora mata, ga shi na rasa miji, ta rasa yanda za ta yi da ni.

Yaya Hajara ta kyabe baki ta ce "Ba don kar a ce na yi karambani ba, koko a ce nima din bani da kirki, da sai in ce ki kaita wanke-wanke da shara birni kawai ki huta, don ni kam ba zan daurawa mijina rikon da Allah bai sa shi ba. Nima ‘ya’ya ne a gabana ba daya ba ba biyu ba, don haka bana neman kari. Can ma kuma kinga ai neman mijin ne, ga kuma kudi da za su ba ta duk wata ki samu na yi mata kayan dakin".

Laminde ta ce "Wannan Uban nata da ke sonta fiye da 'ya'yansa zai amince ne?"

Hajara ta ce "Barni da shi". Ta ce

"Ni yadda yake kaffa-kaffa da ita ai ya fi Uban da ya haife ta. Idan ba ta je birni ta yi wanke-wanke da sharar ba ni ban ga amfanin ta ba, tun da bakin jini gare ta, babu wanda ya taba shinshina ta.

Babban tsoro na ma ko wasu na janta zaure, ta yo ciki a dora min jafa'in da ban ji ba, ban gani ba. Gara dai ku dangin nata....."

"Dangin wa?" Hajara ta tare ta... "Ba dai ni Hajaru ba, don ni ban hada dangi da jinin yahudawa.....".

"Au....abin haka ne? Shi ne ni kuka hada mini? To ku san yadda za ku yi da kayar ku, amma wallahi ba zan rike ba, nayi na Allah nayi na annabi, wanda na daure ma nayi tsayin shekaru goma da doriya, Allah ya amfana!".

Dariya ta kama Hajara, ta yi mai isarta ta ce, "Shekaru goma kina rike da kayarki Laminde,babu wanda ya taba jin kan ku, ki daure ki karasa ladan ki.....shekaru nawa ya rage a kaita gidan miji? Musamman ku nan a kauye?".

Ta ce "In wannan ladan ne ban so, kuma nace dake bakin-jini gareta ba wanda ya taba shinshina ta, ku dau abinku ku karata da ita, ba neman diya mace nake ba don ina haifar maza". Hajara tace

“ki bar lamarin a hannu na, dama wata ‘yar uwar Baban su Hauwa’u na ji tana cigiyar yarinya kamar ta”.

Yaya Hajara ce a dakin Baffa, ta kwantar da murya cikin hikima tana rokon sa ya ba ta Lanto, za ta rike mishi amana, za kuma ta samar mata aikin yi a can Kano.

Baffa ya ce "Aikin yi? Wane irin aikin yi? Da dai makaranta za ki sanya ta Hajara da na fi jin dadi. Shekaruna sun tura, ina da burin samar ma Lanto, kyakkyawar rayuwa kafin in bar duniya, da abin da za ta dogara da shi, ko da ba ta tadda samun ganin iyayenta ba".

Sai Hajara ta koma lallami cikin ha'inci, ta tabbatar mishi cewa ba za ta bar wata rayuwa maras kyau ta faru da Lanto ba, ita ma tana da hakki a kanta.

Dole Baffa ya yarda, ya umarce ni da in hada kayana mu koma tare da Yaya Hajara. Hajara ta ce "Ai sai zuwa gobe za mu wuce, ba ta gama halartar 'yan'uwa ba".

Da daddare Baffa ya kirani, na koma gefe na zauna cike da damuwa, wanda kullum ya ke bina da ban hakuri kan in jure, wata rana sai labari da halin matarsa.

Ya ce "Lanto ki kara hakuri akan naki na da da rayuwa, wata rana sai labari, nima hakuri nake yi da ita, saboda 'ya'yanta, ta zame min dole. Duk abin da ya yi farko yana da karshe, duk yadda za ta yi dani ba zan taba ba da ke auran sadaka ba, yadda take so, sai sadda Allah ya kawo miki miji mai son ki, mai kaunarki.

Ai alhakinki ke bibiyar ta, ga nata 'ya'yan nan duk sun ki karatu, sai gantali a titi, ke kuma da ta hana karatun Islamiyyah ko a gidan mijinki idan kina da rabo sai ki yi, tun da kin samu ilmin firamare ai an gode Allah, daga kowanne mataki na rayuwa za ki iya dorawa".

Ire-iren maganganun Baffa ke nan gare ni a kullum, idan ya ganni cikin damuwa. Kowa ya san dai shi din bai je makarantar boko ba, amma cudanyar shi da al'umma daban-daban, ya sanya kanshi a waje yake, wato,abin nufi, ya san abubuwa na zamani da dama.

Na mike zan fita, bayan na yi wa Baffa sallama, a bakin kofa muka yi karo garammm! Ni da ita, ta ce"To ka da ni ki ji dadi". Na ce "Allah ya ba ki hakuri, Inna".

Kwana na yi ina tunanin wannan sabon al'amari, watau bin Yaya Hajara birni. Kafatanin dangin mahaifina babu wanda ya fi tsanata irin Yaya Hajara, na san kuma ba ta nufi na da alheri a wannan tafiya. Don ba tun yau ba Laminden ta ke mata tayin ta dauke nin tana ki, duk akan kiyayyar ta ga mahaifiya ta.

Sai yanzu kuma rana tsaka, ina auna wacce irin rayuwa zan yi da Yaya Hajara, wadda a zahiri ta nuna min ba tun yau ba bata kauna ta.

Karfe goma na safe na shiga don in yi wa Baffa sallama. Eh, a wurina Baba ne, tun da wan Babana ne. Dogom mutum mai babbar sura, wato babban jiki. Kowa ya kwana ya tashi a kauyen Bujawa, ya san Mallam Baffa Jibir Bujawa, saboda shahara da ya yi akan sana'arshi ta kiwo yana sayarwa. Wadda ya girma ya tashi a kanta.

Can na iske, Inna Laminde, ta kai mishi abin karyawa, na tsinkayi kalaman ta na karshe.

"Me zan yi da abin da za ta samo? Illa iyaka in mata tarin aure da su, duk da dai ake cewa bani da kirkin ban iya zalama ba sai neman zama lafiya. Idan kuwa yarinyar nan tana cikin gidan nan, ba zan taba zama lafiya ba,.....

Kai ana nuna maka samun sauki kana kawo qabli da ba’adi, wa ya ki rayuwar sauki?'

Baffa ya ce "ba na son saukin, ni nafi son a bar min ‘ya ta nan a gabana, nafi amincewa, banda dai da ni da Hajara duk daya ne.....shine kawai yasa na amince, amma ba don ina neman wani sauki ba. Ita dinnan kwaya tal ta fiye min taron yuyuyin ki, koko in ce taron tsintsiya ba shara. Ba don Hajara bace wallahi da bazan amince ba”.

Wani sanyi ya tsirga a zuciyata, domin idan da akwai abin da nake so a rayuwata, a halin yanzu bai wuce barin gidan nan ba, ko don kunnuwana su huta, su sami rangwame daga sababi da bakaken maganganunta, wadanda take saki babu kunya, babu kawaici a kunnuwana.

Baffa ya ci gaba da cewa

"Don ba zan bari ba Lanto, a yi miki abin da ba kya so ba, domin ke din nan duk da nake wan mahaifinki, amana ce ke a hannuna, wadda idan na ci ko ya ya sai Allah ya hukunta ni".

Na ce, kaina na sunkuye

"Na amince Baffa, da kai da Yaya Hajara ai duk daya ne".

Ya ce "To Allah ya sa hakan alherin mu ne baki daya".

Haka na ci gaba da sake-saken abin da zan je in taras a gaba a cikin raina. Allah ya sa hakan alherin nawa ne kamar yadda Baffa ya ke fata.

** **

Karfe goma na safe muka bar Bujawa ni da Yaya Hajara a motar mijin ta, kayana cike taf cikin shudiyar Ghana Must Go, kafin karfe daya mun iso Kanon Dabo, Jalla babbar Hausa, yaro ko da me ka zo an fi ka. Direba na jan mu. Ni dai na san Yaya Hajara mazauniyar garin Jos ce ita da mijinta da 'ya'yanta, don haka na sha mamaki da na ganmu a Kano. Ba don na san Kano bane, a'a, sai don ji da na yi suna furtawa ita da direbanta.

Kamin mu taho sai da Baffa ya kara kira na dakin sa ya ci gaba da yi min nasihar na zauna da kowa lafiya, in kiyaye sallah, in kyautata alaka ta da kowa.

Shiga nan, bulla can direban ya iso gida mai lamba ashirin da daya a cikin Nassarawa G.R.A. Gidan yana nan a Abbas Road kwatankwacin sauran gidajen manyan ma'aikatan gwamnati da ke layin. Muka fito muka karasa ciki.

Allah sarki, me zumunci ya zama ne a wannan zamanin? Ko da ya ke a cewar su (dangin mahaifina) suna da hujja.

Yaya Hajara da ta ke matsayin kanwa ga mahaifina, ba za ta iya rike ni cikin iyalinta ba, ta gwammace ta kawo ni gidan dangin mijinta in yi ta aikatau. In hakan ta faru su dai sun rabu da alakaqai sun huta.

Tarba ta mutunci matar ta yi mana, tana lale da mu. Ta danna wani abu sai ga wata dattijiya ta fito daga wata kofa da na yi tsammanin madafi (kichin) ne, sakamakon qamshin girkin abinci da ke busowa daga kofar, da ya bakunci hancinan mu.

Ta umarce ta da ta kawo mana dan abin jiqa makoshi.

Suka ci gaba da tattaunawa a kaina ita da Yaya Hajara, ga dukkan alamu sun jima da sanin juna, to alhamdulillahi na samu karbuwa wajen uwargijiyar tawa.

Sai bayan la'asar Yaya Hajara ta yi shirin tafiya, tana mai kara ja min kunne kan yiwa uwargijiyata biyayya.

A cikin hirar tasu ne na fahimci cewa, a wani biki ne da suka hadu ita da Hajiyar ta ce da Yaya Hajara idan ta je kauyensu ta samo mata 'yar yarinya karama da za ta dinga taimaka mata. Na kuma fahimci ita matar gidan dangin mijin Yaya Hajara ne.

Bayan fitar Yaya Hajara muka yi shiru daga ni har ita, tana ta danne-danne cikin wannan wayar ta zamani, wadda ko a Bujawa na ga ta zama ruwan dare. Sai da ta kare ta kira wannan dattijiyar ta ce "Sunanta Baba Larai, za ku zauna tare, sai dai kowanen ku aikin shi daban.

Tana kula da kichin ne, ke kuma ba zan ce ga hakikanin aikinki a cikin gidan nan ba. Bayan taya Baba Larai aiyuka da wanke-wanke da share-share, akwai kula da yara.

Babban aikin ki shi ne shirya su kullum da abincin da za su tafi da shi makaranta, duk Baba Larai za ta koya miki har ki saba. Sunana Hajiya Fatima-Binta, ke kuma fa?" Na ce,

"Lanto".

Ban taba haduwa da mutumin da na ji ya shiga raina farat daya irin Hajiya Fatima-Binta ba, ga dai kirki ga fara'a, ga mutunci da saukin kai, sune halayen da na fassarata da su a lokaci daya.

Ta ci gaba da cewa "Za ku zauna daki daya da Baba Larai, ki kula da kanki, ki kula da tsafta sai mu yi zaman mu lafiya mu taimaki juna. Yarana duka kanana ne, suna bukatar wata wadda za ta dinga kulawa da al'amarin su bayan ni a ko,'ina.

Ni 'yar kasuwa ce, ina da manyan hidimomi a kaina shi ne dalili. Ina fatan za ki zauna damu cikin amana mu hadu mu taimaki juna?"

A hankali na ce "Na yi wannan alkawarin Hajiya.....". Ban idasa rufe baki ba suka yiwa falon tsinke, suna ta tadin su na yara 'ya'yan gata. Duk suka baibaye Hajiya suna ta shara mata labarin abubuwan da suka faru da su a yau. Ta ce

"To ga kawa na kawo muku, kuna so ko ba kwa so?"

Gaba daya suka juyo suka dube ni, babban ya yamutsa fuska, sauran ukun suka amsa cikin jin dadi "Muna so, Mami".

A kyamace babban ya ce

"But she is dirty Mami?”

Ta yi murmushi, "Cikin kwana biyu za ta yi fes, Mukhlis".

Ya kyabe baki "In dai wannan ce kawar da kika ce za ki nemo, to bana so, ina da kawaye na a school sun ishe ni".

"Kaifa Muslim?"

"Ni ina son ta Mami".

"Huda fa?"

Ta ce, "Nima ina sonta Mami, za ta goya ni irin goyon da Baba Larai ke min?"

Ta ce, "Kin yi girma da goyo, Baba Larai ma ta tsufa balle ta goya ki, balle wannan 'yar mitsitsiyar? Nour fa?"

Da ganinta ka ga 'yar auta, saboda yadda ta bi take lafe jikin Mamin, ta ja bakinta ta tsuke ba ta ce komi ba, duk sai ta ba su dariya. Daga nan ta umarci Baba Larai da raka ni dakin mu in ci abinci in huta.

A hankali Baba Larai ke koyar dani duk abubuwan da Mami ta ce a koya min, musamman shirin su Nour zuwa makaranta.

Cikin sati daya kacal na gane komi ta fannin kula da su wajen tafiya makaranta da shirya musu abinci cikin akwatin tafiyar su (lunch box), saboda Mami ba ta fitowa sai karfe goma.

Ban da abu irin na su na masu akwai, ni ban ga wani aiki a nan ba da har sai an nemi mai yi. Amma ga Mamin tana ganin hakan taimako ne ake mata, tun da kuwa yanzu ga shi tana samu ta yi baccinta mai isar ta.

Mun shaku da Nour da Huda sosai, cikin 'yan kwanaki kalilan, na rasa mene ne dalilin da ya sa Mukhlis ya ki jini na, tun da in dai don qazanta ce yanzu bana tare da ita, na yi fes na yi shar kamar ba ni ba. Kyawuna ya bayyana a sarari, hatta sabulun wanka na musamman Mami ta sai mini, wanda daga kwalinshi na lura ya fi na Baba Larai mukami.

Cikin watanni biyu kacal na zama 'yar gida, na yi dace da uwar daki ta gari, kuma ta qwarai mai nuna nata ba nata bane, ta hada ni da 'ya'yanta duka ta rike tsakani da Allah.

Duk wani abu da zai bata ni a wurin wannan iyali ina gudun shi, don haka ne na zamo mai kaffa-kaffa da al'amarina. Ba na shiga shirgin Mukhlis ko kadan, shima ba ya shiga nawa shirgin. Zama da su sau dubun-dubata ya fiye min zama da Inna Laminde ta kowanne fanni, na kuma kara zage damtse wajen kyautatawa Mukhlis dan kimanin shekaru goma sha hudu, kuma babban da ga Mami.

Bana jin kiwar yi wa Mami kowane abu da ta sa ni in yi, don a gani na ‘as rainon kauye as I am’ zan iya yin fiye da haka, kafin nan ma, ita ba ta sani abin da ya fi karfina.

A shekara guda kacal ni kaina na san na samu sauyin rayuwa da ci gaba ta kowanne bangare, don Mami ta umarce ni da in dinga zama wajen lesson din su da yamma wanda wani Bayerabe yake zuwa kullum daga karfe hudu zuwa shida, wato bayan sun dawo makarantar boko sun huta.

Ba zan iya cewa ga hakikanin shekarun Mami ba, sakamakon alamun jin dadi da suka boye hakan, suka mai da ita kamar 'yar shekaru ashirin da biyar, bayan a zahiri ta baiwa talatin baya.

A kullum kalaman Mami gare ni su ne.

"Jin ki nake kamar 'yar da na tsugunna na haifa Lanto, ki ci gaba da zama dani da iyalina cikin amana".

Ranar wata lahadi mun dawo daga daukar lesson, kowa ya kama harkokin gabansa, Mami na lura yau sai bi na take da kallo duk in da na gitta. Ta kare ta ce "Lanto zo nan".

Na matsa na zauna bisa carpet a gabanta, a ya yin da take zaune cikin lintsimemiyar kujerar falon. Ta ce

"So nake ki bani tarihin ki a taqaice".

Nan da nan hawaye suka balle, yi nake ba sassautawa. Ta ce "Ba kuka na kira ki ki yi min ba, ina so ne in sani su waye iyayenki na hakiqa, don mutumin da ke zuwa duba ki nan (Baffa) jiki na ya bani ba Babanki bane. Haka Hajara idan 'yar'uwar mahaifinki ce ta hakiqa, zuwa yanzu ya dace a ce ta waiwaye ki, at least ta ji lafiyar abin da ta kawo ta ajiye, ko da ba mutum bane……".

Na ce

"Eh, Baffa ba Babana bane, mariki na ne kuma wan mahaifina".

"Wan Uba na asali?"

"Nima ban sani ba, na dai taso na ganni tare da shi, yana kyautata mini, kamar diyar cikinsa, ko ma in ce, fiye".

"Kuma bai taba gaya miki su waye iyayen naki ba?"

"Bamu taba yin irin wannan hirar da shi ba, ya dai ce mini iyayena suna raye, sai dai shima bai san inda suke ba".

"'Yan wane gari ne?'

"Ya ce dani Mamana daga kasar Bulgaria aka auro ta, Baturiya ce. Kuma danginsu sun ki karbarta a matsayin matar dansu, su kai ta uzzura mata shi ne ta gudu ta barni ina da shekara biyu....." A yanzu kam muryata karkarwa take, cikin rishin kuka.

Mami ta zamo daga cikin kujera ta zauna dab da ni, kana ta janyo ni ta rungume a jikinta tana shafar bayana a hankali, cikin rarrashi ta ce "Shi kuma Baban fa?'

"Baffa ya ce da ni tun da aka raba shi da Mamana ya tafi, babu wanda ya kuma jin duriyar shi".

"Kin yarda shi Baffan naki jinin mahaifinki ne?"

"Eh, na yarda Baffa wan mahaifina ne, saboda kaunar da yake min da kuma tarbiyyar da yake bani baya yi wa 'ya'yansa. Kuma ya taba nuna min hoton Babana, ba su da maraba da shi".

Ta ce "Kyawun naki ne Lanto da yanayin fatar jikinki, ya sa nake tababa, amma yanzu na gane jikin Mamanki kika debo. Bayan Baffa da Hajara babu wanda kika sani cikin zuri'arku?"

Na ce "Sai Baffa Lawal kanin Baba, shi Yaya Hajara ke bi a haihuwa. Asalinmu garin Bujawa da ke cikin jihar Katsina, kuma duk dangin mahaifi na a can suke. Sai dai ba su da yawa, kuma ba masu karfi bane don haka kowa ta kansa yake.

Su suka korar min uwar kuma suka kasa rike ni sai Baffa kadai, shi kuma mata ta fi karfin shi".

Ta ce "Ki kwantar da hankalinki Lanto, Am by your side (ina tare da ke). Ki dauke ni Uwa-Mahaifiya, ni kuma na yi alkawarin rike ki har gidan aure.

Kuma da sannu za mu nemo iyayenki a hankali, saboda ina da contact da kasar Bulgaria, ina zuwa kan kasuwanci na.

Haka maigidana ma'aikacin sadarwa ne, ki kwantar da hankalinki. Yaushe ne kika ce min za ki je dubo Baffan, ko kin fasa?"

"A'a, ban fasa ba, bana son in yi missing lesson ne".

"Babu komi, goben ki je ki dawo jibi, karatun ba zai wuce ki da yawa ba".

Washegari Mami ta sa direban yara ya kai ni Bujawa, da tsaraba rankatakaf na kai wa Baffa da iyalin shi cike da boot din mota.

Ganin na zo da fagon kaya, yau Inna Laminde ta yi min kyakkyawar tarba, duk ta gigice, ni kaina na san yadda na canza ne ya gigita ta. Ta sunto kudi a habar zaninta ta sa murya tana kiran danta Salihu.

Ya shigo ya tsaya a jikin kofa hannuwanshi bisa kofar shigowa, duk tsamin da jikinsa yake yi ya cika dakin. Ya ce “Wace nan nake gani kamar Lanto?"

Na yi murmushi na ce "Ni ce Yaya Sale".

Ya ce "hala cikin inji aka sa ki a birnin aka wanke aka maido ki kamar Uwarki?" Ban amsa ba.

Ta gama kiciniyar kwanto kudi, ta ce "Kai, bana son sakarci". Ta qyafta mishi ido tana nuna mishi galleliyar akwatin da na zo da ita "Ungo maza, sayo mata ruwan leda da lemun kwalba".

Ya karba, shima rawar jiki yake. Zai fice na ce "Akwai direban Mami da muke tare yana waje, ka ba shi lemon ni a koshe nake".

Ya ce "Ai biyu zan sayo, wallahi yau sai kin sha lemon tunda kin zama Hajiya, har hakimcewa kike direba ya tuko ki a galleliyar mota".

[1/1, 14:07] Nrs Zainab A S: Ya fita yana fatattakar yaran da suka yanyame mota mai sitiyari a hannun dama.

Kan ka ce meye wannan ya dawo da ruwan swan da lemon kwalba, ya ce "Na bawa direban ga naki, Allah ya sa a ci damu a Hajjin bana tun da kin zama Hajjaju".

Laminde ta ce "Kai kam! Allah ya sauwaqe maka da shegen kwadayi, tashi ka bamu wuri mutumin banza!"

Ya mike zai fice yana cewa "Ya sauwaqe mana tare da ke, Inna".

Baffa bai shigo ba sai bayan sallar isha, kafin nan na bude jaka na ware ma Laminde kasonta na turmin atamfa Ghana guda biyu, da kwalbar turare wadda ko yadda ake fesawa ba ta sani ba balle fa tsadar sa.

Bakinta ya ki rufo, ta ce "Tattara muje gun Malam ayi kasafin a can".

A kwance muka samu Baffa akan katifarsa kamar ba shi ba, idanuwanshi sunyi ja ainun masu nuna alamun ciwon kai mai tsanani. Jikina ya yi sanyi, duk farin cikin da nake ciki yau sai ya kau, hankalina ya tashi matuka. Da kyar ya kokarta ya tashi, ya ce "Lanto ce?'

Na ce "Eh Malam".

"Jikina ne yau bana jin dadin sa Lanto, lafiya lau na yi sallar magariba, amma zuwa isha'i ciwon kai mai tsanani ya cimmani".

"Allah zai yaye Baffa, zan je chemist yanzu na amso ma magani". Yace

"Ai na tura Sale tun dazun na san idan har ba ya tsaya shiriritarsa ba, zuwa yanzu yana hanyar dawowa".

"Mami na gaishe ku dukkanin ku".

"Allah sarki baiwar Allah, Allah dai ya saka mata da mafificin alkhairinsa, amin".

Na fidda mashi bandirin shadda guda biyu, da takalmi, ya yi ta godiya.

Sale ya yi sallama daga can bakin kofa ya cillo min maganin yai tafiyar sa yana kara jaddada min lallai in tabbatar Hajjin bana da shi za'ayi. Ko ina na ga kujerar Makkan oho. Yanzu na tabbatar da rade-radin da ake yi masa na cewa, yana shan kwaya.

Na janyo kwanon shan ruwan Baffa dake gefe, na balli maganin na matsa na ba shi ya haxe su duka ya kora da ruwa tare, na fiddo masu dogayen wanduna na jeans guda biyar, wato adadin 'ya'yan Baffa. Domin dai shi Allah bai nufe shi da haihuwar 'ya mace ba, watakila shi ya sa ya dauki son duniya ya dora a kaina, ko kuma saboda dan'uwanshi ne da baya da kamar sa? Allahu a'alam.

Laminde ta koma kicin don sako mana tuwon dare.

A nan ne muka samu damar kebancewa ni da Baffa, hirar da muka yi da Mami rannan ya sanya min kwadayin bin diddigi akan iyayena, wanda tun da na girma na taso ban taba yi ba.

Ya zauna sosai ya jingina da bango, na yi saurin cusa mishi filo a baya yadda zai ji dadin jingina sosai.

Ko da Laminde ta kawo kwanukan tuwon ta aje mana, daga ni har Baffa babu wanda ya kalla. Ga dukkan alamu shima Baffan cikin damuwa yake.

"Kin ji ni shiru kwana biyu ban zo na duba ki ba ko? Bana jin dadi a kwanakin nan shi ne dalili. Amma na ji dadi da kika yi hankalin zuwa, in ka ji wanda ya damu da kai kwana biyu shiru, sai ka neme shi ka ji ko lafiya?"

"Haka ne, Baffa".

"Tashi jawo min akwatin can ta karfe daga qarqashin gado".

Na yi yadda ya ce, amma jikina ya yi la'asar, sannan faduwar gaba ta same ni duk a lokaci guda.

Ya lalubo mukullaye a kasan katifarsa ya bude, ya soma bincike, har Allah ya taimake shi ya zakulo abubuwan da yake nema. Hotuna ne guda biyu na zamanin da, wato masu farin kala, ya miko min.

"Kin ce min kina daukar karatu a can gidan, ke nan za ki iya karanta wasiqa?"

"Idan da Hausa ne, zan iya".

"To duba ki gani".

Rubutu ne mai kyau da tsari, sai dai kash! Cikin harshen turanci ne.

Na ce "Turanci ne, amma zan bai wa Uncle Dini (Malamin lesson) ya karanta mani, ko shi ko Mami".

Ya ce "Da kyau, mahaifiyarki ce ta bar maki, ta bani amanar idan kin kai munzalin aure in ba ki. Ko me ya faru da ke mu muka jawo miki muka rabaki da iyayenki karfi da yaji. Ba kuma yadda ba ta yi damu ba ta tafi da ke amma mun ki, kuma ita ma ai da laifin ta, ta ki musulunta ya ya za'ayi mu karbe ta a matsayin matar auran dan mu?

Muna tsoron kada ta tafi da ke ta sanya ki a turbar kafirci.

Can ya gano ta a kasar da ya je karatu, ya jajibo, mu kuwa bamu ga me za mu ci da mushirika ba, har gobe har jibi. Ga ta nan ita ce mahaifiyarki, sunanta Grace, mutuniyar kasar Bulgaria ce".

Na samu kaina da rungume hoton wadda aka kira ‘Grace’ a kirjina, hawaye na malala.Baffa ya ce "Daina kuka KAUTHARA.....! Sunan da mahaifinki ya yanka rago ya sanya miki ke nan. Ban san inda yake ba, bamu da labari akan shi, ya tafi ya barmu da kewa.

Wasu kan ce kurciya aka yi mishi, mu kuwa mun san dalili, zuciya ya yi. Kalli mahaifinki sosai bamu da maraba, shi ya ke bina a haihuwa. Sai Lawal, shi kuma Hajara ke bin shi, mu biyar mahaifanmu suka haifa, shi ne da na biyu, Adamu shi ne auta, amma ya rasu tun da kuruciyar sa.

Na yi matukar mamakin rashin zuwan Hajara gare ki a tsayin shekarar nan da ta barki, amma ba komai, abin da ka yi wa dan wani tabbas shi za'ayi wa naka. Ni na ma fi gamsuwa da zaman kida wadannan mutanen masu alheri, fiye da ita.

Allah ne ya kawo mu wani zamani da naka zai ki ka, bare ya rungumeka. Don haka ta je, idan wani ya ki ka da wuni, wani da kwana zai so ka. Muma nan da ne ta kan zo din, yanzu kuma ta jima ba ta leqo ba.

Ko da wasa kar ki yi tunanin wata rana za ki koma gare ta ki zauna, sai ranar data furta miki da bakin ta tayi nadamar abinda tayi miki, domin kema ta shegantaki, ni kadai na karba. Gaba ce sosai tsakaninta da mahaifiyarki, ni kadai na karbe ki don ta ce ba ta ga dalilin da za ta karbi diyar mushirka ba.

Ki nemi ilimi, ki nemi miji ki yi aure ya fiye miki komi.

Ki tsaya da digadiganki Lanto, ki rabu da su wata rana su da kansu za su gane kuskurensu, ki kama kanki ko ba dade ko ba jima wata rana iyayenki za su neme ki".

Na yi ma Baffa godiya tare da neman alfarmar in tafi da hotunan in dinga gani, in nuna wa Mami, don ta ce ita ma da maigidanta idan ya dawo daga kwas din da ya tafi za su taimaka min wajen nemo min su".

Baffa ya ce "Allah yai miki albarka Kauthara".

"Ya yi mana tare da kai Baffa".

Ya murmusa ya ce "Ba ki tambaye ni sunan Baban ba?"

Na yi murmushi cikin jin kunya,

"Ina da wani Baba ne bayan kai, Baffa?"

Ya rausayar da kai, ya ce "Babu Kausara, sunan shi Nasir, likitan zuciya ne kwararre". Karshen tattaunawar da muka yi da Baffa ke nan.

Na koma Kano da sati daya aka aiko aka gaya min rasuwar Baffa, na dade bana cikin hayyacina, sai da Mami ta hada da sawa ake yi min rubutun dangana. Amma har gobe idan na tuno da Baffana sai na zub da wasu hawaye masu tsananin zafi.

***

Mami ke gaya min mijinta an tura shi kwas ne na tsawon shekara guda a Jami'ar California. Kuma a wannan watan ne ake sa ran dawowar shi.

Ba tare da shawara dani ba Mami ta shigar da ni makarantar su Mukhlis (Nigerian Turkish) da ke Tarauni. Wannan ya kara kular da Mukhlis, ya soma sanya min kahon zuka, komi na yi sai ya kushe ya gwale ko a gaban waye. Ya kuma dage lallai sai Mamin ta sauya mishi makaranta ba zai dinga shiga mota da ni ba.

Mami ta nemi dalili. Ya ce

"For now kam, she is not dirty....."

".....To why? Mukhlis din Mami?"

Ya ce, "I just hate her, and I donno why?"

"Komai yana da dalili.....".

"Kyawunta is too much, sai ka ce wata Devil? Ga ta dai daga kauye amma duk ta fi mu kyau, kina saya mata kaya irin na su Huda, 'yarki ce? Ai ga shi nan ta fi naki 'ya'yan kyau".

Ta yi murmushi "Na dai gane Mukhlis kishi kake da Kausar. Sai me dan ta fi su kyau, sai aka ce ba za su sami mijin aure ba? Ko kuwa duk kanninmu mu muka halicci kanmu?”

Ya kyabe baki, ya dage, ya maya ya rantse, ko a fidda ni daga Turkish ko shi ya fita, in ba za a kai shi wata makarantar ba to zai zauna a gida ya dinga daukar lesson. Amma ba zai yi makaranta daya dani ba.

Mami irin masu halin turawan nan ne masu masifar son 'ya'ya, dole ta mai dani ‘Ansar College’ don farin-cikin Mukhlis.

Dokokin Mukhlis ba su tsaya nan ba, sai da ya kara da lallai sai an raba mana motar zuwa makaranta, kuma direban gidan guda daya ne, sai ya zamanto kullum sai an fara sauke su sannan a dawo gida a dauke ni.

Wannan ne ya sa kullum nake zuwa makaranta a makare, har malamai suka gane. Suka tuntube ni kan dalilin da ya sa kullum sai na makara, na gaya musu cewa ina da matsala ne da dan uwargijiya ta. Don haka suka kawo shawarar the best solution Mami ta samu mai taxi su tsadance a wata kullum karfe bakwai da rabi ya zo ya dauke ni, in an tashi ya je ya dauko ni.

Mami ta amince, don ita ma fitinar Mukhlis ta ishe ta, ga shi ba ta son abin da zai bata ranshi ko miskala zarratin.

A wani week end muna hira da Mami, na ce "Kudin aiki da ta ce tana tara min za ta bai wa Yaya Hajara in sunyi yawa. Na ce ta yi wa Allah ta barshi, tun da ta tsaya min akan karatu ta gama yi min gata na duniya baki daya.

***

Kwanaki biyun nan na week end Mami is very busy cleaning, clearing and decorating gida lungu-lungu, saqo-saqo. Sannan ta ce in shirya da yamma zan raka ta saloon.

Duk sanda za muyi irin wannan fitar, kanti ne ko wani wuri, ni ke rike wa Mami jaka tare da kula da Muslim, Houda da Nourr don kar suyi wani wajen. Wankan su, shirin su da walwalarsu duk ya rataya a wuya na.

Mami na zuwa (Zaynab-Saloon) ne a Mukhtar Muhammed Link, ba ta canza wurin Saloon. Waje ne da larabawan Lebanon suka bude a cikin Kano. Su Mami har dasu pedicure & manicure ta fito kamar wata yarinya 'yar shekaru ashirin, sai ka rantse da Allah ba ita ta tsugunna ta haifi su Mukhlis ba.

A kan hanyar mu ta dawowa ne ta ke gaya min gobe Baban su Mukhlis zai dawo.

Don haka ko da muka dawo gidan bamu zauna ba, Mami da Larai suna ta tsarin girke-girken da za a tanadarwa Daddy kamin ya iso. Ni kuma sai nake ganin zuwan Daddyn zai takura ni (ki ji karfin hali), tun da ba zan dinga samun lokacin da nake samu da ita ba, dole hankalinta da lokutanta su koma kan mijinta. Na saba da Mami sosai, ina sonta kamar yadda nake son mahaifiyata, Grace, wadda ban sani ba, ban taba gani ba.

Ko da yake Baffa ya gaya min sai da ta dauke ni a bakin nono ta tafi, lokacin ina da shekaru biyu a duniya.

A washegari kuwa da asubahi Daddyn ya iso, duk muna barci. Haka har na shirya yara suka tafi nima mai taxi na ya zo muka tafi bamu sanya su a ido ba.

Sai yanzu ne na gano hikimar Mami na dauka na wannan hidimar, da abubuwan sai sun yi mata yawa. Ga ta kuma da son barcin safe don samun nutsuwa. Don ta gaya

min ita kam in ta yi sallar asubahi komawa take, in ba haka ba sai kanta ya yi ta ciwo.

Ko da muka dawo, suna bangaren Daddyn, a matse nake da son ganin wane ne mijin da yai katarin sa'ar samun Mami as a house wife? I would like to see him!

Hakan ba ta samu ba, sai da daddare, inda ta aiko Huda in zo in gaida Babansu.

Na dora mayafi akan doguwar rigar da ke jikina na bi bayan Huda.

Zaune yake bisa dan qankanin carpet din da ke tsakiyar falon, ya mike kafafunsa sambal ya dora kafa daya a kan daya, da remote control a hannunshi yana canza channels. Yayin da Mami ke kishingide a kujerar da ya jingina, tana ta zuba mishi hira kamar ta lashe abinta don so. Kallo daya na yi mishi, ban iya na maimaita ba, saboda tsabar kwarjini da cikar zatin da Allah yai masa.

Da kam ina ganin Mami mai kyau, Mami mai tsabta, da babu na biyun ta a duniya. Ashe Mami mummuna ce, qazama ce ‘yar dukununu akan Baban Mukhlis.

Fuska a sake yake amsa gaisuwa ta, ya ce, "Ya ya karatu da 'ya'yan Mami?"

Na murmusa na ce "Alhamdulillah, bani da abin da zani ce muku, sai godiya".

Shima ya murmusa "Na kawo tsaraba har da ke, sabida labarin ki dana ke sha a bakin su Huda, da safe Mamin yara za ta ba ki". Kaina a sunkuye nace

"Na gode". Na mike na koma daki.

Tun dawowar Daddy sai ya zamanto Mami ba ta da lokacin kowa, har da kanta kuwa, sai nashi. Kacokam kula da su Nurr sai ya komo hannuna.

Wani zubin sai ta hada mu da direba a renakun da ba makaranta, ta ce in kai su Roxy ko Kano Zoo. Hakiqa rayuwarsu abin koyi ce wadda babu hatsaniya a cikinta.

Na koyi abubuwa da dama daga gare su, hatta maganganun da yaran ke yi ina koyon ilimi a ciki.

Satin shi daya ya wuce Abuja, inda ya ke aiki da NTA Abuja (Nigerian Television Authority).

Sai ya zamanto ba mu da abin yi da daddare sai sauraron Daddy, yana feso labarai da tsabtataccen turancin sa kamar Obama.

Daddy News-Caster ne cikakke, kuma fitacce.Duk wani da yake sauraron labarun kasa ya san MU’AZZAM KANTI MU’AZZAM. Duk da ba fahimtar abin da yake cewa nake yi sosai ba, na san MU’AZZAM KANTI yana BURGE NI. Da zarar an nuno shi kuwa 'ya'yanshi za su hau tsalle, har Ice-cream suke lasawa screen din dai-dai bakinsa, wai shima ya sha.

Haka da ya baro ofis waya suke yi ta awanni masu tsaho da iyalan sa, ya yi ta biye ma shirmen yaranshi. Ranar juma'a kuwa komin dare sai ya taho.

Duk inda ake neman mace ta gari, kuma managarciya to Hajiya Mami ta zarce, wajen nunawa miji kulawa, kauna da soyayya kam na jinjina mata.

A duk karshen mako throughout bama jin duriyar Mami, sai in ta fito girka mishi delicious dinta, tana can sassanshi sai Monday idan ya tafi kafin ta sami lokacin kowa da komai. Duk abin da za su bukata ni da Baba Larai ke tanadar musu, in ka ganta ta shiga kicin to girkin Daddy za ta yi, wanda bai taka kara ya karya ba. Bayan wannan komi na gidan mu muke tafiyar da shi.

A qokarin Mami na gyara mu'amala ta da danta Mukhlis, wanda yake kusan tsarana, ta ce in dinga gyara mishi daki kullum, in dinga fidda mishi kayan wanki, in daina damuwa da duk abin da yake yi min.

Ba Laptop dinshi ce baya so in taba ba? To in daina tabawa, ba kuma don kyara yake yi min hakan ba, don kada in bata mishi aiyyuka ne, tun da ba iyawa na yi sosai ba. In sha Allahu za ta tafi Dubai cikin satin nan za ta sayo min nawa.

Duk yadda ta ce haka na mai da hankalina wajen kwatantawa. Dama Uncle Dini ne ya ce mu dinga yin amfani da ita tare duk sanda yake yi mana lesson din Computer.

Gidan iyayen Mami yana nan a unguwar Sultan Road, kuma ba sau daya ba, ba sau biyu ba, ta sha aike na kuma mukan je tare. Babu wanda bai sanni a dangin Mami ba da kuma matsayin da nake da shi a wurin ta. Hajiyar su Mami mutuniyar kirki, duk abin da ta san Mami na so ita ma tana so.

A karshen satin Mami ta tafi Dubai ta barmu a gidan kan harkokin business din ta. Shahararren Boutique ne da Mami a Beirut Road, wanda ya qunshi duk wani nau'in sittiru 'yan waje (designers) na maza da mata. Daga jakunkuna, takalma, trollies,

agoguna, kayan yara da kayan wasansu, fashion jewalleries da sauransu duk babu nau'in da babu a ciki.

Wani zubin Mami har a cikin kantin zama take cikin ofis dinta, idan kuma ba ta nan akwai mataimakiyarta Mrs. Ngozi. Gaba daya karatun Mami ta yi shi ne akan harkar kasuwanci (Business Administration) har zuwa (master) daga jami'ar Bayero.

A wani week end Daddy ya zo, ina dakin su Nour ina shirya ta don za muje tarbar Mami Airport, yau ne take dawowa.

Na jiyo Mukhlis ya fito yana ta fada, shi kam wannan Lanton, must go back to her village, in ba haka ba shi zai fice ya bar musu gidan, har da kukan sa.

Baban shi da ke falo cikin tulin ayyukan takardu ya dago kai a hankali ya dube shi, ya yi mintuna uku yana nazarin sa kafin ya tausa murya ya ce "Zo Mukhlis".

A fusace yake sosai, ya matsa gaban Uban,shikuma ya rungumo shi gefen damar sa, ya ce "Ya ya haka? Ina laifin mai taimaka maka?"

Ya ce a fusace "Ni dai a ba ta komai take so ta fita ta bar mana gidanmu, I just hate the girl.....!"

Ya yi murmushi cikin rashin jin dadin kalaman shi ya ce

"To meye laifinta na yau kuma?"

A gadarance ya ce "Tana min misplacing things, in aje abu a wuri kaza ta dauka ta canza mishi matsugunni in yi ta shan wahalar nema".

"To ko ta daina yi ma gyaran dakin?"

"A'a, ina so a gyara min, amma a nemo wata ba wannan ba, wannan kyanta ya yi yawa, har yana tsorata ni".

Ya tintsire da dariya, ya ce "Ke nan ka fi son a nemo ma mummuna?"

Ya ce "ta wani bangaren na fi son hakan".

"To bari aje a dauko Mamin sai a san abin yi, ta zo ta raba wannan rigima tunda ita ta qulla ba ni ba!".

***

[1/1, 14:07] Nrs Zainab A S: Ban taba hawa motar Daddy ba sai yau, sai dai in ganta kawai a harabar adana motoci, in karanta sunanta in sake karantawa. Wani zubin har in kai hannu in dan shafe ta cikin sha'awa, 'Volvo'. To a yau dai gani a cikin ‘Volvo’ din Kanti Muazzzam, sanyin A.C, qamshin car-fresh hade da sassanyan turaren Daddy ‘Gio-Gio Armani’ (Armani-Code)sun hade sun cakude a cikin motar.

Na samu kaina da satar kallon Daddy babu dalili. Hakan nan dai idanuwana ba sa gajiyawa da kallon sa. Sai da na yi tsam da raina na gane shigar da ya yi ce cikin ‘suit’ ke burge ni, take kuma matukar bani sha'awa.

Na rasa shigar da tafi amsar M.K (yadda Mami ke kiransa ke nan watau Mu'azzam Kanti). Ban san mai ya sa nake yawan tunanin al'amarin M.K ba. “He is classique!" Ina yawan fadar hakan a cikin raina.

Tuni jirgin su Mami ya sauka, muna baya ni da yara ina ta ci gaba da satar kallon sa. Mami tana gaba, don Mukhlis bai biyo mu ba, ya ce da ya shiga mota da ni, gara ya zauna a gida.

Har muka fito Airport din Malam Aminu Kano, ban daina kissime-kissimen banza akan mijin Mami ba.

Muna isa gida Mukhlis ya tada bala'i, shi lallai a yau din nan sai Mami ta mai dani inda ta dauko ni.

Mami ta fidda hannu ta zabga mishi wani irin wawan mari da bai taba ji ba, ta ci gaba da kai masa duka ta ko'ina.

"……..Sai ka gaya min abin da yarinyar nan ta tsare ma a gidan nan……."

"Ba ta tsare min komi ba, I just hate her...na fada na kara! Ki ci gaba da duka na, ba zan taba son ta ba!!"

Daddy ya janye danshi da karfi, ya ce "Ba zai yiwu ba, ba za ki nakasta min yaro a kan 'yar da ko asalinta ba ki sani ba.

Ni duk wannan kame-kamen da kika gaya min akan iyayenta ban yarda da shi ba, balle in yi wani taimako wurin nemo su. Wot's your own business?"

Ta ce "Na ji, ba za ka taimaka min wurin nemo iyayenta ba, amma ya bar min 'yata ta zauna lafiya".

Ya kyabe baki ya ce "An barki, amma ba zan dauki duka ba, babu gaira babu dalili".

A hakan dai da dadi ba dadi muka ci gaba da rayuwa cikin gidan nan, ni da Mukhlis. Yana gaba dani da aji daya, don haka ya rigani kammala karatun sakandire.

Daddy ya shirya mishi liyafar taya murna (dinner) shi da abokanshi a gidan cin abinci na (Pink Peacock Restaurant).

Ina zaune, haka kawai, na samu kaina da son yin wani abu na taya murna ga Mukhlis, a wannan rana mai muhimmanci a gare shi da duk masoyanshi suka hallara. Ko da kuwa a ce zai gwale ni ne ko ya dizgani a bainar jama'a.

Ni da Huda da Nur, Mami ankon wata dakakkiyar shadda ta yi mana babbar riga, Senegalese. Kowa ka kalla a wurin kyawu ne ke dukan kyawu, boko ne ke dukan boko.

Mukhlis ma'abocin abokai 'ya'yan manyan ‘yan boko irinsa, har da jajayen fata, hadi da malaman makarantar su baki daya Larabawan Turkiya.

Ko Mami ban gaya wa uzuri na ba, na bi tasi zuwa Country Mall, na sayo katuna masu matukar qayatarwa na fatan alheri, hadi da turaren da ya ke so, Hugo Boss na dawo.

Karfe takwas duk mun gama shiryawa. Takalmin kafata channel dogo ne sosai mai madauri siriri a idon sawu, wanda Daddy ya sayo min a matsayin tsaraba lokacin da ya je kwas California.

Allah bai yo ni ma'abociyar son kwalliya ba, don ni ko powder bana shafawa, iyakacina in yi wanka in yi brush. Tun Mami na mita har ta haqura ta qyale ni, in ka ganni ina shafa mai to ‘vaseline’ ne, shima sai a lokacin sanyi kadai.

Shi Mukhlis tuni ya bi tawagar abokansa sun tafi, don haka daga ni sai 'yan kannena a bayan mota. Mami da Daddy sunyi shiga ta alfarma, farin cotton lace ne a jikinsu iri daya sak, sai dinkin maza da na mata da ya bambanta, farin cikin da ke cikin zuciyoyin su a yau ba zai misaltu ba.

Ni na san Mami da Daddy duk sun fi son Mukhlis cikin 'ya'yan su, saboda hazaqarsa. Ko hakan ne dalilin da yasa ya zamo mai kaushin hali? Allah masani. Don haka idan har ni din wata 'yar halak ce, dole in taya su son abin da suke so, yana so ko baya so, ba don shi nake son shi ba, alfarmar iyayensa ne. Masu tarin alfarma a gareni.

Aka ci gaba da gudanar da walimar yadda suka tsara shi da abokan sa. Abokin shi Isma'il shi ne mai gabatarwa, shi ya karanto tarihin Mukhlis Mu'azzam Kanti, cikin tsaftataccen turanci, bayan shugaban makarantar su ta bude taro da addu'a.

In ban da faduwa ba abin da gabana ke yi, na ci gaba da kara makale jakata da na sako kunshin katunan cikin wrapping. Yanzu idan ya dizgani a wannan bainar jama'ar ya ya zan ji a raina? Kada kuma in bata musu farin ciki tun da ko gani na Mukhlis ba ya so ya yi, tsawon shekaru biyar da muka dauka tare.

Wata murya daga can cikin kaina na ji tana fadin

"Ki dubi niyyarki ta alheri, ki sadar da alherinki".

Don haka na mike cike da qwarin gwiwa, a ya yin da aka soma miqa mishi prizes, a matsayin shi na head boy wanda ya yi wa makarantar kyakkyawan jagoranci na shekara guda, ya fiddo da makin da ya fi na kowa, ya kuma fi kowa tsabta, qokari da iya turanci, makarantar ta ba shi prizes har babu iyaka. Ta kuma dauki nauyin karatunshi a wata jami'ar kasar Turkiya. Aka dauki tafi gabadaya.

Nima sai na ji ya burgeni, ya ya za ai Da irin wannan mai wanke zuciyar iyaye da farin ciki ba zai samo mafificiyar kaunar su ba?

Cike da sunan Allah a bakina na karasa, na qakalo wani tsorataccen murmushi na miqa mishi.

Jikinsa a sanyaye ya karba ya miqa ma wanda ke tarawa, kasa-kasa (to my surprise) kamar bai son kowa ya ji. Ya ce

"Na gode Kausar".

Farin cikin da ya ziyarci zuciyata a yau ba zai misaltu ba. Daga Daddy har Mami bude baki su kai cikin mamaki, Daddy ya samu kanshi yana yi mana tafi raf-raf-raf!.

Da aka zo daukar hotuna har kujerar da nake ya zo shi da mai daukar hoton, ya ce "A yi mana hoto". Sannan muka hadu dukkanmu family din gidan aka dauke mu tare har ba adadi.

Da haka walimar ta watse kowa cike da farin ciki.

Tun da yake dan qwalisar gidan ya gama nashi karatun, sai Mami ta sallami mai tasin da yake kaini muka ci gaba da tafiya a motar yara, kamar yadda suke kiran ta, alhalin ni ban ga dalilin da zai sa a kira 'spyker' motar yara ba.

Shekara kwana, muna cikin daliban da Ansar za ta yaye shekara mai zuwa, zuwa wannan lokacin duk wata boyayyar surata ta bayyana. Ni Kausar-Lanto, doguwa ce sambal, babu kiba, babu cikar jiki. Ni kaina na san muhimmin abin da yake kara mini kyau shi ne shatar bakina, wanda yake kamar yankar reza, idanuwana ba manya ba, ba kanana ba, hanci miqaqqe straight har baka, kai ka ce dosana mini a

ka yi. Sannan gashin kaina baida yawa cancan, sai santsin tsiya, kuma ban taba sanya mishi relaxer ba.

A kullum na dauko hoton Mamana sai in ga ba maraba, kamar ta yi kaki ne ta tofar, ta fannin kirar jiki kam sai hamdala.

Mun zana WAEC cikin kwanciyar hankali, muna shirin tarbar NECO tafiya ta sake kama Mami Dubai again. Ta tafi litinin da niyyar zuwa friday ta dawo, to kuma sai ta yo min waya ta landline din gida, take ce dani in ci gaba da kula da yara wasu abubuwa sun rike ta sai wata juma'ar.

Na ce "Daddy fa? Ya iso tun karfe biyar na yamma". Ta ce "Babu damuwa, zan kira shi yanzun in mishi bayani".

Ban san mai yasa na fiya jin nauyin Daddy ba, ko don bai sakar min fuska ne, oho? Ban ji dadin yadda Mami za ta barni a gidan daga mu sai shi ba, don shi ko cokali da kofin shayi matarshi ke dauko mishi, ko hanyar kicin baya bi. Na ja numfashi cikin rashin sanin abin yi.

Bayan magariba suna zaune da yaranshi a falo, yana koyar da su home-work, na zo na wuce hannayena rike da kayan wankin yara da aka wanke aka goge, ban yi musu magana ba na wuce, ina ganin sanda Daddy ya dago ya kalleni na sami kaina da samun tangarda a yayin tafiya.

Na yi dakin su Nurr na adana kayan a muhallinsu, sai da na fito ne na russuna ina gaishe shi. Na rasa me ya sa bana son hada ido da Mu'azzam Kanti, kwarjinin shi har ya so ya yi yawa, ilhamar shi da cikar zati suna razana ni. Shi kadai duk ya bi ya cika falon.Duk da tsawo da sirantar da nake taqama M.K ya fi ni, ban taba ganin namijin da sirinta ta yi mai kyau irin M.K ba.

A hankali ya amsa gaisuwa ta, ya kuma kara da cewa

 "Ko zan samu rowan zafi in sha coffee Kauthara?"

Na yi hanzarin dago idanuna na dube shi, ban taba jin wanda ya iya furta kalmar 'Kauthara' irin M.K ba. Ko da ya ke shi haka yake, komai na shi ya fi na kowa. Abin nufi,komi nashi extraordinary ne, wato,duk abin da zai yi, ya yi ko ya ke da shi, sai ka ga ya zarta na kowa da ka sani, musamman wadannan kyawawan 'ya'ya da Allah ya ba shi.

"Akwai rowan zafi, sai kuma me?"

Ya yi murmushi, ya ce "Sai a duba a cikin firji idan Mami ta rage gasashshen namanta a dumama mini".

"Mami ba ta rage ba, sai dai a gasa wani".

"Za ki iya?"

"Zan iya Daddy, kai din ne dai nake tunanin za ka iya cin jagwalgwalon nawa ko a'a?"

Ya yi murmushi sosai, ya ce

"A kawo min kowanne irin jagwalgwalo ne".

Kafin ka ce meye wanna na fiddo naman saniya a firinji, Allah ya so ni bai yi qankara ba, don yanzu direba ya kawo Baba Larai ta sanya a firjin, na wanke na gyare na ci gaba da yi kamar yadda na ga Mami na yi.

Duk irin hade-haden da take yi ban kara komai ba, ban kuma rage komi ba. Kafin in sa a ‘oven’ ruwan zafin da na jona har ya tafasa. Na sanya naman a ‘oven’ na wanke hannuwana da sabulun wanke hannu da ke makale a kichin din kusa da sink na tsane da duster.

Na juye ruwan a karamin flask, na aza kofi da cokali, suger da coffen nasa a karamin ‘tray’ na kai mishi.

"Naman da saura Daddy, amma ba zai wuce 20 minutes ba".

Ya dube ni sosai kamar mai nazarin wani abu a karshe yace "Cikin 20 minutes din Kauthar, ba za ki daure ki taya ni hira ba?"

Ya juya ga 'ya'yan shi,

"To Muslim, kalas, a tafi a yi game a daki karatun ya isa".

Nan suka tsallake littattafansu suka yi dakin wasan su, mai cike da duk wani nau'in kayan wasan yara masu sanya nishadi.

Gaba daya duk na bi na takura, na rasa inda zan sa kaina, ji nake kamar ya zauna a tsakiyar kaina saboda nauyin da jikina yai min.

Wani bangaren na zuciyata na gayamin hakan ba daidai bane, musamman da ya tashi su Muslim, ba kyautawa bane ga Mami.

Ya taso daga mazauninsa ya zauna gabana muka yi facing juna, wannan maganadisun da ya dade yana dawsiniya dani akan Muazzam Kanti ya soma yi min yawo a gangar jiki da ruhi. A take na ji duk jikina ya mace, bani da sauran kuzari sai yadda M.K ya juya ni.

"Zauna sosai".

Dabas, na bi kilishi na zauna, kamar wadda ta yiwa sarki karya!

A tun ranar da na fara ganin M.K nake jin wannan al'amarin na yawo cikin zuciyata da ban san ko mene ne ba. Ni dai na san ina jin nauyin shi, ina kuma matukar ganin girman shi. Amma al’amarin yafi karfin bayyanuwa da harshen dan adam.

Amma a yau al'amarin har ya zarce na baya, da zai min babban adalci shi ne kawai ya barni in tafi, amma na ga shi da gaske hirar yake so mu yi.

Dai-dai lokacin da Mami ta kira shi a waya, ban san me suke cewa ba. Ko da yake ita din ce ban san me take cewa ba. Ya dai yi murmushi nasu na ma'abota soyayya, ya ce

"No matsala take your time lady and let me have mine". Me ta ce, oho?

"Yau na samu kaina da son hira da 'yarki, I really want to help...".

Me ta sake cewa, oho? Ya ce "Farin cikinki shi ne nawa".

Zuwa wannan lokacin na samu na dai-daita nutsuwata, ya sakar min wani lallausar murmushi ya ce

"Kausar feel free with me? Am I not your Dad?

Na lura da ke kina cikin damuwa, ina so in san abin da ke damunki. In dai Mukhlis ne sati mai zuwa zai wuce Turkiya".

Da sauri na dago na dube shi. Ya daga min gira cikin ba da qwarin gwiwa. Da sauri na girgiza kai,

"Bani da matsala da Mukhlis yanzu, ya sauko muna gaisawa cikin dadin rai".

"Don ya ga zai tafi ya bar miki gidan ne shi ya sa ya sauko. Ina so in sani, mene ne sirrin?'

"Sirrin me?"

"Sirrin rashin jituwar taku, komi sai da dalili".

Nima na murmusa

"A nawa dan tunanin, kaunar da Mami ke nuna min ne yake ma kishi, kuma banga laifinsa ba. Abin da kake so shi kake ma kishi, yana son Mamarsa, ita kuma tana nuna ta fi so na.

Sai abu na biyu, nake jin kasancewar na fito daga kauye, shi kuma gaye ne, ko ba haka ba?"

Dariya na ba shi sosai, ya ce "To ina labarin iyayenki? Shekarun can baya Mami ke gaya min abubuwa haka-haka, to ban ba ta hankalina ba, don haka ban fahimci al'amarin ba".

Na kwashe duk yadda Baffa ya gaya min na gaya mishi, babu dadi babu ragi. Saurarona yake da dukkan zuciya da attention .

Ya ce

"Yanzu ina hotunan da wasiqar?"

"Suna nan a ajiye a cikin kayana. Abin da ke damuna ke nan, ina matukar son ganin su.

Ban tashi da soyayyar Uwa ba, a galabaice na tashi. Sai yanzu ne da na samu Mami nake jin na samu Uwa".

"Dauko min hotunan da wasiqar zan gani".

Na nufi daki na yi ta bincika kasan kayana, har Allah ya bani sa'ar gano su cikin baqar ledar da na sa na daure, na kawo mishi.

Kafin ya gama nazari na koma kichin na duba naman, na tabbatar ya gasu. Na kashe oven na juye a plate, na sa wuqa duk da zafinsa na yayyanka. Har na kawo gefen shi na ajiye bai gama nazarin wasiqar ba.

Na samu waje gefe guda na zauna, ya kare ya ajiye a gefe ya ce "Ta ce ne idan da rabo watarana za ku ga juna, dangin mahaifinki sun ki karbarta a matsayin mata, sun raba ta da Babanki karfi da yaji, bayan kuma kafin ta aure shi danginta sun sallamata.

Don haka yau da zaman ya zo karshe, ba ta da fuskar da za ta dubi ‘yan uwanta, don haka kar ki yi tsammanin ta koma Bulgaria kice zaki bita. A'a', ta tafi neman mijinta (Babanki) wanda shima ya ce duk ranar da ta bar kasar nan shima ranar zai bari, tana da yakinin cewa, 'yan'uwan Babanki asiri su kai suka raba su, suka kuma raba shi da kasar haihuwarshi bayan izayar da suke gana mata.

Don haka Kausar ki kwantar da hankalinki kin ji? Ko ba jima ko ba dade watarana iyayenki za su neme ki da kansu, tunda suna sane da ke. Duk da haka zanyi amfani da hoton ga gwamnatin Bulgaria, ko za a dace".

Cike da jin dadi na ce "Na gode Daddy, Allah ya saka da alkhairi".

Washegarin asabar na tashi da masassara da matsanancin zazzabi, don haka na kasa fitowa har misalin karfe sha daya. Inda Allah ya taimake ni yau ba makaranta ana hutun karshen mako.

Har suka yi kalacinsu suka gama Daddy bai ji motsina ba, ina jin shi yana tambayar Baba Larai da ke ta aiki ita kadai a kichin.

"Mutuniyar Mukhlis ina ta shiga ne?'

Ta ce "Nima kam, ban ji duriyarta ba, bari in duba dakin in gani".

Ta daga labule tana kallona ta ce "Lafiya ko? Wannan wane irin barci ne har sha dayan rana?"

Da kyar na amsa mata da cewa "Masassara da zazzabi ne ke damu na".

Ta karaso dakin sosai ta ce "Ayya! Sai ki qunshe a cikin bargo ki ki fada a kai ki asibiti?" Ta dafa kaina da wuyana, zafi rau, ta fita tana gayawa Daddy.

A tare suka shigo, ya tsugunna dai-dai kaina ya dora hannunshi a goshina, wani irin shock ya ratsa tun daga qwaqwalwata har yatsar kafata.Na rantse da Allah son M.K nake, duk da ban san mene ne son ba. Ji nake kamar in tashi in rungume shi ko na samu sa'ida.

Na runtse idona da karfi, hucin numfashina na fita da sauri da sauri.

Ya yi saurin janye hannunsa, ya ce

"Mike, kokarta, hospital za mu. Baba Larai!"

Ya qwala mata kira.

Ta iso da sauri ta tsuguna a gefe, ya ce "Kamata ki shigar da ita mota, ki kula da yara asibiti za mu". Ta ce "To". Shi kuma ya juya ya fita.

Baba Larai ta samo min mayafi na yafa, ta shige kafadata ta rungumo quguna, a haka muka fito harabar gidan. Tuni har ya yi ribas mu yake jira, ta bude min murfin kofar gaba na zauna, ga direba a zaune a bencin maigadi, amma bai ce direban ya kaini ba.

A gani na ban kai wannan matsayin ba. Haba? A kujerar Mami? Anya zaman nan da na yi a gaban motar nan na yiwa Mami amana? Sai dai zafin zazzabin da nake ciki ya hana ni yin tunanin na yi dai-dai, ko ban yi dai-dai ba.

[1/1, 14:07] Nrs Zainab A S: Asibitin Premier da ke Gyadi-Gyadi muka dosa, bai fito daga motar ba ya fiddo wayarshi cikin aljihu ya kira. Wa ya kira oho? Na hango Nurses biyu na fitowa, suka zo suka kama ni zuwa ciki.

Mun yi sa'a babu layi, daga wanda yake ciki sai wata mace guda daya a kujerar jira. Nan na zauna a kan daya daga cikin kujerun, har layi ya zo kanmu. A lokacin shi Daddy ya fita harabar asibitin yana ta kiraye-kirayen wayarsa.

Sai da layi ya zo kanmu ne ya shigo, tare muka shiga ofishin likitan, suka cafke hannu cikin sanayya, suka yi 'yan hirarraki kafin Dr. ya maido hankalinshi gare ni, da tambayar abin da ke damuna.

Na ce "Masassara ce fal bakina, ba zan iya hadiyar komi ba".

"Sai kuma me?'

"Sai zazzabi mai zafi".

Ya taso daga tebir dinsa ya zo gabana, yana 'yan aune-aunen sa. Jikina ya bani M.K ya qura min ido, yana ci gaba da uzzirawa rayuwata da idanun nan nasa.

A duk sanda nake tare da shi, ko na gitta ta gabanshi, na ganshi, ina samun kaina cikin wani irin nishadi.

Na dago ido a hankali na dube shi, shima kallona yake ba sassautawa. Wani al’amari mai girma ya samu muhalli a zukatan mu.

Na yi hanzarin sunkuyar da kaina cikin dimaucewa da abin da na tabbatar yana shirin faruwa dani, koma in ce ya faru da ni, son mijin MAMI!

Ya ilahi, ya Ubangiji ina neman tsarinka da kariyar ka daga Shaitan mal'uni. Ya Ubangiji ina rokon kariya daga butulci da cin amana. Ya Ubangiji ka dau raina kafin abin da zuciyata, qwaqwalwata da gangar jikina ke son assasa min in yarda da shi a bisa tilas ya zan tabbatacce. Na tsani kaina a karo na farko, amma shi Mu'azzamun nayi-nayi in yakice shi na kasa.

Allurai ne da magunguna likitan wanda na fahimci abokin M.K ne ya rubuta mini. Haka kafin in bar asibitin sai da suka tsikara min allura kwaya daya, duk da tsoron allurata yau har aka yi, aka gama ban san an yi ba. Domin hankalina, ya tafi can ga so da kaunar angon Mami.

Doctor ya ce, za a ci gaba da kawo ni allura har zuwa rana i ta yau. Har muka hawo bisa kwalta, ba mu ce da juna uffan ba. Maimakon shirun, sai Daddy ya kunna sautin kira'ar Ahmad Sulayman cikin motar, (Suratul Rahman). Dadin kira'ar ya soma nutsar min da zuciya.

Kacokan ya dauki jinyar ya aza a kansa, shi ne ke zuwa bani magani akan kari, yana kara kusanta ta, yana kara dagargaza min zuciya. Na nemi da ya koma aikinsa,ya ce ba inda za shi sai na kare daukan allura da magunguna na, ya ba da 'excuse' a office. Dole haka na zubawa sarautar Allah ido.

Mami ta yo waya a washegari yake gaya mata jikin 'yar lelenta ya ki dadi. Mami dadi ya kashe ta, ta lura yanzu dai Daddy ya sauko, yana taya ta son abin da take so.

Ta ce "In sha Allah friday ina nan tafe, kayan da na auno ne nake jira a fara yo min gaba da su. Miss you too much……, a bani Lanto".

A handsfree ya sa wayar, bai damu da ina jin su ko bana jin su ba.

"Me kike so in sayo miki Lanto?'

Hawaye suka zubo min sharrr! Na yi hanzarin juyawa wai kada M.K ya gansu, idanunshi fes a kaina, kamar mai nazarin wani abu. Don haka na kasa baiwa Mami amsa. Kamar ya san halin da nake ciki.

Ya amshe wayar ya ce "Ke ma kin san me take so ai, Pakistani da Abayat, ko ba sune tsarabar da kullum take cewa a kawo mata tsarabar su ba?”

Ta ce "Ni dai a bani my daughter ina son jin muryarta, ko masassarar ta hana ta magana?'

Na amsa cikin dauriya da fin karfin zuciya, na ce "Mami yadda Daddy ya ce, haka ne".

"To shi ke nan, agaida Baba Larai, a shafa min kan autata (Nurr)".

***

Sai dakina ya zamto nan ne wajen hirar M.K ni da shi da Baba Larai, idan yara sun tafi makaranta. Mukhlis ya jima da fara karatun ‘Law’ a Turkiya, ko waya ma ba sosai yake yowa ba, duk kuma sanda ya yo, sai ya tambaye ni, na lura Mami na jin dadin hakan qwarai da gaske.

Hankalin Daddy bai kwanta ba sai da ya ga jikina ya soma murmurewa. Akwai wanda ya kai Daddy iya jinya? Ban taba gani ba. Na yi ma kaina fada da kakkausar murya akan in daina bari tunanin M.K na min tasiri. Shima kuma bai taba nuna min wasu alamu na wai shima yana cikin soyayyar ba, sai kulawa (care and concern) kadai.

Ranar juma'a tun safe muke shirin tarbar Mami, wadda za su sauka karfe hudu na yamma. Na gyara su Nurr sosai, kowa ya gansu sai ya yi sha'awa. Ba su da kiba sam haka suke siri-siri uwa Babansu, don kam Mami ba siririya ba ce, kuma ba mai kiba ba.

Karfe uku da rabi muka tafi Airpot din Malam Aminu Kano, ina sanye da atamfa super koriya mai ratsin baki da shudi. Na kawo after dress mara nauyi na dora a kai baqa. Takalmin kafata mai tsayi ne sosai, don ni bana sanya flat shoes sai a cikin gida, kuma haka Mami da ke sayo min su cokal-cokal, ita Mami flat take sanyawa.

A gaban kowa suka rungumi juna, wani maqoqo ya zo ya tokare ni a maqogwaro. Ni Kauthar na shiga uku, na yi asara, in rasa da wadda zan yi kishi a duniya sai da MAMI? Anya MAMINta cancanci hakan?

So nake in yi wa kaina dukan tsiya, ina ruwana don Mami ta rungumi mijin ta. Wata zuciyar ta kara kular dani da cewa"shima ya rungume matarsa, sai ki mutu. A'a, ba zan mutu ba, kwakwalwata ce ba dai-dai ba, ina bukatar ganin Psychiatric Doctor, watakila am in a Serious mental disorder!"

Mami ta iso kaina ta rungume ni, ta ce "Kin rame sosai my dear Kausar".

"Kewarki ce Mami".

Na samu kaina da kantara karya ga mami karo na farko a rayuwa ta. Tun da a zahiri kam zazzabin son mijinta ne ya kayar dani. Shin jama’a a nan duniya akwai butulu irina???

Muna dawowa kowa ya nufi dakinshi don gabatar da sallar la'asar. Da suka fito ne suka hau tebir, ni dama bana cin abincin tare da su.

Ina iya qokarina wajen kaskantar da kaina a gare su, wanda na lura su kuma basa son hakan. To amma yadda suke so in zaman wato, 'YA' da sauka haifa a cikinsu ba zai taba yiwuwa ba.

Ba wai ban yarda da matsayin da suka bani a zuciyoyinsu ba ne, a'a, yaro tsaya matsayinka, kada zancen 'yan duniya ya rude ka.

Na nufi kicin ke nan don in ci nawa abincin a dakin mu, Daddy Kanti ya sa murya ya ce,

"Kausar!"

Mummunar faduwa gabana ya yi, kafin na amsa. Na fito zuciyata cike da addu'ar Allah ya sa ba cewa zai yi in shiga cikinsu da 'ya'yansu in ci abinci ba. Addu'ata ba ta ci ba.

"Come and join us..., daga yau duk sanda nake gari ki tabbatar dake a kan tebir, in ba haka ba nima ba zan ci abincin ba.....".

Daga ni har Mami muka dago ido a sukwane muka dube shi, ko a jikinsa, ya mai da hankali ga cin itacen Apple ba tare da ya bude kowanne dish ba, kai sai ka rantse ba shi ne ya furta abin da ya furta din ba.

Ban karaso ba ban koma ba, haka Mami ba ta ce komi ba, sai ta share kawai ta ce,

"Kin tsaya sororo, ko ba ji abin da Daddy ya ce da ke bane?'

Na daga matacciyar kafata na isa gare su, na ja kujera kusa da Muslim na zauna. Mami ta mike tana serving kowa, babu komi a fuskarta na alamun rashin jin dadi.

Na nemi taimakon Allah na zauna na fara cin abincin duk da raina ba so ya ke ba, tusawa kawai nake yi.

Yadda kika san dusa haka nake hadidiyar abincin da nake cin, duk da irin haduwarsa da dadinsa kuwa, kai ba ka ce ni da Baba Larai muka girka ba. Don duk wasu nau'in girke-girke na zamani mun koya a wajen Mami idan tana yi wa Daddy. Ba ta kuma iyakance mana ga abin da za mu girka ba, tun da har ‘ya’yanta wani zubin a tukunyarmu suke ci.

Bamu kara jin duriyar Daddy ba yau tun da darling ta dawo, duk yadda na yi don in yi barci a wannan daren na kasa. Na kwana cikin rokon Allah ya rabani da wannan mummunan al'amari da yake faruwa da ni, kada Allah ya bawa Mami ikon gane na fada a matsiyaciyar soyayyar mijinta. Yaa Allah! Da wanne ido zan dube ta?

Sai ya zamanto na fara janye jikina daga yadda Daddy ke son ganina a gidan, musamman ta fuskar cin abinci tare da su.

A duk lokacin da na ga za'ayi zaman cin abincin zan shige toilet in yi zamana ko ba abin da zan yi. Ko sun gane ba su gane ba bai dai kara takura ni da zancen zaman cin abinci ba.

Baiwar Allah Mami, ta shigo dakinmu niki-niki da kayan tsaraba, ta samu gefen karamin gadona ta zauna, wanda ke fuskantar na Baba Larai. Ta jima tana nazarina a hankali kamar ranar ta soma ganina, duk na bi na tsargu, dama an ce mara gaskiya.....

"M.K ne ya ce in canza miki daki, ya kamata a raba muku daki ke da Baba Larai, ya kika gani? Kina so ko ba kya so?"

Hankalina ya kara tashi, na yi tsumu-tsumu dani kafin na yi karfin halin cewa,

"Duk yadda kuka zartar a kaina dai-dai ne".

Ta cem "To babu laifi, zan sa a gyara miki dakin can da nake zuba kaya na kusa da dakin su Nur, ko za ki dinga kwana tare da su, yaya?"

Na ce, "Na fi son kwana tare da su din".

Ta ce, "Babu laifi, yanzu dai ki je ki fidda masu kayan wanki anjima mai wankin zai zo dauka".

Na yi mata godiyar tsaraba fal, ta ce, "Babu komi, ni ke da godiya Kausar, yadda kika tsaya kike kula min da 'ya'ya da zuciya daya nima hakan zan tsaya miki cikin kowanne hali".

Daddy bai bar Kano ba sai da ya tabbatar na koma dakin su Nur da kwana.

A satin nan ne muka fara zana NECO, don haka na dauki hankalina baki daya na miqa ga karatuna. Na kuma kirkiro ma kaina hanyar da zan dinga kauce ma haduwa da M.K a duk week end dinsa, ta hanyar komawa bayan gida da karatu inda suke yin kiwon fararen agwagin ruwa cikin swimming karami da aka tanada musamman don agwagin.

Don haka na ci gaba da zana jarrabawata cikin kwanciyar hankali, shima M.K bai kara nema na ba, ko ya neme ni bai ganni bane yana kuma kunyar tambaya oho?

Sai dai ni kaina ina yaudarar kaina ne da gangan, na san ganin shi ya fi min rashin ganinsa salama. Ni kadai na san yadda nake azabtuwa a zuci da gangar jiki da soyayyar mijin Mami.

****

Mu'azzam Kanti Mu'azzam ne zaune a makeken ofishinsa cikin ma'aikatar N.T.A Abuja, tulin aiki fal a gabansa ya kasa cimma komi.

Tunanin 'YAR MAMI? Yes! Tunanin 'YAR MAMI!! Tunanin ‘yar Mami ne ya addabe shi.

Kada ayi aikin rashin kyautawa, kada ayi aikin rashin dacewa, kada ayi aikin dana sani.

Zuciyarsa ta ankarar da shi, amma duk da haka wata kalmar nata yawo a zuciya da kirjinsa.... AURE? Eh, yana son auren 'yar Mami ko a gobe ne, idan har Fatima-Binta za ta ba shi hadin kai.

Mazaaa! Sai a barsu. Suka ce "A'ah, kar a barmu. Ba mu bane muke sanyawa kanmu soyayyar da ba ta dace din ba Takori. Sannan idan ku mata kun dauki auren wanda ka ji ranka, zuciya da gangar jikinka na matukar so, ba tare da la'akari da kusancinka da shi, ko da matarka ba, a matsayin CIN AMANA, to mu ba mu dauka a hakan ba.

Ya fiye mana da mu neme su da ZINA. Babu wanda ya isa ya sanya ma kanshi soyayya, Allah ne yake sawa! Shi ya ke dasa mana ita har ta yi rassa!! Tayi yabanya ta murqushe zukatanmu mu daina ganin dacewa ko rashin dacewa.

Ya muskuta kadan, ya yi juyi cikin lallausar kujerarsa. Shi ne zai karanta labaran wannan makon baki daya, amma ya gaza tattara bayanai. Yana tsoron kada rashin nutsuwarsa ya shafi aikinsa, da yadda shugabansu yake muhimmanta labarun wannan satin. Yana neman wanda zai fasawa cikinsa ko ya huta, a kalla ko bai samu goyon baya ba, ya rage nauyin dake gallabar zuciyarshi.

Ya tabbata bai taba fadawa a irin wannan soyayyar mai takura zuciya ba, a kafatanin rayuwarsa.

Ya rasa ta inda zai bullowa Mami ta yarda da shi, ta amince da hujjojin sa. Yana da hujjojin da zai iya auren 'yarta a shari'a da addini. Sai dai bai san yadda al'ummar al'ada za ta dauki abin ba.

Babu ta inda Fatima-Binta ta rage shi, amma yana son kari, karin kuma ba da kowa bane, da 'yarta.

Inama Fatima za ta yi mishi wannan alfarmar, ba tare da ta qullace shi ba? Ba tareda ta dube shi da wata fuska daban ba bayan wadda take duban sa da ita ta miji masoyi mai amana? She mean a lot him.....!

Bayan kasancewarta uwar 'ya'yan da baya da ya su a duniya,ita din nagartacciyar matar aure ce.Mai kirki mai addini, abun alfahari ga mijinta, abun koyi ga mata 'yan'uwanta, kuma mai son shi tsakani da Allah.....

A duk sanda yai wannan tunanin ne gwiwarshi take sanyi. Anya Mamin ta cancaci wannan SAKAYYAR?

Ya kifa kai jikin teburinshi, yana mai da numfashi a hankali, he must be a betrayer! A Real betrayance!!Sai dai kuma yana ji a jikinsa baxai iya haqura da Kausar ba no matter what!.

[1/1, 14:07] Nrs Zainab A S: Ya riga ya yi nisan da har baya jin kira. Bai damu da duk abin da za a kira shi da shi ba, ya shirya, ya dauka, ya runguma da duk wata fuska da al'umma ko ita Mamin za su kalle shi, ko su alakanta shi da ita.

Ba zai zauna ya kashe kansa a banza ba, ko ya kamu da ciwon zuciya a karon banza da wofi saboda tsoron bacin ran Binta ita kadai ranta. Bai kuma ce baya son ta ba, ko ta gaza gare shi ta wani bangare, soyayya ce matsananciya daga indallahi ba daga yin kansa ba.

Da ya koma gida ya kira Mami, ya ce ta saya ma Kausar waya. Mami Ta ce,

"Dalili?

Wa take da shi da za ta kira?"

"Ba ta da kawaye?"

"NAMIJI MUNAFIKI……!"

FATIMA-BINTA ta furta a zuciyarta, tare da kai hannunta ta yarfe wasu matsiyatan hawaye da suka tsattsafo cikin kwayar idanunta.

A wannan dare Mami ba ta yi bacci ba, hankalinta a tashe matuka. Me take shirin fahimta ne? Me M.K ke nufi? Wannan sabuwar kulawa da yake yiwa Lanto, ta magani da mece ce? Me ke shirin faruwa a idanunta ne? Ba ta da amsa.

Ni dai sai na ga Mami da sabon kwalin waya, ta iske ni a daki ina taya Muslim home-work, ta samu gefen gadon su Huda ta zauna tana wasu 'yan nazarce-nazarcen da ita kanta ba ta san na mene ne ba.

Na dago a hankali ina gaishe ta, ta amsa fuska a sake, ta ce,

"Ga waya Lanto?"

Na ce "Me zan yi da ita Mami? Kawaye gare ni? Kuma tunda muka kare paperkowacce ta kama gabanta, kuma ko adireshinsu ban karba ba balle kuma nambar waya. ‘Am anti-social".

Ta dage sai na karba a hakan, ba ta kuma ce dani M.K ne ya ce ta saya min ba.

***

Aiki ya kacame ma Mu'azzam Kanti, ayyukan da yake tarawa, bai yi ba. Don haka a ranar alhamis ya mai da hankali ya hattama su. Gida yake son tafiya, babu abin da yake matukar son ji irin sautin Lanto. Ya kuma rasa yadda zai yi ya tambayi Mami nambar wayar.

Ya aje biro a hankali ya kama kanshi da hannunshi na dama, deep in thought! Ya ya zai yi ne? Soyayya da 'yar da Mami ta riqa a matsayin 'yar cikin ta???

Ta daina baima Kausar aikin komi, cewa take "Kin fi karfin wanke-wanke da shara a gare ni. Babbar Yaya ce ga 'ya'yana, mai taimaka min wajen hidimarsu,tarbiyyar su, da kula da su da jin dadin su".

Su yi girki tare, su yi shawara tare, su tattauna akan matsalolin kowannensu.

"Ya Allah ka agaje ni, ka fidda ni da Lanto, daga butulci da karya zuciyar Fatima-Binta. Ba ta cancanci wannan ba…….!!!”

A fili Mu’azzam Kanti yake fadin haka.

Don haka ya yi juriya cikin fin karfin zuciya, a kokarinsa na yakice Kausar daga tunaninsa da zuciyar sa. Zai karya zaman lafiya da kwanciyar hankalin da yake samu a gidansa ne kawai muddin Fatima-Binta ta fahimci halin da yake ciki.

He don't want to break his home. Yana da yakinin itama Kausar-Lanto, ta fada a kwatankwacin halin da yake ciki a yanzu. Dole ya yi wa tufkar hanci, don taimakawa rayuwar Mami, amma ba don yana jin zuciyar, ruhin da gangar jikin sun haqura da Kausar ba.

Ya mika tunanin shi ga al'amuran Ubangiji masu ban mamaki, Ubangiji duk yadda ya so haka yake yin al’amarinsa, babu wanda ya isa ya hana shi. In haka ne ke nan ba shi da laifi, ba yin kansa bane halin da ya tsinci kansa; Ubangiji ne ya assasa masa, bai kuma san yaya zai yi da qaddarar sa ba.

Haka ya dawo gidan a wannan satin sukuku da shi!. Duk irin shirin da Mami ta yi domin tarbarsa, kalailaye jiki, gida, toilet, ingantacciyar cima wadda ko a hotel albarka, tura yara da Lanto lesson don kar su dame shi, ingantacciyar tausa, mai warware jijiyoyin jiki da gusar da gajiya, ba ta burge shi ba, bata tafiyar da damuwar da yake ciki ba.

"In faranta min kike son yi Fatima- Binta, ki barni na auri abin da raina ke so……. don samun tabbatacciyar nutsuwata…….".

Haka yace can a qarqashin ransa

Shi da Mamin ne zaune a falo, shi a kishingide cikin kujera, ita a zaune dai-dai santala-santalan kafafunshi.

Huda, Muslim da Nurr suna a gaba, kamin in maro musu baya. Duka suka diba...

"Welcome Daddy.....".

Suka ruga aguje suka dabaibaye shi.

Hankalinshi na kaina, a sadda na tsuguna nake yi mishi barka da zuwa, qokarin kau da kai yake, kar mu hada ido, balle kuma ni da nake jin inama kasar ta tsage in shige, don tserar da kaina daga kaifafan idanun Mami, wadanda ba ni kadai suka razana ba har ma da shi kanshi.

Bani da zabi banda na kwashi matacciyar gwiwata da jiqaqqiyar kafata in doshi daki. Soyayya ba ta taba boyuwa no matter what a kwayar idanu ne?? A gangar jiki ne??? A baki ne ko a hanci wajen shaqar numfashi?? A reaction ne ko a emotion? Haqiqa Mun tabbata qasurguman maciya amanar Mami.

Bai fasa ba, ai namiji ne, kunyarsa ragagga ce, and he is selfish by nature.

Suna bisa tebir domin cin abincin dare, ya dubi Muslim,

"Kirawo Aunty Kausar ta zo ita ma a ci abincin da ita".

"Daddy na kiranki Aunty Kausar".

Wata irin matsananciyar faduwar gaba ce ta same ni mai keta zuciya. A sanyaye na tambayi kaina, mai ya sa Daddyn ya damu dani yanzun? Kada dai in ce abin da ke damuna shi ne ke damunsa? Idan haka ne mun kyautawa Fatima Binta? Dole nima in yiwa tufkar hanci, ta hanyar cewa,

"Ka ce sai anjima zan ci, bani tare da yunwa".

Muslim ya sake dawowa

"Mami ta ce ki zo".

Kamar in ce wayyo Allah! Ko kallabi ban daura ba saboda gigicewa, na bi bayan Muslim, kai da ganina ka san babu nutsuwa ko kankanuwa a tare dani.

Ban san sanda na zube a gabanta ba, a hankali na ce,

"Ga ni Mami".

Komi ma ta fanjama-fanjam, in ji ‘yan Magana. Bani da ilimi, bani da sani, bani da tsimi, bani da dabara sai abin da Allah ya hukunta a gare ni.

Iyakaci Mami ta kore ni, in ta fahimci ina son mijinta, karshen ta kenan. Ta riga ta bani tsanin rayuwa, tushen ilimi, zan iya karbar rayuwar a duk yadda ta zo mini.

Ban iya na dago na hada ido da M.K ba, wanda ke cin abincinshi cikin sukuni da kwanciyar hankali wanda na alaqanta nan take da ganin Kausar da yayi.

"Daddy ya ce ki dinga joining dinmu, ki daina tsawwalawa kanki zaman daki. Ni na lura ma wani ba dai-dai kike ba, wot's wrong?"

Na girgiza kai, babu amsa, don nima din ban san abin da ke damun nawa ba.

Bani da zabi ban da in hau tebir. Feeling somehow a betrayer. Na sanya serving-spoon ina dibar abincin daga cikin warmers, wadanda na tabbata babu inda zan kai shi.

Haka muka tsatstsakuri abincin daga ni har ita, uffan M.K bai ce mana ba, miskili ne na karshen-karshe.

Mami 'yar bokon zamani,

“tun da ba za ku bude baki ku furta ba, na dade da gano ku, bari in bi ku in ga iya gudun ruwanku.....”.

Abin da kowannen mu ya fahimta daga gare ta ke nan.

Don haka shima M.K a darare ya aje cokali, ya mike. Ko sashen da nake bai kalla ba. Ya koma cikin kujerar falo ya kishingida hankalinshi akan zaben tashar tabijin (ko zaben mata za’a ce tsakanin Fatima da ‘Yarta?) oho shi ya bar ma kansa da zuciyarsa sani.

Nima mikewa nayi jiki a sabule, na nufi hanyar daki, jikina ya bani Mami bin mu take da kallo, daga ni har shi.

Mace ma'abociyar ilimi da aiki da hankalinta, duk kam da al'amarin nan na ci mata rai, na dunqule mata a kahon zucci, to amma ya za ta yi da mu? Kowannen mu mahaukaciyar tsimagiyar soyayya ta fyade shi, mugun fyade kuwa.

Duk hukuncin da za'ai mana ai mana, ai dai ba mu furta ba, don haka ba ta da hujjar cewa soyayya muke ko jin nauyin juna? Tun da a da can, ai bama shiri.

Ta kuma lura tun dawowarta daga Dubai ne al'amarin namu ke neman sauya taku, ni dai na tabbata, bani kuma da shakku akan rantsuwata, na rantse ko zan mutu ba aure, ko soyayyar za ta kashe ni, ba zan taba auran MK ba, domin Mami Uwa ce a gare ni, uwar ma irin Mami? Idan har zan auri M.K, ashe kuwa zan auri Baffana,Jibir mai rasuwa, da kuma mijin da mahaifiyata ke aure.

****

Duk yadda ya yi don ya wanke zuciyar Mami da matsananciyar soyayya a wannan daren, Mamin ta bijire, ta ki ba da hadin kai, abin da ba ta taba yi ba ko da wasa.

Lallashi na duniya, ban baki na duniya, kwantar da kai na karshe ga macen da ake matukar so Mu’azzam Kanti ya yi, ko a jikin Mamin.

"Sati guda…! We’re not together, alhalin kinsan ke kadai gare ni…..Mami ki taimaki mijinki mai kaunarki……..Binta……".

"Kauna Mu’azzam? Wace iri kenan?”

Ta fada cikin matsanancin kuka wanda a yau ya fasa sirrin dake zuciyarta.

"Kada ka mai dani mahaukaciya mana? Na ganka sanda kake lalube min waya ka dauki nambar Kausar, haka ne ko ba haka ne ba?"

"Ba haka bane, ke dai kawai tsarguwa ki kai. Yau ne na fara taba maki waya? Laifin me ma na yi miki ne at all Binta ban sani ba!".

"Kana son sani? To bari in gaya maka abin da na dade da sani. Ka gurbata min 'ya da soyayyah…… ka hanata sukuni. Kana son ruguje min ginin da na yi shekara da shekaru ina yi akanta.

Ido baya boye soyayya ‘no matter what…, to haka reaction and emotion. You are in love Ibraheem…… (Sunan da ba ta taba kiranshi da shi ba). "…….Unimportant luv kuma.

Tun da za ka hada mu ka aura ne? Shi ne abinda ban sani ba. Nake kuma son in sani? In haka ne ashe za ka iya auren Houda? To na gode! NAGODE MU’AZZAM!!!".

Ya yi qokarin kamo hannunta, ta fizge, ya kai mata runguma ta goce, ya kai mata kissing ta hankade shi….

"Tsakanina da kai Ibrahim…..sai Allah ya isa……..!!!"

Ba ta yi aune ba, ta ji saukar wawan mari akan lallausar kuncin ta. Jin ta da ganinta suka gushe na wucin gadi. Ta kai hannu za ta rama wata zuciyar ta ce "A'ah". Ta sauke hannun ta kasa a hankali.

Ganin haka kuma ya kamata ya qanqame da karfi, dukkanninsu nishi suke saki a jikin junansu. Kamar wadanda su kai gudun 1000m. Duk yadda ta yi don ta qwace kanta ta kasa, karfin ba daya ba. Sai ta sa kuka, kukan da ta dade tana hana kanta yi akan Da namiji.

Ya sassauta rikon da ya yi mata cikin kirjin shi irin na larabawan Casablanca. Zuwa lokacin ta soma nutsuwa, ko ba komi ta samu ta furta masa abin da ke cin ta a zucci.

"Ki gaya min me na yiwa 'yar taki na soyayyar? Idan na yi zan ce, na yi, idan ban yi ba zance ban yi ba.

Akan me za ki yi min Allah ya isa? Akan laifin da ban sani ba? Ki kira ta ki tambaye ta, cewa nayi ina son ta?!"

Mace mai rauni da saurin yarda da mijinta, a hankali ta soma yarda da dadadan kalamanshi, gami da azababbiyar soyayyar shi. Sai ta soma tunanin lallai laifin na Kausar ne, tun da ita ce mai tsananin jin nauyin shi, jin nauyi kuwa alamun so ne. In haka ne kuwa za ta iya karkato da zuciyarta a hankali zuwa karatu, har yanzu tana cikin shekaru na kuruciya, ‘in her teens’ ba ta isa a kira ta mace ba.

As a mother, she can control her. Ba za ta barta ta ruguza rayuwar ta da soyayya a banza ba.Soyayya wadda bata da riba, soyayyar da aka gina akan kuruciya da sha’awa. A ganin ta Lanton, bata kai wannan gejin ba.

Ko daya ba ta ga laifinta ba, ba kowacce mace ce zata iya kau da kai akan Kanti Mu'azzam ba. Tana kuma da yakinin cewa, tashen balaga ke damun Kausar, amma ba soyayyah ba. A tunaninta fa ke nan.

Cikin wannan week-end din gaba daya tattalin Mami yake kamar jaririya, duk abin da ya san yana bata mata rai ya guje shi, ya daina cewa Lanto ta zo su ci abinci, ya daina hira da ita, ya daina neman ta cikin gidan idan bai ganta ba.

Gare ni na ji dadin hakan, ko yaushe ina cikin daki ina karance-karancena cikin text books na abin da nake son karanta, watau kimiyya.

Har ya koma wannan satin bai kara yin abin da zai bata ran matarshi akan Kausar ba, duk wani feeling ma da yake da shi akan Kausar ya neme shi ya rasa, wanda ke tabbatar mishi da cewa, kwanciyar hankalin Fatima-Binta shi ne nashi.

****

Sai ya zamanto duk zuwan da ya yi in bai ganni ba baya nema, nambar wayar ma da ya sata a wayar Mami ya goge ta daga cikin wayarshi, amma bai goge ta daga cikin kwanyar kansa ba, yayi-yayi kokarin hakan ya kasa. Sai dai kuma bai taba gwada kira ba ko da wasa. Nambar ta zauna ne kawai daram a cikin kansa.

Iyakacin ganin shi da ita idan sun shigo daga lesson ne da suke yi a karshen sati in zasu wuce dakin su, ko da Mami a wajen ko babu za ta gaishe shi ya amsa, ita ma Mamin ta daina daura ido.

Jarrabawarmu ta fito, na yi matukar qokari fiye da zaton Mami, babu abin da na fadi. Ba da jimawa ba na samu admission a jami'ar Bayero, duk da yadda admission dinsu yake da matukar wuya kuwa a wancan lokacin sai mai sa'a. Ta hanyar lashe jarrabawar ‘screening’ da suka kira ‘post-UME’.

Sai dai maimakon kwas din da na nema watau MBBS, Microbiology suka bani. Na amsa na karba cike da godiya a raina a matsayin shi ne zabin Allah.

Na soma daukar lectures cikin nasara tare da fatan Allah ya taimake ni in fita kunyar iyayen dakina. Domin tun daga farkon farawa na fahimci abun da kamar wuya.

****

Daddy ya shirya mana kai ma Mukhlis ziyara kasar Turkiya a karshen shekararshi ta biyu a can, ni kuma a zangon karshena na shekarar farko a jami’a.

Ina daki muna ta aikin makaranta ni da Muslim, don Huda da Nur suna Sultan Road wajen Hajiyar Mami. Na yi saurin dawowa ne yau daga makaranta don ko jiran direba ban yi ba, taxi na hawo drop har kofar gida, sakamakon rashin zuwan lecturer.

Don haka Mami ba ta san ina nan ba, don sanda na shigo tana toilet tana wanka.

Kuma ko da na ji murda kofarta da fitowarta falo ban fito ba, don hankalina ya tafi ga tattara assignment da nake yi cikin littafin Anatomy. Magana take a waya wadda Allah ya bawa kunjuwana ikon zuqowa.

"A wane dalili za ka ce in kaita passport, me za ta yi da shi? Mu tafi da ita Turkiya akan me? Karatun ta fa? Har a week end ba su da hutu……!”..... “Zan kaita M.K, me ya yi zafi? In ka yi hukunci bani da qauli".

Hankalina ya tashi matuka, wato da gaske Daddy ba zai daina abin da yake yi din nan ba? Da gaske burinshi ke nan ya assasa kiyayya tsakanina da Mami? Eh, burinshi ke nan, tun da ya san abin da yake yi din nan ba kyautawa yake yi ba.

Washegari Mami ta ce dani in shirya za mu dan fita. Kai tsaye ‘Nigerian Immigration Service’ muka nufa, aka yi min duk abubuwan da ake yi don karbar fasfo, aka ce mu dawo bayan kwana uku mu karba.

Ni kuma na rantse in har tafiyar nan da M.K a ciki, to ba zan yi ta ba. Already su Huda duk suna da fasfon, don ba yau suka fara fita kasashen qetare ba, duk sanda M.K ya dau annual leave waje suke fita su huta, duk da ba kowace shekara yake daukan ba.

Haka a zamana a gidan sun fita ya fi a kirga, to amma shi da Mami kadai, ni da yara ake bari a gida. Ban ga dalilin da za a ce yanzu dani za ai ba, salon in hana su sakewa su da iyalinsu, nima in takura kaina. Mukhlis din ma da ba wani shiri yake yi dani ba.

Ana i gobe tashin Daddy ya iso, Mami ba ta nan ta je (Zainab Saloon), inda ake wanke mata kai. Baba Larai ma ta tafi cikin gari ta gano 'yarta, yau throughout bani da lecture, don haka ina kicin ina harhadawa Mami kayan girki waje daya kamar yadda ta umarceni kafin ta fita.

Sallamar Daddy cikin kasaitaccen sautin sa wanda ya fi na Cyril Stober (NTA Abuja) amo da fidda sauti rangadadau, ta tsinkayi kunnuwa na.

A zuci na amsa cikin damuwa, da tasowar wani abu mai ta da tsigogin jiki. Koko wani warkakken miki daya rigaya ya warke a jikin dan adam. Ya Allah ka cire min soyayyar wannan bawa naka, ko na samu sa'ida.

Har kicin din ya biyo ni, ya tsaya daga bakin kofa shi bai shigo ba shi bai fita ba, hannun damanshi dafe da qyauren kicin, na hagun rike da suit din shi, jikin shi sai 'yar cikin da zanzarewarsa.

Ya yi matukar kyau kamar yau ya fara sanya suit, kuruciyarshi ta kara bayyana, kai ba ka ce shi ne ya haifi Mukhlis ba. Sai dai ka ce Yayan shi ne.

Ni dai na san shi mutum kullum shekarunshi gaba suke, yana kara tsufa. Amma Mu’azzam Kanti sai ka rantse da Allah kullum kara masa kuruciya ake.

A hankali na juyo na dube shi, tsigar jikina ta tashi yarrr! Har zuwa yatsar kafata. Ya karasa shigowa ya iso inda nake har muna hada kafada, na yi saurin ja da baya, ya sake biyo ni na kara ja da baya.

Haka mu kai ta yi har na tadda bangon kicin na yi tuntube da lokas, ya sanya dogayen hannuwanshi duka ya sanya ni a tsakiya ya hana min hanya ya kankane kowanne bangare.

Kamar in yi kuka, shima kamar ya yi kuka. Na ce.

"Mene ne hakan Daddy?"

Ya langabar dakai abin gwanin ban tausayi, kamar ba Mu'azzam Kanti Mu’azzam ba. Anya ko M.K din Mami ne wannan???

"Na daina yaudarar kaina Kauthar da cewa wai zan iya haqura da soyayyarki, qarya ne wannan!".

Na soma qokarin sunkuyawa ta kasan hannunshi in wuce don tserar da rayuwa ta, ya kamo ni ya qanqame ya mamaye ni cikin wasu irin abubuwa da ban taba tsintar kaina a ciki ba, ko a mafarki. Ban kuma san ana yi ba a duniya.

Tunani da hankalina suka gushe na wucin gadi, bana ji bana ganin komai a duniya ta da kwakwalwata da ruhina bakidaya sai Muazzam Kanti Mu’azzam. Hakan bai hana positive sashe na zuciyata gayamin haramcin hakan ba a addinin mu (kissing) tunda ba aure ne tsakaninmu ba, kuma ba da kowa ba sai da mijin Fatima-Binta? Matar data tsamoni daga qangin rayuwa ta mutunta ni ta martaba ni, martabawar da jinina basu yi min ba, ta gina rayuwata positively! Ashe a duniya babu sauran amana indai akan soyayya ne? Shin kasa rike ragamar zukatanmu da mukayi akan soyayya da manta halacci bazai dakusar da zuciyar taimako da aminci ba a zuciyar mata irin MAMI ma’abota karamci da kyautatawa ga wadanda ke karkashinsu??

Da wannan tunanin da wani sabon tsanar kaina da ya dirar min na angije M.K, daga qarqashin maqogaro na na ce "M.K Mami…….".

[1/1, 14:07] Nrs Zainab A S: Ya ce "Kausar…….. Mu'azzam, shima mutum ne abin a tausayawa, da da yadda zaiyi da haka bata faru da shi ba, sai ki zaba, UWA ko MIJI?"

Ya ci gaba da yin abin da yake yi din (passionate kiss) kamar maganata ta kara mishi qaimi ne maimakon ta ankarar da shi, babu inda baya karkarwa a jikinsa, ni kuma na yi saranda na miqa wuya da duk abinda Allah ya hukunta a gare ni.

Cewa yake cikin kankanuwar murya,

"In ta hana ni auren ki Kausar ……. ai ba za ta hanani wannan ba……!"

Kalami na karshe kenan da Fatima-Binta ta tsinkaya cikin kunnuwan ta. Bayan kyakkyawan ganin data yi, ta yi saurin juyawa kafin kowannen mu ya ankara da ita, ta yi dakinta ta bame kofa.

Karar rufe kofar tata ne ya maido mu cikin hankulanmu, duk da cewa a hankali ta rufe.

"M.K don Allah.....don rasulillahi.....ka fita rayuwata, ka tuna wacece Mami agaremu nida kai, ka taimaki rayuwata kada ka raba ni da Mami, banida kowa sai ita, ta yi min komai a rayuwa....". Na fadi cikin matsanancin kuka tareda sulalewa a kasa na zauna a dandaryar kasa.

"Ke ba ki san soyayya ba ruwanta da wannan.....? Yau da addini ne yace babu aure a tsakaninmu Kausar zan bi umarnin ki, I know my wife just give her time".

"Na ji, amma ka fita, ko ni ka barni in wuce, idan Mami ta dawo ta tadda mu fa?"

"Mamin ta sani, ta san ina son ki, kuma da sannu za ta fahimce mu, saboda ita mutum ce mai tausayi da jin qai.....".

"Ka yi min alfarma.... na hadaka da girman iyayenka, ka daina yin abin da kake yi dinnan a kaina..... ka daina shiga rayuwata, ka taimake ni ka taimaki Mamar mu.....".

"Nima ki taimake ni Kauthar, ba ni na sanyawa kaina ba, kuma bani kadai na ke son ki ba. Sai dai ki ce pretending kawai kike yi wanda ni na kasa....". Sai na rushe da kuka.

"Abu daya nake so da ke Lanto, idan Fatima ta tambaye ki kina so na ko bakya so na? Ki dubi Allah ki fada mata gaskiya.....".

A razane na kara cira kai na dube shi, ya daga min gira. "Eh, ita din yadda kika zace ta ba haka take ba, mace ce mai dimbin kauna da alfarmomi a gare ni, farin cikinta shi ne nawa, ita ma farin cikina shi ne nata.

Da sannu za ta yarje mana muyi aure mai suna aure kin ji Kauthar? Ki kwantsr da hankalinki. Sai ku ci gaba da zamanku da babbar hujja, in ba haka ba ke da itan masu rabuwa ne tun da ko ba dade ko ba jima gidan auren wani za ki. To gida bai koshi ba kinga ya dace a kai dawa?"

Takaici, bakin ciki da tausayin Mami suka kara dabaibaye ni, kamar in dora hannuwa aka in ce wayyo Allah! Ya fahimci ya gama hada min zafi, don haka ya juya ya fice yana kara jaddada min tafiya dani Turkiya babu fashi.

Can ya cimma Mami a daki zaune tsakiyar gadonta ta hada kai da gwiwa ta rasa abin da ke mata dadi a duniya, ta nemi digon hawaye a idanunta, ta rasa.

Namiji! Sai a barshi.

"Wa ya tabo min uwar Mukhlis ne.....".

Sauran maganar makalewa tayi a makogaronsa sakamakon kallon da Mami ta cira kai tana yi masa. Ji take kamar ta kashe shi ta huta, so yake ta kori Lanto, so yake ya farraqa wannan yardar da wannan amincin da sunansa na Da namiji kusan zuma, to ta kore ta ta je ina? Kishi bazai sa hankali da tunaninta da tausayinta su gushe ba. Ita din ma'abociyar, hankali da imani, tausayi da sanin ciwon kai ce.

Ya karaso gefen gadon ya zauna, ya kamo hannuwanta ta fincike. Bai yi aune ba sai jin saukar lafiyayyen mari ya yi a kuncinsa, sannan ta bi shi da muguwar shaqa.

"Gara in kashe ka kafin ka kashe ni.....!'

"Saurara Fatima in miki bayani.....".

"Bayani? Bayanin me? Na karerayi da yaudararka? Allah ya sa idona ya gane mini ba wani ne ya zo ya gaya min ba, balle ka ce anyi maka qage.....".

"Na ji ba ai min qage ba, kuma na rungumi 'yarki, na tsotsi bakinta. Bayan wannan Binta banyi komai ba. Sai dai nima ban san me ya kaini ga yin hakan ba, soyayya .....Mami. .....soyayyah!"

"Soyayya M.K?"

Jikinta ya saki yaraf kamar kayan wanki, yau ita M.K yake gaya mawa yana yiwa wata diya mace soyayya kwatankwacin wadda yake mata. Ya ya sunan maza ne? Mugaye, Mayaudara, Marassa Hankali, tun da basu san ya-kamata ba.....

Ta cika shi ta koma gefe ta soma rera masa kuka. Ya sake bin ta cikin lallashi ya kwantar da kai a kafafunta,

"Na haqura Binta, na haqura Fatima, wallahi ba zan aure ta ba.

Kin fiye min kowa Binta, bayan mata ta sunna ke UWA ta ce, data bani dukkan kauna a sanda bani da iyaye, ta tallafe ni a sanda bani da komai, ta auri marayan da ba Uwa ba Uba, alhalin tana cikin gatanta. Uwa-uba ta haifa min iyali son kowa, tare da ba su tarbiyya abin alfaharin kowanne Uba. Tun da na kasance mai bata miki rai da cin fuskarki haqiqa na yi asara!

Magana ta karshe Fatima ki dauki Kausar ki mai da ta inda kika dauko ta shi ke nan, zan yi kokari in yi ma zuciyata linzami.

Amma idan har tana tare damu bani da tsimi bani da dabara akan al'amarin da ke faruwa da ni".

Ta kama mijinta ta rungume, tana addu'ar kada Allah ya nuna mata ranar da za ta raba su, ko ta maimaita kuskuren da ta yi (marin mijinta).

"Forgive me M.K?"

"Na yafe miki duniya da lahira, nima ai rannan na mare ki, ramawa ki ka yi".

Ta ciro kanta daga kirjinsa,

"Kaima ka rama".

Sai ya rama mata da fatar bakinsa.

"Ni kuma ba zan kori Lanto ba, she mean a lot to me….".

"Shi ne dalilin da ya sanya ita bakya ganin laifinta sai nawa?'

"Me ta yi wanda zan ga laifinta? Waya take maka ko binka take yi? Kula ka take ko ita ta ce ka dinga yin abin da kake yin? Gaba kake da ita ka fi ta shekaru da tunani, kai ne ya kamata ka yi wa kanka birki, don ba zan taba iya hada shimfida da 'yata ba, sai dai ka zaba ko ni ko ita?'

"Na zabe ki Fatima-Binta, wallahi na zabe ki. Tafiyar ma an fasa da ita, na rantse miki na haqura da Kausar har duniya ta nade."

Suka koma ma abin da ya fi komi muhimmanci a gare su, har wayewar garin ba wanda ya kuma jin duriyar su, ko abinci ba su nema ba.

****

Sun tashi kasar Istanbul a washegari tareda dukkan ‘ya’yansu, gida ya rage daga ni sai Baba Larai. A washegari ina falo ni kadai ina aikin assignment na tsinkayi dirin mota, kafin kararrawar kofar shigowa ta ankarar dani akwai baqo mai son a bude mishi kofa.

Sanye nake da wani bakin material mai laushi, dauke da dinkin da bai kama jiki ba, riga da zani da kallabinsu.

Na bude, muka yi arba ni da wani mutum, saurayi mai matukar kwarjini, fari sol, ko ko in ce, jajawur. Sai dai kuma abin da ya shagalar da idona ga kallonsa shi ne, komi da ke zane a fuskarsa, wato hanci, ido, baki irin na Mamin Yara ne.

Ya karasa shigowa fuska a sake, da ganin shi ka ga mutumin da yake jiqe cikin ingantaccen ilimi na addine ne ko na bokon? Akwai fara'a da faram-faram a tattare dashi, don a take ya sakar min murmushi.

Na ba shi hanya ya wuce har tsakiyar falo, muka gaisa cikin mutunta juna. Ya ce, "Ya na ga gidan kamar ba kowa?"

"Eh, sunyi tafiya ne zuwa kasar but Turkiya".

"Dubo Mukhlis ke nan?"

Na gyada kai.

Ya ce, "Ni sunana Sagir, kanin Mami ne Uwa daya Uba daya. Ke kuma fa? Don ban san ki ba".

Na zauna a kujerar da ke fuskantar tashi,

"Anya hakan zai yiwu? Kana dan gidan su Mami ba ka sanni ba?"

"Allah sarki, shekaruna takwas rabona da gida, dawowar ke nan jiya-jiya na ce bari in zo in ga 'yar'uwata, don tun jiya nake neman layinta ba ya shiga. To ashe ba ta kasar ne".

Na mike zuwa kicin ya bi ni da kallo, na juyo kadan ya yi saurin kau da kansa. A niyyata in kawo mishi lemo da ruwa, amma sai wata zuciyar ta ce,

"A'a, na koma inda na tashi na zauna".

Ya yi murmushi ya ce

"Ba lemo za ki kawo min ba? Kawo min mana?".

Cikin mamakin yadda aka yi ya karanci zuciyata na mike na isa ga kicin, na dauko gwangwanin lemon Rany mai sanyi da gorar ruwan Eva, da tambulan na aza a karamin tray, na karaso mishi da su.

Ya ce, "Thanks".

Ya bude ya juye a cup din ya kai bakinsa, kurba daya-biyu-uku ya ajiye.

"I would like to ask, wace ce ne?"

"Hadimar Mami ce!".

"Hadima kamar ya ya?"

"Eh, to hadima zan ce, tunda ni ke kula da hidimar yaranta ina kuma taimakonta a kicin, ita din kuma tana min riko na uwa da 'yarta, ta yadda idan na ce ni hadimarta ce ranta yake baci. Don haka zanyi mata karar, har a bayan idonta kamar yadda take so, in kira kaina, 'Yar Mami".

Ya yi murmushi ya ce, "Wonderful. Karatu kuma fa?"

"Ina shekara ta farko a jami'ar Bayero". "Ana karanta mene?"

"Microbiology ne".

Ya sake cewa, "Wonderfully good, Allah ya sa mu a danshin ma'aikata kiwon lafiya".

Wasa-wasa sai ga shi na sake da Sagir muna ta hira, hirar da ban taba sakin jiki na yi da wani da namiji ba. Sagir akwai fara'a, saukin kai da son hira. Har labarin iyayena na ba shi da yadda a kai na zo gidan Mami. Sai dai na lura yana da wata al'ada guda daya wadda bana son ta ga da namiji, watau smoking.

Ya gaya min ya kare karatunshi a kasar Moscow, ya fito da kwalin likitancin yara, ba da jimawa ba zai fara neman aiki.

Mune da hira har karfe tara na dare, shakuwa da aminci mai tsanani Allah ya hada ya qulla a lokaci guda. Da kyar ya duba agogo ya ce,

"Kausar kina da dadin hira, kin shantakar dani kada Hajiyata ta yi min fada".

"Ta yi ma fada? Sai ka ce wani yaro karami?'

"Babba ma ana mishi fada Kausar idan ya yi abin da bai kamata ba, tun da cike take da dokin ganina".

"Allah sarki, haka ne kuwa?"

Ya fiddo kan wayoyin shi guda uku daga aljihu, ya ce, "Ungo wannan muke communicating ko? I found a good friend".

Na yi murmushi,

"Ina da waya, sai dai in ba ka nomba".

"Bana son wayarki, da tawa nake so ki dinga amfani. Ko kina tsoron kada saurayinki da ya ba ki ya tuhume ki?"

Na kai hannu na toshe baki cikin dariya, "Kai Uncle Sagir, ni bani da wani saurayi, Mami ce ta saya min Allah".

Ya sauke wani asirtaccen numfashi, ya ce,

"In haka ne karbi wayata. Mami ba za ta ce don me ba".

Na miqa hannu na amshi lafiyayyar wayar da ban saba gani ba, sai ko a hannun irin su Daddy, na ce,

"Na gode".

Ya dau nambarshi ya zuba a ciki, ya sanya sunan "Uncle Sagir" yai saving. Haka muka yi sallama kamar ba za mu rabu ba, da alkawarin gobe in Allah ya kaimu tunda yake lahadi ce da wuri zai zo ya tayani gadi, tun da nazama 'yar gadi, amma fa idan hakan ba zai zama takura gare ni ko karatuna ba".

"Zai zama kam, amma ga karatun nawa, gab muke da fara jarrabawa".

Ya ce, "Shi ke nan, Allah ya ba da sa'a, am not in a hurry, daga nan har a kare jarabawar ma dinga gaisawa ta wayar".

Na ce, "Wannan din ma kam ban saba ba, kuma zai dinga raba min hankali"

"To ni kuma Kausar ya ya za ki dani?"

"Ban gane ya ya zanyi da kai ba, goyo?"

Ya yi murmushi, ya ce, "Tukunna, ki dai yi min wannan alfarmar ki dinga daga kirana".

Na gyada kai kawai. Ya ce, "Mu kwana lafiya".

"A gai da min Hajiya da kyau".

"Za ta ji".

Har bakin motarshi na raka shi muna daga ma juna hannu har ya fice a gate.

Abun kamar sihiri, tun daga ranar muka zama wasu irin gam-da-gam ni da Sagir, a waya kawai. Ban kuma bari wayarshi ta shafi karatuna ba, mun qayyade lokacin waya kamar wasu mata da miji, da safe da daddare kawai. Sai next da yake yawan aiko mani, ba dare ba rana. Wanda hakan ya haifar da wata matsananciyar shakuwa da kauna a tsakanin mu.

Bayan dawowar su Mami a ranar Mami ta ganni da sabuwar waya, ta nemi jin ba'asi.

"Ya ce shi kaninki ne, the same parents, ya zo mun sha hira, yace ya dawo karatunshi daga Moscow".

Ta rungume ni ta ce "Sagir is back?'

"Eh. Sagir ya ce mani sunanshi".

"Tashi maza shirya mu tafi, yau gidan Hajiya za mu kwana, hira da dan'uwana".

Daddy ya balla mata harara

"Ai sai ki je ki kwanan, tunda ke ce ke auren kanki".

Ta langabar da kai,

"Don Allah M.K?'

"Wallahi ba za ki kwana ba, ku je dai ki yi mishi sannu da zuwan ku dawo".

Muka shirya fes, dukkaninmu kowa ya yi kyau, ba ga yaran ba ba ga manyan ba. In da ni ce Mami, nake haifar da wadannan zuka-zukan 'ya'yan banga abin da zai sanya ni yin wani family planning ba, watakila kuma daga ita har maigidan ra'ayinsu ke nan? Allah masani.

Hajiya ta rasa ina taka-saka-ina-taka-aje da 'yan jikokinta. Jin ana oyoyon zuwan Mamin yara Sagir ya iso dakin Hajiyar, in da a can kowa ya baje suna ta zubawa Hajiya labarin kasar Turkiya, wai Yaya Mukhlis ya zama qatoto. Ta kawo musu wannan ta kawo musu wancan.

Hada idonmu ke nan muka sakarwa juna ni'imtaccen murmushi. Ya ce

"Kausar din Mami". Nima na ce, "Sagir din Hajiya".

Kowa yai dariya. Hajiya ta ce,

"Wai ni Binta sai yaushe za ki aurar da diyar taki ne?"

An soso ma mai gyambo inda ke mishi qaiqayi, ya zauna dab dani yana wani kankance ido, duk kunya ta kamani, musamman da na fahimci Mami na kallon mu, ta yi uwa ba ta gane kome ba, ta ce

"Sai randa Allah ya kawo mijin ina ce? Wannan ba ta da saurayi ko daya bakin jini ne da ita, ko za ki sa a dinga yi mata rubutun farin jini ne?"

Sagir ya qyalqyale da dariya,

 "Amma Mami kin yanki gayu".

"Yo wannan wani gayu ta iya? Ita ke nan kullum cikin Pakistani da Abayat, ko irin dan fente-fenten nan da 'yammatan zamani ke yi su zama kamar turawa ba ta iya ba, wa zai taya? Don ma Allah ya taimake ta fara ce, da abun ba zai yi mata kyau ba".

Sagir dariya yake sosai, nikuma na ya mutse fuska ina kallon Mami, ya ce

"Hajiya ba sai kun wahalar da kanku ba wajen yin rubutun farin jinni, ga miji Allah ya kawo ma Kausar har gida....." Ya nuna kansa.

"......Ko ba kya so na Kausar?'

Da-dai na ga in na zauna mutumin nan zai ci gaba da tsinkani da yawa, sai na tashi na bar musu dakin. Daga ganin fuskar Mami da Hajiya ka san sun matukar jin dadin wannan al'amari.

Mami ta ce, "Da gaske kake Sagir? Bana son wasa".

"Babu wasa cikin maganata, da zarar na samu aiki na yi settling komai nawa zan auri Kausar, idan har za ku bani ke da M.K?". Ta ce,

"Me zai hana?"

****

Muje ga littafi na biyu wanda tare suke da dan uwanshi don muji shin wanene mijin Lanto? MK din ko Sagir din?

[1/1, 14:07] Nrs Zainab A S: ALKAWARI BAYAN RAI ASALINSU

Asalin su Mami mutanen garin Hadejia ne, mahaifinsu Justice Mukhtar Muhammed aiki ne ya kawo shi Kano. Jin dadin zaman garin Kano ne ya sa ya baro mahaifarsa ya zo nan Kano ya sayi gidan da suke ciki a yanzu.

Su biyu kacal iyayensu suka haifa, kuma shekaru biyu ne kacal a tsakaninsu, wanda Bintan ta bawa Sagir.

Rayuwar Justice Mukhtar Muhammed da iyalinshi rayuwa ce abar koyi mai tsari mai ban sha'awa, babu abin da yake gabansu kamar kula da cigaban rayuwar su da neman na kansu. Ko da suke manyan 'yan boko, basa wasa da kasuwanci da garin Dubai. Don haka asirinsu a rufe yake babu abin da suka nema suka rasa a rayuwarsu.

Sun kuma dauko 'yan'uwansu na kauye marasa aikin yi sun dora akan kasuwancin su cikin amana, don wanda ke kula da shagon Mami ma kanin Justice ne uwa daya uba daya. Ita kuwa Hajiyar Mamin nata shagon na turaruka ne ‘Haramain’ da na wuta da su gawayin Dubai a kantinan dake layin Sabon Gari na Kano. Tun haihuwar Sagir ta samu matsalar da dole aka juya mata mahaifa.

A shekararta ta biyu a jami'a ne ta hadu da Mu'azzam Kanti, a lokacin shi yana karatun ‘master’ duka a Jami'ar Bayero, yana karatun kimiyyar sadarwa tana nazarin kasuwanci.

Rannan ne ta je cin abinci shagon ‘Al-Amir’ da ke cikin B.U.K suka hadu a kujera mai fuskantar juna, da ganin shi kaga irin daliban nan da basu da komi sai karatun, jeans din jikinsa kodadde kuma dan gwanjo. Ba a maganar kodaddiyar shirt dinsa. Haka nan Allah ya kimsa mata kaunar sa, ta samu kanta da biyan kudin abincinsu su biyu.

Ya dube ta da kyawawan idanunshi ya ce, "Ya ya za ai haka?"

Ta ce "Babu komi, niyya na yi".

Ya ce "To na gode, amma next timekar ki sake".

Ta yi murmushi ta ce, "It's my pleasure in sake next time din, sai idan bamu hadu a ‘restaurant’ din ba".

Ya ce "gashi ni kuma dama ba al'adata ba ce shiga ‘restaurant’ din ba, ni nake dafa abincina da kaina, yau din ma a masifar yunwace nake, shi ya sa".

Ta ce "Shi ya sa nake sha'awar rayuwar Campus, saboda irin wadannan experiences masu koya ma mutum rayuwa ta dogaro da kai".

Haka suka ci gaba da hirar Campus har tsayin wani lokaci. Su kai exchanging phone no da address na gida. Shi yana zaune ne a cikin quatersdin malamai gidan wan babanshi, wanda ke rike da shi tun rasuwar iyayensa a hatsarin mota tun yana karami.

Ba shi da komai sai kokari, kuma ba dan kowa ba. Irin daliban nan ne gifted da malamansu ke alfahari da su, don kuwa duk tsangayar su shi ya fiddo first class a zamanin yaye su daga digiri na farko.

Wasa-wasa sai abin nasu ya rikide zuwa mahaukaciyar soyayya. Ya san bashi da abin da zai auri Binta a yanzu, dama ko wacce mace tun da bai da madogara, sai Allah.

A lokacin da ta shiga mataki na uku mahaifinta ya uzzura da son yi mata aure, ko don ta raba shi da mazan da ke kara-kaina a kofar gidansa.

Kai tsaye ta gabatar mishi da da Kantin a matsayin wanda take son aure, duk kuwa da irin 'ya'yan manyan da ke rububi a kanta, da 'ya'yan abokan Babanta.

Mahaifin nata ya bukaci ganawa da shi, ya kuma amsa kiran.

"Binta ta gabatar min da kai a matsayin wanda take son aure, na sa anyi min duk wani bincike da ya kamata in sani game da kai na kuma samu daddadan feedback, how do you see it?'

Ya lankwashe 'yan yatsun hannunshi cikin na juna, a ladabce da kunyace ya dukar da kai, ya ce,

"Da gaske nake ina son Binta, sai dai bani da halin aure a yanzu, ina neman aiki ne, ban kai ga samu ba".

"Me ka karanta?"

Ya ce

"Kimiyyar yada labarai ne(mass comm.)".

Ya ce

"To a kawon takardun in gani ko zan iya taimakawa, nima in tayaka neman aiki".

Har gobe ba zai manta da Justice Mukhtar Mohd ba, wanda ya zamo silar duk matakin da yake da shi a yanzu.

Hatta gidan da za su zauna a ciki shi ya ba su a nan kusa da su, ya ce kafin Allah ya ba shi halin sayen nashi. Ya sama mishi aiki a N.T.A Abuja da albashi mai tsoka.

Shekaru uku da aurensu ya sayi gidan da suke ciki a yanzu, ya bai ma Justice nasa. A lokacin sun haifi Mukhlis. Rayuwarsu ta ci gaba da mikawa har zuwa matakin da suke kai a yanzu.

Yana aikin ya nemi izinin tafiya karo karatu a Jami'ar Harvard. Da ya dawo aka kara mishi matsayi, duk wasu kwasa-kwasai da ya yi bayan nan wajen aikin ne suka tura shi.

Don haka Kanti Mu'azzam har gobe yake tunawa da wadannan alfarmomi na Mami da iyayenta, ba ya da kamar su, ko shi butulu ne ya hakura ya barma Mami 'yarta.

To idan shi din ya hakura ya tilasta kansa da hakurar ita natacciyar zuciyar fa? Soyayya ce wadda ta fi karfin tunaninsa, ta shallake saninsa, wadda bai taba ji a diya mace ba. He is sorry to say it again "INCLUDING MAMI". Addu'a yake yi akan Allah ya cire mishi amma kullum kamar yana kara izata.

** **

Ya koma bakin aiki ranar lahadi da yamma, kuma a ranar ne da daddare Sagir ya zo da shirin samartaka. Duk budurin nan bai san ana yi ba, ita Mamin ba ta gaya mishi ba ko da wasa.

Ya kasa haquri da karasa jarrabawar tata, soyayyar Kausar ta yi mishi mugun kamu. Support 100% daga iyayensu da Yayarsu.

A galabaice ya zauna cikin 3 seater din Mami, a sa'ilin da ni kuma ke bisa kilishi ina cin abinci. Muka yi ma juna kwal da ido kamin mu saki dariya sassanya a tare.

"Na kasa haquri ne Kausar, jarrabawa ta ki karewa, har yaushe ne?"

Ya sauko ya sanya hannu cikin plate dina muna ci tare.

Haka ya mai da gidan Mami wajan hirarsa, dandalin soyayyarsa da walwalarsa. Ya yin da Mami ke kara jika mana soyayyar da goyon baya, da shawarwari na yadda za mu kaima cikar burin mu. Kullum ba zai zo ba sai ya qunsowa su Nur chocolate da Ice-cream, don haka ya sa suka manne masa uwa babansu, saboda ba sa ganin hakan a mahaifinsu,verystrict, though, unsocial person.

Cikin nasara Sagir ya samu aiki da AKTH bangaren yara (paediatric). Soyayyarmu kuwa sai abin da ya yi gaba, sai dai ya rage zuwa saboda aikinsu na dare da rana, sai a waya muke haduwa.

Ranar wata sunday ya samu rangwamen aiki, daga hospital din bai koma gida ba kai tsaye ya taho saboda akwai muhimmiyar maganar da yake so su tattauna shi da 'yar'uwarsa.

Da ganinsa ka ga Dr. Sageer Mukhtar Muhammed, irin mazan nan ne masu razana mata da kwarjinin da Allah yai musu.

Rataye a hannunshi na hagu lab-coat dinshi ce. Ni dai na san ina da kyau, amma har sai nake ganin Sagir din yafi karfina.

A gajiye yake muraran, Daddy na gida ya kara yi ma Allah godiya. Daddy ya dube shi ya ce,

"Da alamun the Doctor is hectic". Ya ce "Ba wani abu yunwa ce kawai, ya ku ke?'

"Kowa lafiya". In ji Mami.

Mintuna wajen talatin suna ta hira shi da Daddy, yana ta zuba ido ya ga giftawa ta ban fito ba, ya dubi Mami, "Wai ina mutuniyar ne?'

Mami tace "Tana daki, ban san me take yi ba, yarinya sai ka ce huda-huda, ban taba ganin ta babu takarda da alkalami a hannunta ba".

Daddy ya ce

"Doctor Sageeruaure sai yaushe ne? Ina ganin lokaci yayi da zaka aje iyali.

Ya ce "Bari in fito, sai in ba ka bayani".

Nan ya ajiye coat dinsa ya karaso dakinmu.

Muka sakarwa juna soyayyen murmushi, ya zo ya zauna dab da ni ya tankwashe kafa, ya kai hannu ya zare biron da ke hannuna ya soka min cikin gashin kaina, wanda ko kallabi babu. Gashin yala-yala mara tsaho yake kallo cikin al'ajabi, bai

taba sanin haka gashin yake ba. Ya rufe text book ya hada da jotter ya dauke su ya yi baya da su.

"A dinga hutawa ana bai ma maigida haqkinsa, wannan ko karatun likita kike sai haka, haba Kausar, kar ki bari kwakwalwarki ta motsu da karatu mana?".

Na yi murmushi kawai, Allah na tuba idan ban yi karatu ba me zan yi? Ba uwa ba uba babu dangi, sai dosanannen danagi. Tun ina sa ran watarana zan ga iyayena ko su su neme ni har na fidda rai. Ya ya za a yi Sagir din ya aure ni bai ga iyayena ba? Karatunnan shine gata na shine rufin asiri ga rayuwa ta. Wannan tunanin kadai ya sanya jikina yai matukar yin sanyi.

Ya lura da hakan, don haka ya kai hannunvshi bisa havata ya dago ni mu kai facing juna, hucin numfashinsa na dukan hancina.

Dukkanmu bamu ankara ba sai ganin Mami da Daddy mu kai a kanmu, bai razana ba, bai kuma canza daga yadda suka same mu ba. Ya juya ga Mami ba tare da ya cika havata ba, ya ce

"Mami me ke damun 'yarki?"

Daddy kallon mu yake cikin rashin fahimta, gaba daya fuskarshi ta sauya. Ya juya ya fita, Mami ta bi bayan shi ba tare da ta ce uffan ba.

"Me kuwa ke damuna? Ban da soyayyar Sagir da fargabar ba zai iya aurena babu iyaye ba".

"Ki dubi Allah Kausar ki gaya min me ke damun ki? Kada ki manta aure za muyi, idan kuma kina da wani ne da kike so ki gaya min mana, domin farin cikinki da kwanciyar hankalinki shi ne nawa. Kausar ba zan takura miki ba idan ba ki na'am da ni ba".

A matsayina na mai son nesanta kaina da al'amarin Mu'azzam Kanti, dole in ba da goyon bayana ga Sagir, don cimma rayuwa mai amfani, amma ba don soyayyarsa ta dada ni da kasa ba. Na fi kwatanta shi da aboki mai dadin mu'amala fiye da masoyi.

Idan kuma ni din har mace ce mai lafiya a jiki, kuma wadda ke da bukatar da kowanne dan adam ke da shi, to zan iya auren Dr. Sagir mu kuma zauna lafiya cikin mutunta juna, amma ba cikin soyayya ba.

Bani da excessive love feeling a kanshi irin wanda nake da shi akan mijin mamata. So daya ne rak, na Mu’azzam Kanti ne. To amma ya za ai na furta mishi wannan? Don haka na furta wadda nake ganin za ta fisshe ni.

"Ina tunanin iyaye na ne, Doctor Sageer, ba zan iya aure ba tare da su a kusa dani ba".

"Ni kuma a shirye nake da na aure ki ko da a ce ba ki da iyayen, ko da a ce daga sama kika faxo. Iyayena duka sunyi na'am da ke, haka 'yar'uwata ko ba'a san iyayenki ba, ke an san halinki, a kalla an zauna da ke shekaru masu yawa anyi miki kyakkyawar shaida.

Don haka daga Hajiya har Justice sun yadda da ke. Kuma ai ba haka za a yi mana auren ba a nemo dangin mahaifin naki ba".

Hankalina ya nutsu da kalamin shi, na yi murmushi. Ya ce "To ya ya? kin amince ko a'ah?" Gyada mishi kai na yi.

Ya matso dai-dai kunnena na dama ya rada min kalmar "Lanto, na gode".

Ya cimma Daddy a falo, wanda har zuwa lokacin bai koma dai-dai ba, ita kanta Mami ta kasa gane mishi, wani kallo-kallo ya ke wa Sagir kamar a wulakance,kuma kamar a rashin fahimta.

Shi Sagiru kam bai kula ba, ko kuma ya kula din ya yi mishi ta 'yan boko oho? Gabanshi ya zube ya ce, "Daddyn yara, maganarmu ta dazu, na ce bari in shiga in fito sai in baka bayani".

"Wacce ke nan?'

"Ta cewa da ka yi ya kamata in aje iyali".

"To ka samo din?"

"Eh, na samo, kuma a karkashin ikonka, gidanka da yardarka....."

........"Wa ke nan?"

Babu haufi dircct ya ce

"Kausar Mu'azzam Kanti".

Yake ya yi, wanda aka ce ya fi kuka ciwo. Kafin ya tattaro nutsuwa da hankali ya dura a zuciyarsa, ya daure matuka ya yi saranda, da kyar sautin ya fito daga bakinshi.

"Kausar din 'yar makaranta ce ina ce?"

"Eh, 'yar makaranta ce, Baban yara, amma ai karatun baya hana aure. Ca nake kai da Mami ma haka ku kai, ba ta gama karatun ba ka aure ta?"

"Anyi haka, amma ka bani lokaci in yi nazari, ita ma Kausar din akwai bukatar in tattauna da ita, don mun ji ta bakinka, ita ba mu ji nata bakin ba. Mai yiwuwa kai din ne ka gani kana so, ita ba ta ce tana son ba, kuma ba za mu yi mata auren dole ba a matsayinta na amanar Allah a hannunmu".

Jikin Sagir yai sanyi lakwas, don ya lura kamar Kanti bai yi na'am da zancen ba. Ba haka yake gani a sauran mutanen da ya yiwa wannan albishir din ba.

"Har zuwa wanne lokacin Mu'azzam?'

"Bani nan da sati daya".

"Ya yi min nisa".

"Ka daure da hakan".

"Shi ke nan, Allah ya jishshemu alheri".

** **

[1/1, 14:07] Nrs Zainab A S: "Ban gane abin da kake nufi ba?' Ta fada dai-dai lokacin da ya shigo dakin barcinsu yana kokarin yi masu light up. Ya kashe ta kunna, ya sake kashewa ta sake kunnawa.

"Tun kafin in ci kwalarka, ka gaya min me kake nufi akan kanina? Kana tsammanin yana da wata manufa ne ko wani mugun hali da za a hana shi aure a kansu?"

"To ki ci kwalar tawa man sannan in gaya miki. Mtss!" Ya ja wani matsiyacin tsaki ya juya zai fice ya bar mata dakin. Ta sha gabansa.

"Wallahi sai ka gaya min me kake nufi da Kausar kafin ka bar dakin nan".

"Kada in mare ki Binta.....".

"Ka marenin mana, ai ba yau ka fara marin nawa akan Kausar ba.....".

Karfi ya sa ya angije ta yai ficewarsa.

Mami ta zauna a nan bakin kofa ta dinga rusa kuka. Ba ta tausaya ma Kausar kamar yadda take tausayin Sageer, yadda ya dauki son duniya ya dora a kanta. It wlll be a heart break, idan ya ji cewa wai shima surukin nashi sonta yake yi, mai yiwuwa ne ya janye ya ce ba zai hada hanyar neman aure da shi ba. Dole ta shigar da manya a zancen dan abin ya shallake tunaninta.

Washegari ta shirya sai New-Site (gidajen malamai na jami'ar Bayero wajen Baffan M.K.). Bayan sun gaisa da Karima matar Baffa, ita kanta ta lura Bintan na cikin damuwa.

Ta ce, "Ta zo ganin Malam ne".

Ta ce, "Kash! Yanzun nan ya shiga cikin makaranta, amma ya ce ba jimawa zai yi ba".

Don haka ta ci gaba da zaman jiran sa, suna ta hira da Karima har malam din ya dawo.

"A'a-a'a! Yau Maman Mukhlis ce a gidanmu, jiya-jiyan nan na gama magana da shi a waya, yake ce dani karatun saura shekara biyu".

Ta ce, "Haka abin yake, shekara kwana".

Ya ce, "To Allah ya bamu sa'a, amin. Ya maigidan to? Kwana biyu ban ji duriyarsa ba".

Ta ce, "Ai zancen shi ne ma ya kawo ni".

Aunty Karima ta basu waje. Ta kwashe komi ta gaya mishi tun daga dauko Kausar da ta yi, ta kare da cewa, "Babban abin da nake gudu shine, kada yaran su farga da rashin amincewar sa hakan zai karya masu zuciya".

Malam ya dube ta sosai ya ce,

"Ni kam Binta, da za ki bi shawarata sai in ce ki kyale Mu'azzamu ya auri yarinyar nan, tun da dai ba haramun bane. In kin hana shi auren wadda kika san halinta ai ya kwaso miki fitsararriyar da za ta zo ta wargaza miki gida, maza ba a yi mana haka ki barmu da abin da muka gani muna so. Gara wannan kin santa, kin san halinta ciki da bai dinta, idan ita ma tana son shi, kinga kin zalince su".

Gaba daya jikinta ya yi sanyi, hankalinta da nutsuwa suka zo mata, ba ta san sanda ta bude baki cikin fadin "Har ga Allah na amince M.K ya auri LANTO".

"Ba sai na shiga lamarin ba ke nan?"

"Ba sai ka shiga ba, ka barni ni da kaina zan gyara kurakuraina zan shirya komi".

Ya ce "To Allah ya yi miki albarka, ya daukaka zuri'arki, ya kare ku daga sharrin makiya da mahassada. Na ji dadi kwarai da kika dauko al'amarin kika kawo gare ni, ba ki kai inda za a ba ki gurguwar shawara ba. Daga yau duk abin da yai miki na vacin rai ko na nuna fifiko a kan yarinyar ki zo ki gaya min ki ga yadda zan yi da shi, sai ya gwammace uwarshi ba ta haife shi ba.

Saboda mu ba butulu bane, sai dai aure sunnar ma'aiki ne, bai kamata ki yi shisshigi da nuna iko a cikin lamarin aure ba, ki mutu su ki bin ki da addu'a, su zo

suna cewa gara da kika mutu, kuma suyi aurensu su zo suna cewa da ba ki mutu ba da ba su samu wannan 'yancin ba".

Ta kara razana, hawaye fal idonta. Ta ce, "Wallahi tallahi malam na yi nadama, na tuba Allah ya cire min kishin".

Ya dauko biro ya dinga rubuta mata addu'o'i nagartattu na neman yardar Ubangiji, kasancewar shi H.O.D na Islamic Studies ne.

Ta dawo gida cike da wata irin nutsuwa da karin imani, cike da tunanin hanyoyin da za ta bi ta kara musu soyayyar wadda ba da dadewa ba take fatan suyi aurensu, Kausar ta ci gaba da zama a dakinta a matsayin matar gida.

Hakika tana tunanin dama ranar da Sagir zai dauke Kausar ya barta ita daya, ba za ta taba samun mataimakiya irin Lanto ba, tabbas Kausar din ALHERI ce a gare su. Wancan abin kai mai kama da jela shi ake ma kishin, bayan kuma Kausar din ba gutsire mata shi za tai ba, to taimakon da Lanto ke mata fa? Duk da suma suna taimaka mata ne amma ba za su iya biyanta da zuciyarta da amanarta data mallaka musu ba. To amma sai me?

** **

Baje suke a falon shi da Sagir da tarin envelop suna ta rattaba sunaye. A fitar da Mamin ta yi wadda ya tabbatar ba ta dadi ba ce ya san kararshi za ta kai, shi kuma idan akwai abin da ya tsana a rayuwarshi bai wuce a ce yau ya vatawa Baffan nan nashi da ba ya da kowa a duniya sai shi, ya gwammace in karar ce to ta kai ma Justice fiye da ta vata shi a wurin ubanshi, don bai iya daukar zafi ba.

Tana fita dakin Lanto yai sallama, daga bakin kofa ya tsaya ya harde hannuwanshi a kirji, idanuwanshi sun kada sunyi jawur, jijiyoyin jikinshi duk sun miqe musamman na kansa sun yi rada-rada kamar mai fama da matsanancin ciwon kai.

Ya ce, "Wurin ki na zo, Kauthar!"

Na dago a hankali na dube sa, ganin tension din da yake ciki gaba daya na tsure, tsorona Allah kar a maimaita 'yar gidan jiya wanda har yau ban daina istigifarinsa ba.

"Sagir ya gabatar min da yana neman aurenki, kina son shi ko bakya son shi?"

Babu haufi, babu dogon turanci na ce, "Eh, inason Doctor Sageer". Yanayin yadda na bada amsar gatsar babu kunya ya bala’in bashi mamaki.

Ya qura min ido kamar yai kuka, idanunshi a kaina still ya ce, "alright, game da lokacin aure ko kina da wani lokaci da kika ware da nufin yin aure a cikinsa?".

"Yanzu ma a cikin hutu nake?"

"Which mean....?'

"....., am ready".

Ya lumshe ido, a hankali yai murmushin da bai taba yi ba, yayimin kallon sakaryar banza kafin yace

".....Allah ya ba da zaman lafiya Kauthar!"

Daga haka ya juya ya fita.

A take ya kira Sageer ya ce, "Ya je ya bugo invitation card na daurin aure yanzu-yanzu, next weekyake so a daura auren".

Abinki da mai neman kuka....., amma ya danne zalamarsa.

"So soon haka?"

"Haka nai niyya, in kuma ba ka yi sai ka bar masu yi suyi".

Ya ce, "Na tuba na bi Allah na bi umarninka, yanzu zan je na sanar ma Justice, daga nan zan biya wajen masu bugun I.V".

Ya ce, "To ka hanzarta dai".

Kafin Mami ta dawo sai ga Sagir da bandiran katina da albishirin Daddy ya amince a daura aure sati mai zuwa.

"What a sacrifice?' Mami ta furta a hankali, a yayin da hawayen idonta suka zubo, ta yi kokarin kar su zubo amma sai da suka zubo din a tafin kafar Kanti Mu'azzam, wanda ya fada ya rame ya bushe a lokaci daya.

"Kada ayi haka M.K.....". A yayin da ta dauki katin daya tana dubawa bayan fitar Sageer. Ya kamo matarshi ya rungume, cikin dauriya yace ".....Zan iya barin komi don in faranta miki Mami, kada ki karya min gwiwa, support dinmu suke nema.....".

Shi kuka ita kuka, abin gwanin ban tausayi.

Washegari ya tattara ya koma bakin aikinsa, da cewa duk abin da ake bukata a sanar da shi ta waya ba zai zo ba sai friday wato ranar daurin aure idan an sauko daga sallar juma'a kamar yadda aka rattaba a jikin katin. Ta ce, "Su kuma Dubai za su wuce domin sayayyar kayan aure". Hakan kuwa aka yi.

Bayan mun auno kayan mun dawo, nake gaya ma Mami bana son taron biki daurin auren kadai ya wadatar. Ta ce,

"Saboda ba ki da kewaye? To ni ina da su, don haka sai na shirya liyafa.

Ana i saura kwana biyu daurin aure ne muka yi shirin tafiya Bujawa. Ni, Mami, Sagir da wani abokin Justice Alkali Muhyidden.

In ban da faduwa babu abin da gabana ke yi, don ban san irin tarbar da Laminde za ta yi musu ba, tun da a tsayin shekarun da Baffa ya rasu ban zo na duba ta ba, sai yanzu da nake neman madaurin aure.

Amma akasi ga tunanina, Laminde ta yi mana kyakkyawar tarba, ta yi mana shimfida ta kawo mana ruwa a kwanon sha mai tsabta. Ta ce, "Uhm! In gaya miki Lanto, watan da ya wuce wasu turawa suka zo neman ki, sun ce su dangin uwarki ne, don Haladu dan gidan Malam Mummuni na kira ya yi mana tafinta. Na nemi Hajiya Hajara na rasa, dan ita kadai ta san inda kike, sai kuma marigayi.

Ala dole suka hakura suka koma, amma sun ce duk ranar da Allah ya kawo ki na karvi adireshin inda kike na ajiye musu watarana za su dawo".

Dukkanmu mun kidime, barin ma Sagir, ya ce, "Amma dai Inna kin san tana garin Kano, Kano kuma ba vuyayya ba ce".

Ta ce, "In na san tana Kano na san inda take a cikin Kanon?'

Haushi da takaici ya ishi kowa. Ta sake cewa, "Tun da Baffanki ya rasu ba ki kara leko mu ba, idan ni ba 'yar'uwarki ba ce a kalla zan ci darajar riko, kuma ki yi zumunci da 'yan'uwanki".

Kowa ya ce, "haka ne, Kausar tana ba ki haquri Inna".

Ta kira Sale ta ce, ya je ya kira Baffa Lawal mai bin Yaya Hajara. Gidansa babu tazara sosai tsakaninsa da gidanmu.

Baffa Lawan ya iso yana ta lale da baki, ya ce, "Lanto ba ki kyauta ba, saboda ni ba Baffanki bane tun da Baffan naki ya mutu ba ki kara gaishe mu ba".

Na sunkuyar da kai na yi ta ba su haquri, ya ce, "A to, kanki ki kai wa. Arniyar uwarki ta turo neman ki ba mu san inda kike ba".

Na ce, "Babu komi, inda rai da rabo watarana za mu hadu".

Ya ce, "Haka ne".

Mami ta gabatar da Sageer a matsayin mai neman aure na. Baffa ya sanya albarka, aka qulla komai na aure bisa al'ada da addini, muka baro su cikin dadin rai, bayan Sagir ya bi duk ya cika su da toshi.

An rabu akan ana saura kwana biyu direba zai zo ya dauke su. Har kuma Hajara da ke Jos za su tura mata ta taho.

M.K bai iso ba sai ranar daurin aure wato friday, ya hade cikin lallausar shadda fara kal, wadda kallo daya ya ishe ka kimanta daraja da qualitynta, sai walkiya yake duk inda ya gitta, sai ka ce shi ne angon. Sai dai kuma ya saya kwayar idonshi cikin dark space na ‘Prada’, ta yadda ba za ka gano halin da zuciya da kwayar idanunshi ke ciki ba.

Na sha tambayar kaina shin maza irin su MK nawa ne a duniya? A komi MK daban yake, a duk inda ya shiga baya da na biyu, wannan kuma baiwa ce daga Allah. Irin wadannan mutanen dai-daiku ne a cikin al’ummah,

Daurin auren da aka yi a masallacin da ke cikin unguwar Nassarawa ya tara albarkar al'umma da dama, duk daga bangaren su Sagir da mahaifinsa, sai 'yan tsirarun abokan Daddy.

Ba yadda Baffa Lawal bai yi da M.K ba akan ya karvi wakilcina amma ya ki, sai shi Baffan ne ya amsa akan sadaki naira dubu hamsin kacal.

Da yamma ne aka wuce 'Alliance Francais’ inda Mami ta shirya liyafa, ta yi min ado cikin laffaya ruwan sararin samaniya, kai ka ce baquwa ce daga kasar Mouritania.

Aka ci aka sha aka yi videos da photo, amma ba a dauko mai kida ba. Abin ma da babu wasu 'yan mata duk kawayen Mami ne, yawanci 'ya'yansu ne su kai min kawance, sai kuma course mates dina da muke mutunci, don ni kam bani da wata shakikiyar kawa, kowa abokina ne.

Shi kansa Sagir din ai a matsayin aboki nake kallon shi, bani dainfatuated feeling a kan shi. Shima angon yana can shi da nashi abokan suna tasu walimar a gidan Justice, wadda aka bankare raguna uku aka gashe, aka kyafe, sai naso suke, kuma duk abin da aka ci daga Chines Restaurant aka yi odar shi.

Sai da duhun dare ya shigo idanuna suka raina fata, yau fa ake yin ta, zan bar Mami, kannena da kyakkyawar rayuwarmu? Ina! Sagir ya sake tunani, na aure shi ba don ya rabani da Mami ba, sai don ci gaban abotarmu, ya ci gaba da zuwa gidan mana kamar yadda ya saba muna hirarmu". Na furta ga Mami cikin matsanancin kuka,

A yayin da ta karkace tana yi min kwalliyar amarci da wani farin cotton lace mai kananan duwatsu. Ya bi jikina ya kwanta saboda laushinsa. Ta kawo turaren 'fahrenhiet' ta feshe ni da shi. "AURE YAKIN MATA....." In ji Mami, wadda kuma can a karkashin zuciyarta wata irin voyayyar nadama ce.

Motocin daukar amarya suka iso, to nan fa ake yin ta. Nur da Huda, sun kama bakin kofar dakinmu sun kankane ba inda za ni, sai da aka ce har da su za a tafi sannan suka hakura.

Gidan da Justice ya saya ma Sagir yana nan a Hotoro G.R.A, gida ne flat mai dakuna ciki uku da falo biyu, kicin da store da study room.

'Yan kawo amarya suka watse, Mami ta lallava su Nur suka bi ta da alkawarin gobe za ta sa direba ya kawo su. Aka barni daga ni sai halina, ji na yi kamar kabari aka kawo ni aka binne, kowa ya watse.

Sagir da abokan aikinshi Doctors suka cika falon, ina jin su suna ta daru wai su lallai sai sun ga amarya, shi kuma ya dage ba wanda ya isa ya gane mishi mata.

A karshe dai su sukai nasara, don sun ce ba inda za su idan ba su ga amarya ba. Ya yi sallama a dakin ina takure gefen gado, kaina cikin gwiwoyina, in ban da rabzar kuka ba abin da nake. Ya zo ya zauna dab dani ya mika hannu ya ciro kaina daga cikin gwiwoyina, ya sa harshe yana lashe hawayen.

Ya ce "Wa ya tavo min my babe?"

Abu ne wanda ban taba ji ba, kuma ban taba gani ba. Sai da ya yi mai isarshi tukunna ya koma cikin nutsuwarshi, ya ce

"Taso muje ku gaisa da Doctors, sun dage sai sun ganki, na yi na yi su tafi sun ki".

Na miqe na gyara lulluvina, hannuna a cikin nasa muka yiwa falon kawanya. '"Fantastic!" In ji daya daga cikin su, "Allah ya bar kauna ya sanya alkhairi". Sagir ko kunya babu ya ce

"Amin".

Ya soma gabatar min da su, "Wannan Dr. wane ne, likitan ka za ne, wancan Dr. wane ne, likitan kaza ne".

Wani a cikin su ya ce, "Kai kuma fa?" ya nuna kanshi Ya ce,

"Ni Dr. Sageer Mukhtar Mohammed ne, likitan yara ne".

Aka kyalkyale da dariya. "Amma by now na koma likitan soyayya". Suka ce, "Allah ya ba da zaman lafiya Dr Soyayyah". Haka suka fice suna ta kwarara mana addu'a.

** **

[1/1, 14:07] Nrs Zainab A S: Ba zan iya cewa ga abin da zan dorar a first night dina ba ban da azaba. Amma a hakan ne Mami take ce dani wai auren abun so ne? Ina kalubalantar Mami. Idan wannan azabar ita ce auren, to lallai zan koma inda na fito.

Ga Sagirun ko a jikinsa, annashuwa yake yana kara zafafa soyayya. Albarka na shata fadi yake, wai 'yar jami'a ta kawo budurci gidan miji. "Am proud of you Lanto, may ours be among the bests!"

Daga ranar kuma bai sake kulani da wannan ba, don ya lura a matukar tsorace nake da shi. Sai bayan sati guda bayani ya sha bambam, aka koma 'yar gidan jiya.

"Da na san kai dan iska ne ma mugu, wallahi da ban amsawa M.K aurenka ba".

Dariya ya yi cikin matsanancin nishadi, ya ce, "To say I love you is not a way to express a feeling……".

"Wata sabuwar kalma ce wannan a cikin soyayyar wadda ban sani ba ko me?"

"Yeah, ba ki sani ba, bara in koyar da ke daki-daki, dalla-dalla……..".

Kamar ba Sageer ba, ban san ina ya koyo wadannan al'amuran ba. Ko naki ko na so cikin dan lokaci dole Sagir ya soma samun kyakkyawan matsugunni a zuciyata, fiye da matsayin da na aure shi a kai. Iskanci kuwa (kamar yadda nace) bai rage ba sai ma abinda ya karu.Maimakon tsana, sai ma hakan ya rikide ya koma sayo masa matsananciyar kauna a zuciyata. Lallai miji ba wasa ba.

** **

Satinmu uku da aure muka tattara muka koma gidan da asibiti ta bai ma Sagir cikin AKTH. Sagir ya ci gaba da aikinsa cikin nasara da kwarewa, yayin da nima na ci gaba da karatuna cikin kwanciyar hankali.

Sau daya na je gidan Mami ban kara ba, saboda yadda su Nur ke rikicewa idan zan tafi. Ita Mamin tana zuwa a kai a kai, ko ina da wata damuwa? Tana so ta ji, in akwai in fada mata, ta yi min maganinta, in babu in ce mata babu.

Yo me Sagir din ma zai yi min na rashin kyautawa? Kullum cikin tattalina yake da tattalin farin cikina. Miji ne na fita rsara kuma abin alfahari, don haka a kullum kara son shi nake.

Ko da wasa Mami ba ta taba yi min zancen M.K ba idan ta zo, ban kara jin duriyar shi ba, kuma nima ban tambayeta ba. Na tuntuvi Mami ko za ta sake neman mai taimaka mata ne? Ta ce, "Baba Larai ta isheni 'after all', yara duk sun girma sun iya kula da kansu. Wani zubin ma kafin in tashi daga barci sunyi shirinsu sunyi tafiyarsu". Nima din ko da wasa ban taba gwada tambayarta M.K din ba.

Katsam Mami ke gaya mani aikin da M.K ya nema da gidan talabijin na CNN ya fito, za su koma kasar America da zama, sabon wata mai kamawa.

Duk inda hankalina yake to ya dugunzuma ya tashi, na yi ta kuka kamar raina zai fita, na ce, "Ni sai dai in bisu, na fasa auren".

Ta ce, "Kar ki damu kanki Kausar, ga Hajiyarmu ga Justice suma iyaye ne a gareki. Uwa-uba mijin da ke matukar son ki, ki rike su kamar mu, babu abin da muke yi miki da ba za su yi miki ba".

Haka kukana da tashin hankali na bai kara ko ya rage komi daga hijirar su ba.

A kullum kokarin Sagir shi ne ya faranta mini, ya dadada mini da soyayya da kulawa. Nima kuma ina iya kokarina wajen kyautata mishi, sai dai can a karkashin raina wani gyambo ne wanda har yau bai warke ba, ban kuma san ranar warkewar sa ba. Don haka na tattara al'amarin na mika ga Allah, ina mai rokon shi jagoranci a rayuwar aure na.

Duk wani masoyin M.K na gaskiya ya taya shi murna da samun wannan aikin, ya kuma yi tattaki har gida ya je ya taya shi murna.

To haka Sagir ya ce in shirya ranar asabar da daddare mu je muma mu yi wa Daddy congratulations.

Ni kam da Sagir zai yi shawara dani sai in ce da bai sani cikin 'yan taya murnar nan ba, bana son duk wata alaka da za ta sake hadani da Mu'azzam Kanti. Tun da na yi aure bamu kuma haduwa ba, kuma bana son haduwar tamu. Allah shi ne kadai masanin wannan sirrin, don haka shi kansa Sagir ya lura da sauyawar da fuskata da gangar jikina ma gaba daya da ya yi zancen zuwa yi ma Daddy murna tare da ni.

Na lura jikinsa ya yi sanyi, ya kuma shiga cikin wani dan tunani. A satin gaba daya ban gane masa ba, ya birkice min kamar ba shi ba, ya zama wani irin mutum mara umh mara umh-umh. Sai dai yai ta bi na da kallo kamar yau ya fara ganina.

Na yi tunanin ko kin ba da goyon bayana da zuwa yi wa Daddyn murna ne ya vata mishi rai? Don haka na ce mu shirya muje, shi kuma ya ce "Fau-fau ya fasa".

Yana kwance cikin rest chair, bayan ya dawo daga aiki, rike da jaridar ‘Triumph’ yana nazari, na zauna dai-dai kafarshi ina mishi tausa a hankali, ya janye kafarshi ba tare da ya ce dani ko ci kanki ba.

Na kwace jaridar na ce, "Sagirrr!".

Da wasu irin rinannun idanu ya dube ni, kala bai ce min ba.

"Na rasa kanka cikin 'yan kwanakin nan, na yi tunanin ko na yi laifi ne ban gano ba? Na bincika ko daga ina kuskuren nawa yake in gyara, Allah bai bani ikon gani ba. Ina so ka gaya min don Allah don darajar iyayenka laifin me na yi maka?" Idanuna suka cicciko.

Kamar ba zai yi magana ba, tsayin mintuna a kalla goma kafin ya ce, "You want to know?"

"Eh, I want know my mistake for reconciliation".

Ya yi murmushi, "Meye dalilinki na qulla gaba da Daddy?"

"Gaba? Wace irin gaba?"

Ya sake murmusawa, "Gaba mana? A tunanina ke ce mutum ta farko da za ta fara yi mishi murnar abin alherin da ya same shi, idan ba bakin ciki kike ba meye hujjarki na kin son zuwa ki yi mishi murna?"

"Na ce da kai hakan?"

"Ba ki ce ba, amma yanayinki ya nuna, kuma masu iya magana suka ce, "Labarin zuciya a tambayi fuska".

"Tunda dai ban furta hakan ba, ba ka da hujjar da za ka ce haka. Mai yiwuwa ni wani abu daban nake tunani a lokacin".

Ya ce, "Ko?"

Ban amsa ba.

"To bani wayarki?"

Ba tare da wani tunani ba na je daki na dauko na ba shi. Ya shiga lalube-lalube wanda ban ga dalili ba, yana zargina ne da voye wani abu a cikin waya ko me?

Ya caje wayata tsaf, kamin ya miko min abata. Yana kallona da wani irin murmushi mai lankwashe da azababben kishi. Na kama shi ya janye, na rungume shi a gigice.

"Kada ka tayar min da hankali Sagir, mene ne?"

Ya angije ni, "Ni ba mahaukaci bane Kausar, meye dalilinki na kin sanya nambar Daddy a dukkan wayoyin ki? Kina nufin ba ki da alaka ne da shi ko ya ya sai matarsa?"

"To yanzu me ya kawo wannan tambayar, ina ruwana da nambar Daddy?'

Ya sake kashe ni da wannan kallon da bana so, kallo ne mai cike da tuhuma, zargi da rashin yarda. "Ba ki da abin da za ki ce ma M.K a matsayinshi na wanda ya rike ki har auren ki?"

"To me zance da shi? In mun hadu ai za mu gaisa".

"Haka kawai ba za ki iya kiran M.K ki gaishe shi ba?"

Frankly speaking na ce, "Ba zan iya ba".

"Dalili?'

"Nauyi yake yi min Sagir, ina matukar ganin girmanshi".

"Ni kuma fa?"

A fusace na ce, "Ka isheni da silly questions Sageer……..why all these?".

Yayi wani irin murmushi cike da KISHI idanun shi a karkace yace

"Bana nufin komai da ke sai ALHERI, kina son MU'AZZAM KANTI".

Na sunkuyar da kaina domin na kasa jure kallon kishin da yake jifana da shi, a sanyaye nace

"Ni na gaya maka?"

"Ba ki gaya min ba, don haka a barshi a hakan, tsinkaye na ne kawai nake gaya maki b,a kuma cewa nayi lallai ki yarda da ni ba, hakkannan ba jayayya nake so muyi ba ‘it is my observation’, ki yafe ni. Sai dai ni na san ba zan iya saki in bar mishi ba, don nima ina son ki……!"

Sati guda muka kwashe cikin wannan takaddamar kafin Sagir ya sauko, daga baya kuma ya mance zancen shaf, don shi dama yana daga cikin irin mutanen da ba su fi ya sanya abu a ransu ba har ya zo ya dame su ya hana su aiyukan su. Musamman da wanda ake bidirin dominsa ya daga ya bar kasar shi da iyalinshi.

A wannan watan na lura ina fama da laulaye-laulayen shigar ciki, ni ce barci, kasala da kwarara amai. Gaba daya hankalin Sagir da kulawarshi sai ya dawo kaina. Ina matukar alfahari da samun Sagir a matsayin miji da babu ta inda ya rage ni. A haka na ci gaba da fama da karatu da laulayin ciki, har Allah ya sauke ni lafiya na samu Fatima-Binta, sunan da da gani har Sagir muka amince mu sanya mata ke nan.

Ai kuwa Sagir na yi mata albishir kafin suna da kwana uku sai ga ta ta iso da tsarabar baby rankatakaf, duk da ba abin da Sagir bai saya ba. Su Nur suna ta murnar samun kanwa.

A gidan Hajiya aka yin taron suna, wadda ta ce ba a kyauta mata ba tun da ba a yi mata kara ba, kanmu da Mamin mu kawai muka sani.

Ni da Sagir mu kai ta ba ta haquri da alkawarin next haihuwa idan mace ce ita ce, idan namiji ne Mukhtar ne.

Bayan haihuwar mai sunan Mami da watanni hudu, Sagir ya soma nuna min wasu abubuwa da bana ganewa. Alal misali, ya fi ya yi min zancen M.K da son gyara alakar mu da ta gurvata.

Abu na farko da ya fara yi shi ne, zuba min nambobin wayar M.K a wayata, ya kuma ce lallai a gabanshi in kira shi in gaishe shi, a cewar shi M.K bai cancanci gaba ba

daga gare ni. Koma mene ne a tsakaninmu a can baya ya wuce. Sai a manta a fuskanci gaba.

Dole na yi dialling nambobin akan idonsa, kuma a hands-free. Ta jima tana ringing kafin ya dauka. Ya yi magana cikin muryar nan tashi mai rikita ni da gigita ni.

"Salam, wa ke magana?"

Na yi ajiyar zuciya mai nauyi na ce, "Kausar ce".

Shiru ya yi bai ce komi ba. Na yi ta maza na tattara nutsuwata musamman da na tabbata Sagir observing dina yake. Ya Allah ka cire min wannan masifar, da aure na da iyalina ina ruwana da mijin Mami? Ko ma dai mene ne bani da laifi shi ya sani, da baya yi min zancen da tuni na mance da M.K, don haka ko yaya ne laifin nashi ne.

"Cewa za ki yi Mrs. Sageer Mukhtar Mohd.anyway. Ya kuke? Ya uwargidata?'

"Duk muna lafiya".

Tsigar jikina ta ci gaba da tashi, kirjina ya soma bugu, abin da nake gudu ke nan, amma Sagir din da gangan ya ki ganewa.

A sanyaye na mika ma Sagir din, na miqe nai daki ya bi ni da kallo. Suka ci gaba da hirar su ta tsawon lokaci, kafin suyi sallama.

Haka muka ci gaba da zaman da dadi ba dadi, shi yana tuhumata da don me na san ina son M.K shi na aure shi? Wannnan yaudara ce. Ni kuma ina mai kalubalantarsa da cewa, ni da zuciya daya na aure shi, amma wannan rashin yardar da yake nema ya vullo da ita, ita ce za ta cuce mu gaba daya, tun da dai na riga na yi aure ai magana ta kare. Idan na yi mishi irin wadannan kalaman sai ya ji sanyi.

Fatima na da watanni bakwai na shirya zuwa Bujawa, Laminde ta karve mu sosai. Mun je gidan Baffa Lawal mun gaisa, ya ce, "Har yau babu labari, masu nemana daga dangin mahaifiyata ba su sake waiwayo wa ba". Ya ce, "Amma in kwantar da hankalina, in da rai da rabo". Na ce "Haka ne".

A satin ne tafiya ta kama Sagir da mahaifinshi daurin auren wani cousin din Justice din zuwa garin Hadejia. Ni dai haka na samu kaina da bana son Sagir da wannan tafiyar, shi kuma sai xoki yake, a cewar shi ya jima rabonshi da garinsu.

Ya gama hadewa cikin kaftan ina tsaye harde da hannuwa jikin kofa ina kallon shi, ya yi kyau matuka ta yadda har na kasa dauke idona a kansa. Sha'awar mijina ta tsirga mini har kashi da vargo. A duk sanda irin wannan ta same ni yana ganewa, ya san kuma ko zan mutu da sha'awar ba zan taba furta mishi ba. Ina kallon shi yana dariya kasa-kasa, kamar bai san halin da nake ciki ba. Na san a ranshi cewa yake, "Yau dai zanga iya gudun rowan ki……".

"Ni bani hanya in wuce, kin wani kankane min kofa.....".

Na bi shi da idanu, ya sake kashe ni da shegun lumsassun idanunsa, ban san sanda na kama shi na kankame ba.

Duk wata kwalliyar daurin aure mun hargitsata, anyi squeezing dinta. Sai da muka dawo normal ya duba agogo, ina jin tun auren mu bamu taba samun gamsasshiyar soyayya ba irin ta yau ba, it's among the moments of history..... those unforgettable moments...precious and remembered!.

Sagir ya kasa sakina, kissing ya ke babu kaqkautawa. Sai da wayar Justice ta katse shi, da kyar ya mika hannu ya amsa, inda Justice ya fara yi mishi fadan shanya su da ya yi.

Muka kintsa muka fito, sai wasu kayan ya sake don na cukurkuda wadannan. A kofar fita falo ma ya sake ban peck a kunci. To haka da ya shiga mota ya tayar ya ce.

"Dan kara miko min kadan".

Na zura kaina ta tagar motar ya ci gaba da romancing yadda ranshi yake so. Da kyar ya ja motar yana daga min hannu tare da fadin, "Take care of urself.....Lanto". Cikin murmushi nace

"I will, in sha Allah".

Haka na zauna shirim a falo abin duniya du ya dame ni. Mai sunan Mami tana wurin Hajiya yaye, tun satin da ya wuce. Haka nan dai na soma samun faduwar gaba lokaci-lokaci.

Na kunna tauraron dan adam don raba kaina da tunanin da ke addabata, amma bana fahimtar duk wasu programme da ake gabatarwa.

Karfe hudu na yamma sai ga Idi direban Hajiya, da ganin fuskarsa ka san a dimauce ya ke, duk da yana kokarin voyewa.

Muka gaisa a takaice, ya ce, "Dama Hajiya ce ta aiko ni cewa in zo in dauke ki".

"Ga shi Doctor ba ya nan, in kiran ba na sauri bane me zai hana idan Dr. ya dawo mu zo da daddare?'

"Ai Dr. din ta gaya mishi, kuma shi ya ce in zo in dauke kin".

Gabana dai bai daina faduwa ba, karewa ma faduwar gaban yanzun ta fi ta farko. Mayafi kawai na dauko na yafa akan doguwar rigar da ke jikina, na bi bayansa bayan na sa key na rufe kofar shiga gidan.

Tun daga farkon layin har karshen sa cincirindon mutane ne, kuma abin mamaki a kofar gidan su Sagir cunkoso ya fi yawa.

Da kyar nake iya daga kafa kamar ba a kan kasa nake tafiya ba, hankalin kowa ya dawo kaina, ban tsaya ba sai a falon Hajiya. Nan ma cike yake da mutane, aka ce in karasa cikin daki Hajiyar tana can.

A yadda na ga Hajiya abun babu dadin fade, ta ci kuka har ta gode Allah, idanuwanta kamar barkono aka gumbuda musu. Na zauna a gaban ta a galabaice.

"Hajiya me ke faruwa ne? A fidda ni duhu".

Ta kamo ni ta rungume muka ci gaba da kukan tare. Tun ma ban ji musabbabin ba na tabbata koma dai mene ne ba mai dadin ji bane.

"Ki yi wa Allah Hajiya ki gaya min abin da ya faru".

Amma Hajiya ko uffan ba ta ce mini ba.

Wani dan'uwan Justice ne ya shigo, "Ina Kausar din? Ta zo an hada shi ta yi mishi addu'a, kema Hajiya ki taso".

"Wa aka hada?" Na tambaya cikin karaji?

Hajiya ta ce,

"Duk wani mai rai mamaci ne Kausar, muma nan duk ita muke jira, Allah ya yi ma Sagir rasuwa akan hanyar su ta dawowa, sun samu accident a take Sagir rai ya yi halinsa, Justice kuma yana gadon asibiti ya samu karaya har biyu a kafa, ki yi dauriya ki je ki yi ma mijinki addu'a.

Ta kama hannuna muka miqe tare, har falon Justice, inda gawar Sagir dina ta ke. Na dai bude fuskar na tabbatar shi ne, ban kara tantance me ke faruwa a duniyar ba.

****

[1/1, 14:07] Nrs Zainab A S: RAYUWA, JUYI

Sati biyu bayan rasuwar Sagir mutanen America suka koma, ko da yake shi Daddy dama kwana uku ya yi ya tafi ya barsu. Daddy ya zo har dakin Hajiya ya yi min ta'aziyyar maigidana.

Mami ta ce in ci gaba da zama nan gidan Hajiya in kare takabata kafin a san abin yi. Hakika mutuwar dan'uwanta ta doke ta fiye ma da Hajiya, ta rame ta yi fiyat.

Hajiya kuwa kullum karfafa min gwiwa take akan haquri da dangana. To Sagir din ne abin so ga kowa, kuma mijin da nake da tabbacin ba zan samu mai kaunata

kamar shi ba. Don haka maganar wai in daina tunanin Sagir ko in daina yi mishi kuka abune da na tabbatar har abada ba zai taba yiwuwa ba...!

***

Daki guda Hajiya ta ware min nake zaune. Da na kare takaba na koma makaranta. Ina cikin shekara ta karshe ne, don haka al'amarina babu sauki. Mai sunan Mami tana debi min kewa, kullum na ganta sai in ga kamar naga Sagir saboda tsabar kamannin su.

Bana yin sallah in tashi ban rokawa Sagir rahama da gafarar Ubangiji ba, a matsayinsa na wani mutum da ya inganta rayuwata 'positively'. Wani al'amari wai shi aure ya fice min a ka, Sagir kawai nake so, kuma Allah ya karva.

Hajiya da Justice suka soma damuwa da karakainar zawarawa da tuzurai a gidansu, ina sawa ana korar su.

Rannan muna zaune a falo take yi min fada akan in yi haquri in fidda miji cikin su in yi aure ya fiye min kwanciyar hankali, don har yau, shekara guda da rasa Sagir, ban koma cikin nutsuwata ba.

Na ce, "Hajiya idan kina tunanin zan iya hada rayuwa da wanin Sagir kin yi kuskure....."

Ta ce, "Ba ki yarda da kaddara ba ke nan Lanto?" Na sa havar zanina na share hawayen da suka kawo min zarya, na ce, "Na yarda da kaddara, to amma Hajiya auren ne kawai bana marmari, bana sha'awa. Gatan da za ki yi min Hajiya shi ne kawai ki dinga sanyani cikin addu'ar ki".

Ta ce, "Ai kullum ina yi miki Lanto-Kausar, Allah ya zava mana abin da ya fi ALHERI". Na ce "Amin".

Muka samu hutun zangon karatu na farko, a wannan lokacin ya zamanto na samu kaina da son neman shiri tsakanina da dangin mahaifina. Don haka na sanar da Hajiya ina son zuwa Jos wajen Yaya Hajara, daga nan kuma idan na kwana biyu sai in wuce Bujawa.

Direba ya ajiye ni a kofar gidan Yaya Hajara da misalin karfe biyar na yammacin ranar litinin. Na tsaya a kofar shiga na danna kararrawa, wata yarinya budurwa 'yar kimanin shekaru goma sha biyar ta zo ta bude kofar.

Ko ba ta fada ba na gane ita ce Hauwa'u diyar Yaya Hajara ta fari. Babu alamun sanayya ta ce, "Shigo".

Na samu gefen kujera na zauna ina nazarin dakin, muka gaisa cikin rashin sanin juna. Ta ce, "Mama ta je ofis amma ki jiraye ta tana kan hanyar dawowa.

Na tambaye ta, "Dama Mama tana aiki ne?" Ta ce, "Ma'aikaciya ce a bankin G.T watau (Guaranteed-Trust)". Ta kawo lemu da snacks ta ajiye mini. Abinki da jini, nan da nan muka saki jiki da juna muka soma hira sosai. Dai-dai lokacin da sauran kannenta suka shigo daga Islamiyya.

Yaya Hajara 'ya'yanta biyar, Hauwa'u ce ta fari, sai Gaddafi, Fa'iz da Fa'iza, da autarsu Maryam.

Shida dai-dai Yaya Hajara ta iso, bayan ta yi parking motarta a harabar adana motoci, ta shigo rataye da jakarta. Sanya kanta ke da wuya cikin falon ta yi turus, "Wa nake gani haka kamar Kausar? Yau a gidana?'

Na sadda kai kasa ina wasa da'yan yatsuna, na ce, "Ni ce Yaya". Ga dukkan alamu jikinta ya yi sanyi, a take nadama ta zo mata.

Wato dan uwanka dan uwanka ne, no matter what, ita taki Kausar, yau ga Kausar din ta biyo ta da kafafunta.

Sai da ta shiga bandaki ta yi freshen up gajiyarta, ta iskeni a falon. A take ta sa Hauwa'u ta shigar min da jika ta dakinta. Ta samu kujera mai fuskantata ta zauna, ta dube ni da idanun basira ta ce,

"Ya ya hanya, ya kuma Hajiyar Justice da babyn ki?' Na ce, "Duk suna lafiya, kuma sun ce a gaida ku". Ta ce, "Ki yi haquri Kausar, tun bayan rasuwar Sagir ba ki kara gani na ba, aiyuka ne sun min yawa, duk da haka na san ban kyauta ba". Na ce,

"Babu komi Yaya, nima ina karatu ne shi ya sa bana samun lokacin zuwa".

Yaya Hajara ta kara gyara zama ta ce, "Kausar ki yafe ni, hakika a can baya ban kyauta miki ba. Nice wadda ya dace in dauki dawainiyar rayuwarki, amma shaidan ya sanya ni ban yi hakan ba, sai yau dana ganki kin zama mutum nadama mara amfani ta same ni. Babu abin da mahaifinki bai yi min ba a rayuwata, amma da rashin arziki na saka masa.

A yau na ji kunyar ki sosai Lanto, ina rokon ki ki yafe mini". Na share hawayen da suke yi min zarya, na ce, "Abin da ya wuce ya wuce Yaya, babu amfanin a dinga tayar da shi".

Ta umarce ni da in je in yi wanka in huta. Na sanar da ita ina tare da direban Hajiya a yau zai koma Kano, don haka ta umarci mai aikinta da ta kai mishi abinci.

Kwana biyu gidan Yaya Hajara ya haifar min da wani jin dadin cewa, nima fa mutum ce kamar kowa da ke da dangin uba, wadda kuma wannan shine pride na kowanne dan adam. Na saba da dukkan yaranta, musamman Hauwa'u da muke kwana mu tashi daki daya. Maigidan Yaya Hajara Alh. Aminu mutumin kirki ne, don yadda yake

ja na a jiki kamar su Hauwa'u. Da na ce ina da bukatar zuwa Bujawa, Yaya Hajara ta ce sai dai mu tattara dukkan mu direba ya kaimu, saboda ita aikin ofis ba zai barta ba.

Sai ya kasance yau gani da kwana a dakin Inna Laminde ni da Hauwa'u da sauran yara. Washegari kuma gidan Baffa Lawal muka wuni, yana ta haba-haba damu, shima ya ce yana mai bani haquri, kuma har yanzu ba labarin Nasiru (mahaifina) suma turawan da suke nema na basu kara waiwayowa ba.

Bayan kwanaki uku muka sake komawa Jos. A kullum ita ma Yaya Hajara lallashi na take akan in yi haquri in yi aure, zaman haka bai kamace ni ba, tun da kuma ba rasa maneman na yi ba. Na kan kalle su ne kawai, amma can a karkashin zuciyata cewa nake ina zan kuma samun miji irin Sageer?

Sageer wani irin miji ne da samun kamar shi a wannan zamanin sai an tona. Mu yi wasa, mu yi dariya, mu yi girki, mu gyara gidanmu. Ya mai da kanshi bawa a gare ni, nima na sadaukar da kaina a gare shi. Yana tattalin farin cikina, yana bina da duk abin da nake so. Ya zamo wani bigire na zuciyata ta yadda faduwanshi ya kayar da zuciyata akan aure, na gwammace in yi ta yi mishi rainon diyarsa har illa masha-Allah.

Idan na yi wa Yaya Hajara wannan has ashen, sai ta ce, "Cikar imanin ki da mutuncin ki za ki duba Lanto, aure martaba ne, kina son mijin ko bakya son shi, ki yi haquri ki yi tawakkali, Lanto ki kasance cikin godiya ga Allah a bisa duk abin da ya zava miki".

Cike da kewar juna na baro Jos, saboda hutunmu ya kare. Yaya Hajara ta ce da zarar na kare karatuna wajen ta zan dawo, nima kuma na fi son hakan.

Na dawo ranar lahadi, washegari monday na koma makaranta. Mai sunan Mami na tare da Hajiya a kullum tana rainon ta, tana samun kyakkyawar kulawa, domin Hajiya ba daga nan ba, ta dauki son duniya ta dora akan Baby Fatima. Ta kan ce, "Ganin ta nake uwa Sageer".

Ranar wata lahadi ban iso makaranta da wuri ba, sakamakon tashi da Fatima ta yi da zazzafan zazzavin malaria, sai da na kai ta asibiti na mai da ta gida tukunna.

Don haka na iso a makare, already anyi submitting assignment wanda na kwashe kwana biyu ina hadawa cikin tsananin bincike a manyan littattafai. Don haka wata course-mate dina Blessing ta bani shawarar in je kawai in samu malamin a ofishinsa in ba da excusedina.

Sai dai kuma duk ajinmu ba mai iya tunkarar Dr. Habibu saboda thoughness dinsa, 'yan ajin da yawa sukan ce yana da jin kai, he is sticking on one word, (baya canja Magana), in ya karvi takardun 'yan aji ya karva ke nan, ba ya karvar excuse daga baya.

Na yi zurfi a cikin tunanin in je ne in ceci C.A dina ko ko in kyale? Daga baya na yanke shawarar in je din ko da kuwa zai kore ni ne.

Na yi addu'a kamin in yi sallama a kofar ofishinsa.

Na daga kai a jikin kofar shiga ofishin an rubuta Dr. Habibu Kofar-Sauri. Na yi qundunbala na shiga, bayan ya amsa sallama ta a ciki kamar baya so.

Ya yi min nuni da kujerar gefenshi na zauna, na fara gaishe shi, ya amsa. Kana na soma koro mai excuse dina cikin harshen turanci. Ga mamakina sai ya ce in ba shi takardun.

Na zage zip din jakata na dauko su, sai dai jikina ya bani ya qura min ido, ya sanya gilashi yana nazarin takardun, ya ce, "Kausar Nasir Bujawa?" Na ce, "Yes malam". Ya ce, "Shin ko zan iya sanin Kausar na da aure?'

Na rasa dalilin wannan tambayar, amma dai na nisa, "Maigidana ya rasu, shekaru biyu da suka gabata". Ya ci gaba da nazarin takardun kamin ya ajiye su gefe, ya ce, "Shi ke nan". Na taso na fito amma jikina ya bani kallona yake ba ya ko kiftawa.

Ina dakina da yammacin ranar ina harhada wani assignment din. Ayshe mai aikin Hajiya ta yi sallama a kofar dakina na amsa mata, ta ce, "Kina da bako a waje". Na yi tsaki cikin takaici na ce.

"Amma Ayshe sau nawa zan gaya miki idan an turo nemana a waje ku ce bana nan?" Hajiya ta jiyo mu daga falo, ban yi aune ba na ji ta yi kiran Ayshe ta ba ta makullin dakin baki, sannan ta ce, "Je ki bude mishi dakin baki ko wane ne ki ce gata nan zuwa"

Ta iske ni a daki ta ce, "Fita ki je, kina da bako ko nima za a aike ni a ce ba'a nan ne?" Haushi da takaici kamar in mutu, na zari zurmemen hijabin sallah ta na zurma na fita.

Sai me nake shirin gani ni Kausar? Dr. Habibu ne. Gwiwa a sage na yi sallama ya amsa. Ko da nake korar mutane na kasa korar Dr. Habibu saboda kwarjinin da ya yi min. Cikakken mutum ma'abocin wadatar ilimi da annuri, dan kimanin shekaru arba'in da haihuwa. Ta ko ina bai da makusa ko nakasu. A perfect gentle-man indeed!

Ya miqe tsaye cikin girmamawa, sai da na zauna sannan shima ya zauna. Ya yi murmushi ya ce, "Kina mamakin ganina ko Kausar? To kar ki yi mamaki, bincike mai

zurfi na yi a kanki kafin in zo gare ki. Don haka daina mamaki, garin masoyi ba ya da nisa.

Na yi ajiyar zuciya ina kallonsa, ban ce kala ba. Ya ce, "Ina Baby Fatima?" Na ce, "Tana cikin gida". Ya ce, "To don Allah ko zan samu alfarmar ganin ta?' Ban yi magana ba na taho cikin gida na dauko masa ita.

Ya karve ta ya dora a cinyarsa ya ce, "Very beautiful baby, Allah ya ji kan babanta". Na ce, "Ameen". Idanuwana suka cicciko.

Ko mene ne Sagir duk kai ka jawo mini, da ka tafi ka barmu. Ba don haka ba wa ya isa kullum ya jawo jiki ya ce ya zo yana so na? Na yarfe wasu matsiyatan hawaye da suka tsatstsafo mini.

Ya yi murmushi ya ce,

"Ina da irin ciwon ki Kausar, don haka ba zan yi mamaki ba ganin kina kuka a gabana don na ambaci baban Fati. Matata Madina ta mutu a wurin haihuwa ta barni da jariri Saddik, yanzu haka yana hannun Hajiyata, zai yi sa'an Fatima".

"Allah sarki". Na furta a hankali. Haka kawai na ji jikina ya saki da shi, soul-mate' wato we have the same feelings. Fatima ta sauko daga cinyoyinsa ta dawo gare ni, na dauke ta na rungume. Ya ce,

"Ina so in maye gurbin baban Fati ne Kausar idan za ki karve ni".

Na ce, "Na gode, amma ina bukatar lokaci in yi tunani Dr.". Ya ce, "Hakan yana da kyau, na ba ki daga yau har rana ita yau Kausar, Allah ya zama jagoran mu". Na ce, "Ameen".

Na dawo gida na shimfide Fatima wadda zuwa lokacin ta yi barci a kafaduna, nima na kwana cike da tunanin maganar Dr. Habibu. Alal hakika idan da wanda na taba jin zuciyata ta yi amanna da ya maye min gurbin Sageer, to Dr. Habibu ne.

Na farko dai ya mallaki hankalin kansa, na biyu yana da wadatar ilimi irin yadda nake so. Sai na uku yana da sana'a kwaqkwara mai tsabta wacce zai iya rike ni dan ita babu takura. Sannan daga sura har zuwa halayyarshi babu na kushe, don kowa yabonshi yake a tsangayar mu, musamman saboda kamewar sa.

Washegari muna kalaci Hajiya ke tsokana ta,

"Ko ke fa? Da alama shi wannan ya samu gwamnati, tun da aka share lokaci da shi". Murmushi na yi, "Malamin mu ne fa Hajiya". Ta ce, "Kai abu ya yi kyau, kinga sai ku yi ta karatun ku". Na yi dariya.

Mun yi waya da Mami a ranar kamar in shaida mata maganar Dr. Habibu, daga baya dai na yi tunanin in kyale ta kawai tun da ban ma gama tsai da hankalina akan maganar ba.

Wasa-wasa sai ga Dr. Habib na neman samun gurbi a zuciyata, na kan vata lokaci ina tunaninsa.

Da abu yai gaba kuma sai ya kasance har waya muke vata lokaci muna yi, yana fayyace min irin yadda yake so na da irin rayuwar da yake tsara mana. Mutum ne da ya san wani abu wai ilimi, domin gaba daya karatun shi a kasar Greece ya yi shi, sannan kuma ya jima yana aiki a nan jami'ar Bayero.

Yau ne cikar ranar da muka yi alkawari da Dr. don haka tun bayan isha aka shaida min isowarsa. Sanye cikin atamfa mai karshen tsada na cimma sa a dakin baki kamar wancan karon.

Tun kamin in zauna ya ce,

"Kin san Allah Kausar tun kafin ranakun nan su cika tunanin amsar da za ki bani nake, don na ga kamar na yi miki tsufa".

Murmushi na yi, "Ashe akwai batun tsufa a cikin aure?' Ya rausayar da kai ya ce, "Halin 'yammatan wannan zamanin ke nan". Na ce, "Gara da ka ce 'yammata, amma ni ba 'yammata ba ce. Kada ka manta har da Fati a kasa". Ya lumshe ido ya fadada fara'arsa, "Ke nan na samu karvuwa ke nan?" A kunyace na ce, "Kusan haka". Ya ce,

"Bani da kalmar da zan yi miki godiya sai dai addu'ar Allah ya barmu tare, ya kuma nuna mana ranar da zamu kasance mamallakan juna, ameen".

Tun daga wannan lokacin muka shimfida sabuwar soyayya ni da Dr. sai dai ta fi karfi daga gare shi.

Ba zan ce bana son Habib ba, sai dai ni a gare ni zanyi aure ne kawai domin cika sunnar manzo da kuma farin cikin magabatana. Don zamana haka a gidan su Sagir baya da ma'ana, sai dai in ce ina zaune ne saboda makaranta, in haka ne to ranar da aka kare karatun fa?

A son Dr. nan da watanni biyu masu zuwa ayi komaia gama, amma ni na nuna na fi son sai na kare karatuna tukunna. To ba shi da zavi ban da ya bi nawa zavin.

Ina kan hanyar komawa gida daga makaranta, Dr. ya kira ni na amsa, ya ce, "Kina ina yanzu?'

"Ina kan hanyar komawa gida". Ya ce, "To gani nan yanzu zan kawo miki Saddik". Na ce, "Ka taho mishi da kayan sawa tun da yake week end ne sai ya kwana da Fatima". Ya ce, "To muna zuwa".

Saddik kyakkyawan yaro dan shekaru ukku, ya ce, "Ke ce sabuwar Momina da Daddy ya gaya mani?" Na ce, "Ni ce Saddik, ajinka nawa?" Ya ce, "Ajina ashirin ko Daddy?" Ya ce, "Mantawa ka yi ajinka tamanin". Dukkanmu muka sa dariya.

A gaskiya ina matukar sha'awar tsarin rayuwar Dr. mutum ne mai sassaukar rayuwa da rashin hayaniya. Komi cikin ilimi yake yin sa, don haka ne nake tunanin rayuwar aurenmu za ta tafi yadda nake so.

Kwananan Saddik biyu a waje na ya zo ya dauke shi, ni da Hajiya muka hada mishi tsaraba niki-niki, na shi da na Hajiyar Dr. Da daddare ya zo ya dauke shi suka tafi.

Na dawo makaranta ranar wata lahadi na cimma Hauwa'u ta zo yi min kwana biyu, da yake ta kare S.S.C.E dinta. Ba karamin jin dadin zuwanta na yi ba, abinki da dan uwa, ba ta da aiki sai rainon Fati. Ta same ni da daddare cikin sirri take gaya mani babanta ya dage ta ci gaba da karatu bayan ita kuma aure take son ayi mata.

Na ce da ita, "Daddy yana da gaskiya Hauwa'u, bakya ganin yadda auren zamanin nan ya zama ne? Yana so ya gina maki rayuwa mai inganci ne fiye da a mai da ke bazawara da quruciyarki. Don sakin yanzu mazan sun dauke shi ba a bakin komi ba. Masu karatun ma ya suka kare balle yara sabon jini irin ku?

Hauwa'u ta ce, "Bana tunanin Yusuf zai kasance daga cikin irin wadannan mazan Yaya Kausar, wallahi ya san abin da yake yi, kuma dan babban gida ne, ya yi min alkawarin barina in yi karatun har sai na ce ya ishe ni, amma bayan munyi aure".

Na ce, "Kin tabbata zai barkin Hauwa'u? A ina yake, kuma yaro ne ko babba ne?" Ta ce, "Yaro ne sabon jini bai fi twenty seven ba, a Kaduna yake aiki da matatar mai (Petrelium refinery). Ni dai wallahi ina son shi sosai, na taho wajen ki ne don in nemi shawara Yaya Kausar, don Momi ma ko zancen ba ta son in yi mata, wai na yi kankanta. Shin ana kankanta da aure ne?"

Na ce, "Ina laifin su? Suna son gina miki rayuwa ne, ya yi haquri ya kara miki lokaci atleast ki fara kammala ko da level I ne".

Ta ce,

"Na yarda da shawarar ki, kuma zan wa Yusuf bayani. Kin san kuwa kullum sai na yi mishi zancen ki?'

"Zancena kamar ya ya".

"Na kan ce mishi wata sister na ce wallahi, one year of marriage mijinta ya rasu ya barta da baby, a kullum ina tausaya mata".

Na ce, "Nima ina tausayawa kaina Hauwa'u, amma da na yi haquri ga shi Allah ya kawo min makwafin sa, duk da na san ba zai taba maye gurbin Sageer a zuciyata ba, sai dai ya kwatanta. Amma an ce a rashin uwa akan yi uwar daki".

Ta ce, "Ina ma na san ki lokacin da kuke tare da Sageer?" Na yi murmushi, moment din na dawo min fresh, kamar ya shiga cikin asibiti ne zai je ya dawo.

Hankalina ya tashi kwarai ainun, sai da na dangana da kuka sannan na ji sassaucin zuciyata. Hauwa'u ta ce, "Da na sani da ban yi miki maganar ba". Ita ma sai hawaye.

Fatima ta shigo ta kama hannuwana tana ja wai Uncle diddi..... Wato Uncle ya zo. Nan na duba wayata, ashe yana ta kira bamu ji ba daga ni har Hauwa'u. Na gyara fuskata na zizira kwalli don kar ya gane na yi kuka, amma sai da ya gane din.

Ya ce, "Idan ke matar mamaci ce, nima mijin marigayiya ne. Don haka hakan ba zai dame ni ba a yanzu Kausar, amma muddin muka yi aure nima za ki dulmiyani cikin damuwa". Bai jima ba ya tafi, dama ya zo kawo min wani littafi ne, tun da kuma am not in the mood ya san ko ya tsaya ayi hirar ba za ta yi armashi ba.

Hauwa'u ta koma da sati biyu Yaya Hajara ta yi min waya take sanar dani an kawo kudin aurenta daga gidan su Yusif, kuma Daddyn ta ya karva, amma biki sai ta kare level one.

Nan take na kira Hauwa'u muka yi ta murna, ta kuma hada ni da Yusuf din muka gaisa. Na ce da ita kuma kinga lokacin tunda na kare karatuna sai mu sha biki. Ta ce, "Biyu za'a hada dukkan mu". Na yi murmushi, don ni yanzu na fara tunanin har sai na kare NYSC ma.

Muna falo ni da Hajiya tana karatu da medicated glass dinta, cikin littafin (Ahlari), ni kuma ina nazarin takardun karatuna. Aka sanar dani ina da bako wai dan uwana ne daga Bujawa, na sa lulluvi na fita.

Na sha mamaki da na ga Sale dan Inna Laminde, a hannunshi jakar bakko ce taf da tsarabar su gujjiya, daddawa, aya, kwan zabbi da sauransu, ya ce duk a kawo min in ji Inna, kuma tana gaishe ni. Mun dade muna hira a dakin baki, na shiga cikin gida na samo mishi abinci ya ci muka ci gaba da hira.

Sai goshin magariba muka yi sallama ya juya, bayan na ba shi kudin mota.

Munyi waya da Mami a ranar take sanar dani ta koma karatu a jami'ar Chicago, sannan su Muslim duk sunyi nisa da karatu. Mukhlis ya kare karatunshi yana tare da su, na yi mata murna sosai for the achievements'din da suke ta samu a rayuwa. Sai dai ko da wasa bama yin zancen M.K daga ni har Mami, na rasa dalili.

To sai kuma ga bikin bamu shaidar karatu ya matso, dole Hajiya ta aika ma Yaya Hajara. Baba Lawal da Inna Laminde, da iyalinta duk sun halarta a gidan Justice ana i gobe za'a gudanar da taron, in son samu ne dole su Mami su halarta.

Ni dai da kaina na ki in sanarwa Mami, don na san muddin Mami ta ji dole su rankayo gaba dayan su. Tun da na samu na yakice M.K daga zuciyata bana marmarin duk wata hanya da za ta sake hada ni da shi, ko da a mafarki ne.

Sai dai shima kamar ya san ra'ayina. A cikin satin Mami da yara ne suka taho, har da Mukhlis. Take gaya min in yi haquri da rashin zuwan Daddy, yana New York din shi bai taho ba, sakamakon ayyukan office da suka yi mishi yawa, amma yana yi mani murna, digirin Allah ya sa rai aka yiwa.

Ta kawo wani dan kit ta bani, gift ne in ji shi. 'Yar akwatin samfurin ‘polo’, ba komi bane a ciki face biro, agogon hannu, nail cutter, da inki da za a durawa biron in ya kara, duka design din ‘polo’.

"Wata kyautar sai manya". Na fada cikin zuciyata. Idan kin ga dalolin da aka narkar wajen sayen wannan tarkacen banzan sai ki rike baki.

Su huda duk sun zama 'yammata, su Muslim an zama samari, 'ya'yan Mu'azzam Kanti, wadanda ba daya suke da sauran 'ya'ya ba, wurin ilimi, nutsuwa da kyawun sura.

A ranar da suka iso ne su Hauwa'u ma suka iso, gidan Hajiya ya zama ba masaka tsinke. Mami ta kara kyau da gogewa alamun komi na rayuwa zam-zam. Hajiya ke ba ta labarin Dr. Habib, don ita ba ta san wai M.K ya so ni a baya ba. Yo wane mai hankali ne ma zai yi wannan tunanin? Sai mu dabbobi (ni da M.K) marassa hankali marasa sanin ya kamata.

Koma dai mene ne ni dai alhamdulillahi tun da Allah ya kawo min miji dai-dai ni, dai-dai da rayuwata, wanda zai rike ni da mutunci har illa masha Allahu.

** **

[1/1, 14:07] Nrs Zainab A S: Filin 'Convocation Square da ke cikin jami'ar Bayero cike yake da motoci na zamani manya da kanana, su Dr. Habib na gefe suna kaiwa da kawowa kafin a fara taron. Taron da ya hada har da shugaban kasa da ministoci na ilimi, da wadanda ba na ilimin ba.

Nice mutum ta farko da aka kira a tsangayarmu, kuma ni kadai na fiddo second-class Honour (upper). Don haka idan ka dubi fuskar Dr. Habibu daga duba na farko, za ka fahimci tsantsar farin cikin da yake ciki, to haka 'yan uwa da masoyana cike suke da godiya ga Allah.

Mun dawo da daddare a dakina Mami ke tambaya ta wai wane ne shi wannan Dr. Habibun?

Na yi mata bayanin sa da abin da ya kamata ta sani game da shi. Ta ce, "Kin tabbatar kina son sa har cikin ranki?" Na ce, "Da bana son shi Mami ya za ai na bari har maganar aure ta gifta a tsakanin mu?" Mami ta yi murmushi mai qunshe da ma'anoni da dama, ta ce, "Uhm! Kausar ke nan, ban san yaushe za ki daina yin abubuwanki na quruciya ba".

"Mami ban gane ba?"

"Ba nufi na ki gane ba, amma ni na gane, damuwar ki yi auren ne don a daina yi miki kwakwazo ya sa kika fidda wannan mutumin. Amma ki nutsu ki bi komi a hankali, nima akwai abubuwan da nake dubawa ne a hankali komi za ya warware maki da yardar Allah".

Na yi nisa a cikin tunanin kalaman Mami, har ban san yaushe ta fita daga dakin ba ta barni da cunkushasshen tunani. Ta dauki Fatima dake ta rikici tasa zani goya ta a bayanta, suka nufi wurin Hajiya.

Wannan na nufin..... Mami ba ta goyon bayan tarayyata da Dr. Habibu? Wannan na nufin Dr. Habibu bai samu karvuwa a wajen Mami ba? Wannan na nufin ina shirme ne ba soyayya ba a ganin Mami?

To in ban yi auren ba me take nufi da in yi? Ba zan bari Mami ta yi min sakiyar da ba ruwa ba.

Sun koma America ranar lahadi, suka bar Mukhlis saboda za su je ya gaida dangi a Hadejia shi da Justice. Sai da suka je suka dawo sannan ya yi booking flight.

Ya leko dakina da daren ranar ya ce, "To Kausar da ALHERI, sai Allah ya sake dawo da mu". Na ce, "Safe journey Mukhlis". Muka dubi juna muka yi dariya cikin tuno quruciyar mu.

Da sati ya zagayo na soma hada kayana domin komawa Jos kamar yadda muka yi da Yaya Hajara. Hajiya ba ta ji dadi ba, to amma ba yadda za ta yi, domin zan fi samun sukuni a can din fiye da nan gidanta, ko dan Hauwa'u da ta lura tamu ta zo daya. Na kuma roqe ta da ta bani little Fatima in tafi da ita za mu dinga zuwa akai-akai tana ganin mu.

Hajiya ta ce, "Anya Kausar ba wani abu muka yi miki ba kike gudun mu?" Na yi dariya na ce, "Ni kuwa Hajiya me za ku yi min a duniyar nan da zan guje ku a kanshi?" Ta ce, "To ki bar min Fatima in dinga ganinta ina jin dadi". Dole dai don farin cikin Hajiya na tafi Jos ba tare da Fati ba.

Kwanana uku kacal Dr. ya zo, mun sha hira mun more. Da zai tafi ya ce ya dace cikin watan nan ya turo magabatansa a aje wata kwaqkwarar magana. Na ce, "Ba yanzu ba sai na kare NYSC, yanzu kuma da zancen ya je wa Justice ko Baffa Lawal duk cewa za su yi ayi auren yanzu. Ya vata rai sosai ya ce, "Amma dai ba haka muka yi dake ba ko Kausar?" Na ce, "Ka yi haquri Dr. gaggawar ce bana so". Ya ce, "Shekara guda muna tare Kausar ai ina tunanin ba mu yi garaje ba ko? Kina tunanin zan iya jiranki har wata shekarar again?" Na ce,

"Ba ka fahimce ni ba Dr. atleast in fara NYSC din ko ban gama ba idan na gamsu da lokacin da ya yi mani sai na yi maka magana". Ya yi shiru bai ce komi ba, haka muka rabu zuciyarshi babu dadi.

Bai yi fushi ba dai ya ci gaba da zuwa waje na a week-end, ni kuwa ina tunanin maganar Mami ne, na cewa in bi abin a hankali in yiwa zuciyata kyakkyawan jagoranci.

Posting dina na NYSC yfito,na samu an barni a arewa inda aka tura ni jihar Kaduna.

Na fara bautar kasa ta cikin kwanciyar hankali, a sakateriyar gwamnatin jihar Kaduna. Da muka samu sarari bayan watanni uku na je Kano na gai da Hajiya, na ga Fatima ta kara wayo. Dr. ya je har K.D wajen sau uku. Hajiya ta ce, "Haka tun barin ki gidan nan kafafunshi ba su bar kofar gidan nan ba yana zuwa yana gai da mu". Na ce, "Bawan Allah ke nan".

Na fiddo waya na kira shi na ce, "Yau dai gani a Kano". Ya ce, "Kai haba, to gani nan isowa yanzu".

Na cimma shi a dakin baki dauke da Fatima, tana ganin shi ta wangale baki ta ce, "Uncle!" Ya karve ta ya ce, "My dear Fatima matar Saddik". Na yi dariya na koma ciki don samo masa abin jika makoshi.

Mun nitsa da hira ya marairaice ya ce, "Saboda Allah Kausar ki tausaya mini a sanya ranar auren nan haka". Na ce, "Na amince Dr. Allah ya bamu sa'a".

Saboda farin ciki Dr. rungume ni ne kawai bai yi ba. Muka yi sallama ya tafi da niyyar a ranar zai kai zancen ga mahaifiyarsa don ta sanar da Baffaninsa.

Tun dai rabuwarmu da Dr. akan hakan to ban kara jin duriyarsa ba, har na koma Kaduna. Sai da na yi kwanaki bakwai da komawa ya kira ni a waya.

"Kin ji ni shiru ko Kausar?" Muryarshi kamar ta mai fama da mura, ban nuna mishi na damu ba, "Ah haba, na san yanayin aiki ne". Ya ba ta shiru na dan lokaci kafin daga bisani ya yi karfin halin cewa.

"Maganar dai ba za ta yiwu ta waya ba, zan zo on week end sai mu tattauna sosai". Jikina a masifar sanyaye na ce, "To". Don na fahimci ba lafiya ba.

Dr. bai zo ba sai ranar lahadi da yamma, har na fidda rai da zuwanshi, karfe biyar na yamma ya kira ni ya ce in same shi a inda muka saba tsayuwa.

Yana cikin motarshi Toyota Camry, kafarshi daya a ciki daya a waje, da waya a kunnenshi yana magana.

Tun daga nesa na fahimci Dr. ya rame ya fita hayyacinshi, kamar wanda ya yi kwana bakwai kan gadon asibiti.

Na bude daya kofar na shiga na zauna, tun kan na idasa zama na soma koro mishi tambayar dalilin ramar shi. Ya ce, "Kausar you are my life, idan na rasa ki ban san ya ya ragowar rayuwata za ta kasance ba.

Na samu Hajiya da zancen mu, amma ta nuna min ba ta amince ba....."

"Saboda me?" Na tambaye shi kirjina na dukan tara-tara ba uku ba.

Ya ce, "Zancen da zan yi miki ke nan, akwai wata yarinya Jamila, kanwar marigayiya matata (Madina), the same parents Da iyaye suka ga ya kamata na aura a can baya, har suka gabatar min da maganar. A lokacin na amince har na ce su jiraye ni zuwa wani lokaci, a lokacin ne kuma na gamu da ke, na ji nan duniya ke kadai nake so, a take kika sauya min akalar rayuwta

Don haka ranar da na kaima Hajiya zancen ki abin da ta fara tambaya na shi ne, ya ya kuma zancen Jamila? Hankalina ya tashi, don shaf na mance da ita, tun daga lokacin da kika shigo rayuwata.

Na yi kokarin in fahimtar da Hajiya amma ta kafe, karshe da na takura sai ta ce sai dai in hadaku ku biyu in aura".

Na yi saurin dako ido na dube shi, babu alamun wasa a zancen sa. Don haka na mai da kaina kasa na sunkuyar.

Ya ci gaba da cewa ba tare da ya saurari ta bakina ba, "Bani da zabi ban da in amince da hakan, saboda tsoron kar a hana mini aureki kwata-kwata.

Daga ni har shi shiru muka yi, cikin rashin sanin abin yi. Kai idan ka ganmu sai ka rantse mutuwar iyayenmu aka aiko mana. Daga baya Dr. ya bukaci jin ta bakina, na ce ya barni sai na yi shawara tukunna.

Da na je Jos a karshen satin nake gaya ma Yaya Hajara yadda mu kai da Dr. Ta ce, "Wannan shirme ne, sai dai in shima dama yana son yarinyar, in ban da haka babban mutum kamar shi, Dr. a ilimi a ce za'ayi mishi irin wannan auren ya yarda, ai ba zai yiwu ba. Shi dai yana so kawai. Don haka ya rage naki ki yarda ko a'a, tun da dai in kin ki shi ma wani mai matar dai za ki aura, tun da sunanki bazawara".

Na ce, "Ni fa Yaya Hajara ko dama can ba wata muguwar soyayya nake ma Dr. ba, kuma Mami ta fada dama dai kasancewar shi ba shi da matar ne ya fi jan ra'ayina. To tunda yanzu yana da mata ai ya zama daya da sauran zawarawana

Ta ce, "Abin da nake so da ke Lanto, ki dage da addu'a Allah ya kawo miki miji na gari, wanda zai so ki saboda Allah ba dan wannan baturiyar fatar taki ba. Maganar gaggawar yin aure ki ajiye ta a gefe ki fuskanci abin da ke gabanki, ki nemi zavin Allah amma ba zavin zuciyarki ba".

To da nasihar Yaya Hajra na yi amfani na soma yakice Dr. Habib, musamman da aka sha bikinshi da kanwar matarshi Jamila, suka tare a cikin gidajen malamai na old site. A yadda yake nufi shi ne, wai daga baya za a zo a yi nawa bikin idan na kare NYSC.

Don haushi na goge lambobinshi daga wayata, na canza layin waya duk saboda shi. Shima tun da ya soma dandanar zumar amaryarshi ko duriyar shi ban kara ji ba. Maza ke nan!!!

Don haka na dauki al'amarin mayaudaran mazan wannan zamani na aje a gefe, masu cika mace da dadin baki har sai ta ji kanta uwa mai kambun sarauniya, sannan su yakice ta.

Na kammala NYSC dina cikin nasara, na tattaro na dawo Jos cike da godiyar Allah.

A wannan satin zuwa Kano ya kama ni, domin zan karvi wasu takardu a makaranta. Don haka na nemi rakiyar Hauwa'u, wadda bikinta ya karato dai-dai wannan lokacin.

Mun tafi da alkawarta wa Yaya Hajara kwana uku kacal za mu yi mu dawo.

Muka shirya akwatun mu direba ya sanya a mota, da tsarabar himilin dankalin Jos da Yaya ta aike ma Hajiya. Tafiyar awanni uku kwarara ta kawo mu Kanon Dabo.

A gaskiya ina matukar son garin Kano, ko da yake a nan ne na yi kusan rabin rayuwata, na yi rayuwa da Mami da 'ya'yanta, na yi da Sageer. Ya ya kuwa ba zan so garin Kano ba?

Sanye nake da atamfa xclusive baka mai ratsin fari da ruwan kasa, yafe da mayafi ruwan kasa, wato brown. Na cure gashin kaina a cikin ribbom ya leko ta kasan kallabina, sai daukar ido yake. A kafafuna flat shoe ne kirar vincci, rataye da jakarshi su kuma farare ne.

Muka yi sallama a falon Hajiya, Hauwa'u ce a gaba ni a baya. Yana sanye da ruwan tokar shadda (Ghalila), karkar da ita kamar takarda, kamar yadda yake a al'adarshi (dinkin tazarce).

Ya kara fari ya kara mulmula kiba mai tsari da ban sha'awa. A fuskarshi gashin man's pride ne kwance lub-lub kamar ana shafe shi da mai, har sheki yake. Quruciyar shi ta dada bayyana a sarari.

Yana zaune kamar yadda yake zaman carpet dinsa, wato sai ya dauki kafa daya ya dora akan daya, M.K ne.

Wani irin motsi na ji har cikin kwakwalwata ya zagayo ya kashe lakar dake cikin gangar jikina. Ban yi tsammanin zan kara ganin shi a rayuwata ba, babu mamaki mafarki nake irin wanda na kan yi lokaci zuwa lokaci a kansa.

Jin sallamar mu da ya yi ya juyo a hankali, muka yiwa juna qurii da ido na 'yan dakikai. Ni na fara kawas da kai ganin ya kasa dauke ido a kaina.

Hajiya tana "Oyoyo! Da mutanen Jos". Muka karasa muka zauna a gefen ta.

Na russuna ina gai da Hajiya, sannan na dubi shashen da yake ba tare da na bari mun sake hada ido ba, na soma gaishe shi.

Ya yi gajeran murmushi, ya ce, "Ba zan amsa gaisuwar ki ba Kausar, sai dai in amsa na kanwarki".

Na yi wani irin murmushi cikin matukar jin nauyinsa, na ce,

"Dalili?"

Ya kai hannu ya shafi kwantacciyar kasumbarshi mai tsananin taushi da sheki. Ya ce,

"Zan iya tunawa, rabona da ke tun ta'aziyyar rasuwar marigayi, daga wannan lokacin ko waya ba ki taba yi min ba balle ki yi tunanin ki ziyarce mu. Alkawari, zumunci da aminci ba su ce hakan ba".

Hajiya ta ce, "Ba ku gayyace ta garin naku bane don haka ban ga laifinta ba, tun da dai ba fifffike za ta yi ta je mukun ba".

Ya yi murmushi, "Kin yarda da batun Hajiya Kausar?" Ni dai murmushi na yi. Ya ce, "To yanzu muna gayyatarki, ki bani passport dinki da na Hauwa'u, sai mu koma tare".

A wannan lokacin ne na yi magana, "Ka yi haquri Daddy, za ni amma ba yanzu ba, idan lokacin da na ga ya yi min ya yi zan sanar".

Ya ce, "Ba wani nan, ke dai bakya son yin nisa da bazawarinki malamin jami'a, shine kawai dalili".

Hauwa'u ta ce, "Wane malamin da tuni ya yi aurensa?" Bai ce uffan ba, sai dai an ce labarin zuciya a tambayi fuska.

Hidima sosai Hajiya ta shirya ma M.K, don tun da muka zo ba ta barmu mun huta ba. Wani aiki ne ya kawo shi Nigeria na tsayin sati guda, don haka dawainiyar shi na wuyan Hajiya.

Da daddare har dakina ya cimma ni, ina jera kaya cikin wardrove, Hauwa'u na daura ma Fatima pampers. Ya tsaya daga bakin kofa ta tokare hannunshi na dama jikin kofar.

Ya ce, "Kausar".

Na bar abin da nake na fuskance shi cikin rashin sukuni. Ya ce,

'Ko zan samu 'yan rakiya zuwa Abuja gobe da safe?"

Cikin mamakin sa na ce, "Kaima ka san hakan bai kamata ba". Ya ce, "Ko da Hauwa da little Fatima ne?' Na yi shiru don ban san amsar da zan ba shi ba.

Ya ce, "Already na sanar da Hajiya, kuma ta amince don haka ku shirya da wuri, by (6am) za mu dauki hanya".

Babu yadda na iya, a washegari muka tashi tun asuba muka kintsa, na samu Baby bag na shirya kayan Fatima da duk abin da za ta bukata. Karfe shida da rabi muna kan hanyar Abuja.

Hauwa'u da Fati da ke a kujerar baya ba'a jima da fara tafiya ba barci ya dauke su, sanyin A.C da ke cikin motar ya yi yawa. Ina so in ce da shi ya rage ko don Fati bana son yin magana. Ya yi min matukar kwarjini, don haka na samu kaina cikin rashin sukuni da rashin sakewa gaba daya.

Ba a jima ba na soma rawar dari nima, ya lura da hakan, ya mika hannu ya rage A.C, ya kuma ciro coat din da ke jikinshi ya mika mani, na amsa da sauri na zira hannayena. Ba mamaki don shi mazaunin kasar sanyi ne shi ya sa sanyin bai dame shi ba.

Mun yi nisa sosai har mun kusan shiga jihar Kaduna, ya dau C.D ya sanya na kira'ar Ahmad Suleyman, cikin suratul Taubah. Mun nitsa a sauraron karatun ya ce a hankali, "Kausar".

Na cira kai na dube shi ba tare da na amsa ba. Ya ce, "Lokaci ya yi da za mu daina yaudarar kanmu, bayan rasuwar Sageer na yi kokari matuka wajen ganin na fidda ke a raina, amma na gaza. Duk wasu hanyoyi da ya kamata in bi wurin kauce ma hakan na bi duk a banza, jikina yana bani we are meant for each other, amma idan kina ganin wani abu akasi da yadda na fada, to ki bi. Wallahi ba za ki yi nasara ba kamar yadda kika fara rasa mai shirin auren ki, alkawarin Allah ba ya tashi, amma idan kina ganin ba haka bane, to ki ci gaba da gwadawa".

Na yi shiru kamar ruwa ya cinye ni, alal hakika lokaci ya yi da ya kamata a ce ina gidan aure kamar kowa, sai dai ya ya za'ayi in auri mijin Mami? Wallahi ko zan rasa miji a duniya kamar yadda yake ikirari ba zan iya ba.

Ya yi murmushi, "Kina da hujjar ki Kausar, wato (Binta) nima kuma ina da tawa. Aure na da ke ba haramun bane, sai dai kawai ki ce min al'adarki ce ta haramta shi. Kausar I love you and I connot afford losing you, ki yi tunani sosai, ki taimakemu mu baiwa zuciyoyin mu abin da suke so da kanmu ba tun yau ba. Ina bayanki daga kowanne kalubale za ki fuskanta, balle ma Fatima ta yarje min aurenki ba tun yau ba, hankalinta da tunaninta ba daya bane da na sauran mata.

A da kam ta dau abin da zafi, amma yanzu ta fahimta. In gaya miki abin da ba ki sani ba, da yardarta da amincewar ta na taho nan neman auren ki a karo na biyu. Ta san cewa ko ba dade ko bajima idan na so zan iya kara auren ne, ta ce kuma da in kwaso mata wadda ba ta san halinta ba, sau dubu gara in aure ki. Tun da duk mun san halin juna, sai mu yi haqurin zama da junan mu. Don haka ni yanzu

amincewar ki kawai nake nema, Kausar ki dubi Allah kada wannan karon ma ki ce min a'a....."

Na ce, "M.K ‘give it a thought’, idan ita za ta iya ni ba zan iya ba"

.....”

"Saboda me?"

"Saboda uwata ce, kuma idan ita ta yarda su Mukhlis fa? Don Allah M.K ka bar wannan zancen, ka bar ni in yi aure na a inda zan samu kwanciyar hankali, ka barni in zauna da iyayen goyo na lafiya ba su cancanci wannan sakayyar daga gare ni ba".

Zancen ke nan har muka dawo gida, shi yana a bisa ra'ayinsa, nima ina a bisa nawa. Wanda daga baya abin ya zame mana rigima sosai.

Ban san ya aka yi ba, da daddare lokacin Justice ya dawo, Hajiya ta shigo dakina fuskarta babu annuri, ta ce, "In same su a dakin Justice".

Hankalina idan ya yi dubu ya tashi, ban san sanda na soma yarfe hawaye ba. Shi ke nan ya rabani da su kamar yadda nake gudu, ya rabani da martaba ta a idanun su.

Na yi sallama a kofar falon Justice ya amsa mini, sanye nake da bakar abaya da mayafinta, idanuwana sunyi zuru-zuru na rasa inda zan sa kaina saboda kunya.

M.K na fara yin tozali da shi, ga dukkan alamu shi kam ba abin da ya dame shi. Na koma gefen Hajiya na zauna ban san sanda hawaye suka keto mini ba, wane bayani zan yiwa su Hajiya da zai nuna babu hannuna a cikin wannan al'amari?

Na kai gefen mayafina ina sharewa, Justice ya ce, "Kausar? Haba Kausar? Ashe ba ki dauke mu iyayen ba kamar yadda mu muke tsammani? Na dauka zuwa yanzu da Fatima diyar Sageer take raye a duniya still kina nan a 'yarmu, ko da a ce kuwa kin yi aure ne a waje ba a cikin gida ba? Mene ne banbancin ki da Mamar Mukhlis da za mu ki yi miki auren da Allah ya halatta? Sai dai kuma idan bakya son Mu'azzam ne, to nan bamu da ta cewa".

Shiru na yi cikin rashin sanin abin cewa, ta wani bangaren kuma cike da mamakinsu kamar ba su san ya ya muke da Mami ba, ko ba su san wace ce Mami a gare ni ba. Su dinnan mutane ne extraordinary samun irinsu a wannan zamanin yana da wuya, mutane ne masu zuciya ta gari.

To har kwanakin da M.K ya diba zai yi a gida Nigeria suka cika bai samu wata kwaqkwarar amsa daga gare ni ba, daga shi har su Justice. Sai dai ya ce ya bani daga nan har wata mai zuwa in yi tunani na karshe, shi kam yana nan akan bakansa, babu gudu babu ja da baya.

[1/1, 14:07] Nrs Zainab A S: Na zauna zugum ni kadai a falo ina tunane-tunane yadda za mu yi rayuwa daga ni sai M.K cikin gidan nan. Ina jiyo motsin Baba Larai a kicin tana ta kiciniyar gyare-gyare.

Na dau waya na kira Hauwa'u muka shiga hira, da yake bikinta ya matso. Baba Larai ta leko daga kicin tana tambaya ta abin da zan ci. Na ce, "Ta bari kawai zan zo yanzu da kaina in yi girkin Daddy sai in ci, ta nemi wanda za ta ci kawai".

Bayan na kare shirya tebur na fada toilet din dake makale da dakina, na shirya cikin riga da siket din versace, ina tazar gashin kaina da hand-dryer na ji shigowar motar M.K.

Ko kamin in idasa in cimmasa ya bayyana cikin dakin, hannunshi na dama rike da brief case, ya yin da na hagun ke rike da falmaran din suit din shi, ya watsar da su ya iso gare ni ya miko hannu ya rungumo ni ta baya. Kafin ya juyo ni all overya hade da jikinshi yana sauke wani irin wahalallen numfashi. Atlast! Allah ya cika mana burinmu na shekara da shekaru, me za mu ce da shi ne, ban da mu gode masa.

Mun dade cikin wani hali, cikin wata irin rayuwa da ban taba tsintar kaina a ciki ba. Cikin wata duniya da ban taba shiga ba ko da a mafarki ne.

Har lokacin sallar magariba ta wuce bamu ankara ba, da kyar na kwaci kaina a hannun M.K muka fada toilet. Wanka na taimaka mishi ya yi kafin da mu hau tebur. Muna manne da juna kamar masu tsoron kada wani abu ya ratsa a tsakaninmu.

***

Idan wannan ita ce soyayya, to ban taba jin ta a SAGEER ba, idan wannan shi ne AURE, to ban taba dandana shi a SAGEER ba, idan wannan ita ce KAUNA, to ban taba dandanata a rayuwata ba.

At last! Allah subhana ya dube mu da kyakkyawar niyyar da ke zuciyoyin mu ya mallaka mana juna. Kanwa ta kar tsami kwannafi ya kwanta, sai fatan Allah ya ba da zuri'a masu albarka.

Ya kwantar da kai a masangalin wuyana, ya ci gaba da fassara min wane ne MU'AZZAM? Kuma mce ce soyayyar??

** **

Har muka share sati biyu muna varzar amarci ba mu sa Mami a ido ba, sai dai na san koma dai yaya ne cikin juriya da dauriya take, don cikar farin cikinmu. Alas! A yanzu kam ya samu nutsuwa ta har karshen rayuwar shi, wato mata biyun nan da yake matukar so a duniya da lahira (Mami da 'yarta).

Don haka a dawowar Mami wani abu wai shi KISHI ba mu san shi ba, Allah subhana ya yaye mana tun da ya dubi zuciyoyinmu na ALHERI ne ga junan mu.

A ranar da Mukhlis ya dawo da kwalinshi na Lauya, wato (LLB) a ranar ne na haifi Mukhtar (Justice) bayan shekara guda Mai sunan Hajiya ta biyo baya.

Ko da Mukhlis ya tsinkayi aurena da mahaifinshi jinjina kai ya yi, wato abin nan da ake cewa fadan da ya fi karfinka…... Sai dai kuma shima ya so hakan, kamar yadda ya ce fiye da a ce a waje Daddy ya je ya dauko musu.

Soyayyarshi da Fa'iza diyar Yaya Hajara kanwar Hauwa'u ta yi nisa, don haka shi din yanzu cikakken mutum ne mai hankali, ya daina duk abubuwan da yake yi na quruciya.

Bikin Hauwa'u ya tashi, don haka dukkannin mu muka tattaro muka yo Kano, daga nan muka wuce Jos inda Daddy ya samu halartar daurin aure. Ba kuma tare da zaton kowa ba ya biya sadakin Mukhlis da Fa'iza, don haka muka kece da biki babu kama hannun yaro.

Kowa yana sha'awar tsarin rayuwarmu ni da Mami da maigidanmu, sai fatan Allah ya ja da rai ya kuma raya mana zuri'a, ameen

Rayuwa ta ci gaba da mika mana yadda ba mu zata ba. Da ci gaba da nasarori ta fannoni da dama. Mu'azzam Kanti Mu'azzam mutum ne da kafin a samu kamarshi cikin dubban maza sai an tona. Ga dai adalci, ga kuma soyayyar, kulawa da iya tafiyar da rayuwar iyalinshi ta yadda babu wadda ta isa ta yi complaning kan cewa ba a kyauta mata ba.

Sai kuma ya yi katari da wata irin uwargida mai rahama a gare shi, har gobe ba zai daina alfahari da FATIMA-BINTA ba. Kamar yadda nima har jibi ba zan daina alfahari da ita a matsayi guda biyu da zuciyata ta bata ba, musamman da ta hada har da Fatima cikin iyalinta. Wato UWA kuma 'YAR UWA , sannan abokiyar shawara amma ba KISHIYA BA.

Masha Allahu laquwwata illa billah.

Takori

[1/1, 14:07] Nrs Zainab A S: Sati biyu da komawar shi sai ga Mami katsahan, babu zaton mu ba tsammani. Daga ni har Hajiya mun yi mamakin zuwan ta, kasancewar Daddy bai jima da komawa ba.

Mami ta same ni a dakina da daddare fuska babu sukuni, ta ce, "Wurin ki na zo Kausar". Na ce, "Ai gani Mami". Ta ce, "Kina son ki kashe min miji ko? Daga ni har ke mu yi asara?"

Na girgiza kai cikin tashin hankali. Ta ce, "In ba haka bane mene ne? Kin ce don ni kika ki auren M.K, to ni din gani na zo in shaida miki cewa, da amincewa ta da yarda ta....."

Na cire kai a hankali ina kallon ta, magana take baka da zuci (heart and soul). Na bude baki in yi magana amma harshena ya yi min nauyi.

Da kyar na samu furucin ya fito daga saman harshena, "Mami ke da bakin ki kike cewa kin amince in auri mijinki? Kina ganin hakan ya kamata?"

Idanun ta suka ciko ita ma, ta ce, "Ni na yarda da kaddara Kausar, na yarda idan tun fil'azal Allah ya rubuta ku mamallaka juna ne ni ban isa in ce a'a ba, sai rabo da haqki ya kawar dani kamar yadda Allah ya kawar da Sageer don ya nuna ku din ALKAWARIN Allah ne.

Kishi aikin banza ne Kausar, idan babu zuciyar mijin da kwanciyar hankalinsa me nake tutiya da shi? M.K ya rasa walwala, ya rasa sukuni, ya rasa kwanciyar hankalinsa duk a dalilin rashin amincewar ki. Da aje a kwaso min wata wadda ban sani ba ban san halinta ba gara mun zauna tare.

Bana son cewa da kike yi din nan wai saboda ni ba za ki auri Mu'azzam ba, alhalin kina son sa yana son ki, ba za ki jawo min abin da haqki zai yi sanadina ba".

Daga baya kuma ta koma lallashi, ni Mami har mamaki take bani, kamar ba mijinta ba. Irin wadannan matan ma'abota jin kan mazajen su da jiye musu feelings din su tsiraru ne a cikin al'umma.

Lallashin duniya da ban baki Mami ta yi har ta koma bani tausayi, don haka na ce, "Kamar yadda su Justice suka bani lokaci in yi tunani mai zurfi, ita ma ta bani lokaci".

Don haka har ta koma fushi take yi dani. Sai na gwammace ta yi ta fushin dani da dai in yi abin da daga baya zan zo ina nadama, wato auren M.K, duk kuwa da cewa shine kadai wanda zuciyata ke ciwo domin sa.

Na yi lalube cikin duniyar baki dayanta, mai ya sa ba zan so wani a duniya irin yadda nake son M.K ba? A iyaka lalube na babu, na gwada ban samu ba, domin ba ko wadanne mutane ne masu nasibin M.K ba.

Ya kama zuciyata ya dabaibaye da al'amarin da ba zan iya fassarawa ba, abin da zan iya cewa kawai shine, M.K nake so har kashi da vargo.

A karshen satin muka tattara muka koma Jos, ba tare da su Justice sun samu wata sahihiyar magana daga gare ni ba. Justice da Hajiya sai suka koma bani mamaki kamar ba su suka tsugun suka haifi Fatima-Binta ba.

Allah kareem! Mun je kasuwa ni da Hauwa'u mun yo ma Yaya Hajara cefanen sati, Hauwa'u ke jan motar, muna shigowa harabar gidan muka yi arba da wata galleliyar mota kirar ‘Giuleitta’ baka sidiq fake a rumfar adana motoci. Na dan tsaya ina kare ma motar kallo cikin nazari. Wane ne mamallakin wannan motar?

Tun kamin in shiga babban falo na soma jiyo muryar Inna Laminde da Baffa Lawal, na yi sallama Hauwa'u na biye dani rike da sauran ledoji. Gaba daya mutanen falon suka amsa sallama ta, a ya yin da idanuwana suka gane min wani abin al'ajabi.

Sanye take da bakar abaya da mayafinta kirar Omman, fara ce sol har ta soma jaja-jaja don fari, ba za ka ce ga hakikanin jinsin da ta fito ba tsakanin larabawa da turawa. Idan har ba idanuna ne suka yi min karya ba ita ce wacce ke jikin hotona da aka kira 'Grace' da nake kwana da wuni kallon hotonta.

Mutumin da ke zaune a gefen ta kuma ba shi da maraba da Baffana da Baffa Lawal, sai gogewar jiki da ya fi su. Sai na tsaya kikam a bakin kofa, ni ban shigo ba kuma ban koma ba.

Miqewa ta yi ta iso gare ni, ta rungume ni, kafin nan ni tuni na sulale a kasa sumammiya.

Ko da na dawo hayyacina ban gasgata al'amarin ba, in rungume ta in rungume mahaifina na rasa inda zan sa kaina don farin ciki. A karshe kuka muka saka dukkanin mu mai gigitarwa.

Ta yi min nuni da kanne na su biyar a zaune, daya bayan daya muka yi ta rungumar juna cikin matsananciyar kauna. Mus'ab, Khairat, Bilal, Nusaiba da Ikhlas.

Shi ya sa Ubangiji (S.W.A) ya ce, "Kar ku fidda rai daga rahamata". Addu'ata ta shekara da shekaru yau Allah ya karva, ba da dabarata ba, ba daga sanina ba, ya kawo min su baki daya a lokacin da ban zata ba.

Sai da komai ya lafa suka nemi mu tafi Kano wajen iyayen goyona. A can ne Hajiya ta yi wa su Mami waya, cikin kwanaki biyu rak sai ga su sun iso har da M.K.

Na samu kaina a karo na farko da yi wa M.K waya ina gaya mishi abin alherin da ya same ni, ya taya ni murna kwarai tun kamin su iso.

Don haka a tsakaninmu Mami ta shirya mana liyafar taya murna. Mun ci mun sha mun yi hani'an cikin godiyar Allah, Justice ya rufe taron da addu'a.

Gaba dayan mu Justice ya shirya mana motoci muka rankaya Abuja don gano muhallin su, da kuma kara dankon zumunci a tsakanin su.

** **

Gida ne babba, dai-dai misali a unguwar Maitama. Motoci har guda uku a rumfar adana motoci 'yan uban-ubansu. Rayuwar su cikin tsari mai ban sha'awa da sanin ciwon kai, daga su har 'ya'yansu.

Daga baya ne Abban yake gaya mana shi babban likita ne (Consultant) a babban asibitin Abuja bangaren zuciya.

Tarba ta bajinta Grace (Maimunatu) ta shiryawa Mami. M.K da iyayen su. Sai da aka ci aka sha aka yi nat, sannan Mami ta fara koro musu labarin tun ranar da Yaya Hajara ta kawo mata ni, har kawo aurena da Sageer, da rasuwar shi.

Kowanne ya jinjina, aka yi ma Sageer addu'a da fatan nima Allah ya kara min dangana.

Mami ta ce, "Ita kam tana son ta ji ya ya a kai suka tafi suka barni hannun Inna Laminde?" Suka dubi juna ita da mahaifina suka yi murmushi, kafin ya soma

Ni dai sunana Nasir, dan asalin garin Bujawa ne ta jihar Katsina, cikin maraici na uwa da uba muka taso ni da 'yan uwana, don haka ne muka taru muka dunqule cikin sanannan hadin kai da kaunar juna.

Baffa mai rasuwa shi ne babba, sai ni, Hajara ta biyo baya, sannan Lawal. Amadu autan mu shima ya rasu tun da quruciyarsa. Tun ina karami Allah bai sa min son sana'ar mu ta gado ba, wato kiwo da noma, wadda muka taso muka taras mahaifinmu na yi.

Na fi sha'awar in yi karatu, musamman da turawan wayar da kai suka iso Katsina, bayan kammala karatuna na sakandire na samu tallafin gwamnati zuwa kasar Bulgeria inda na fara karatun MBBS.

Ita wannan Grace (course mate) dina ce, ajinmu daya. Da farko abota ce a tsakanin mu wadda daga baya ta rikide ta koma soyayya, soyayya ce irin ta zamanin da, wadda babu ha'inci ko yaudara ko son zuciya a cikinta.

Sai dai na san ba yadda za'ayi dangina su mara min baya, saboda ba musulma ba ce kuma ba yarenmu ba, baturiya ce tsantsa. Yadda nake maraya haka take marainiya, ba uwa ba uba. Iyayenta sun rasu a wani Air-crash da ya rutsa da su a yankin kasar ‘Athens’ tun tana sakandire. Don haka muka nemi madaura aure suka daura mana, da yake Hausawa ne mazauna can.

Shekarun mu biyu da aure muka haifi Kausar a kasar Bulgeria, ni na zava mata suna Kausar, amma mahaifiyarta na kiran ta Lilian. Ban takurawa Grace cewa lallai sai ta musulunta ba, don na lura ba ra'ayinta bane, ta fi sha'awar addininta na kirista.

Da muka kare dukkan karatun mu, ya kama dole zan dawo gida. Na dauko Grace da Kausar muka taho, nan gidan Baffa mai rasuwa muka sauka. Suka yi ta ina aka saka ina aka aje da baturiya, sai dai bayani ya sauya daga lokacin da na sanar da su ita baturiyar matata ce, wannan 'yar kuma tawa ce, sannan Grace tana cikin addininta na kirista.

A nan gidan marigayi Baffa aka ware mana bangare guda dabayan gida da madafi, daki ciki da falo kamin Allah ya sa in samu aiki. Yadda ta yarda ta baro danginta, kasarta da daular da take ciki saboda soyayyar da take yi min, haka ni kuma na dauki alwashin kyautata ma rayuwar Grace duk yadda za'ayi dani kuwa, don kiri-kiri suka nuna min basa son ta.

Suka kira taron tattaunawa (meeting) a tsakanin su. Har da Hajara, akan auren da na jajibo musu. Ba yadda ba su yi dani ba kan in sake ta, ta koma kasarsu su sama min yarinya in aura na ki.

A cewar su wai za su bani diyar abokin mijin Hajara in aura, wadda wai ita ma kamar baturiya take, idan farar fata nake so. Na kafe akan cewa idan ba za su karvi Grace a matsayin matata ba, to su kore mu tare mu koma inda muka fito.

Don haka suka hade kai su da matansu suka fara yi ma Grace kisan mummuqe ida bana nan, su da 'ya'yansu da su Laminde suka hana ta zaman lafiya. Izayar yau daban ta gobe ta gobe daban. Da abin ya ishe ta ban sani ba tattara yanata-yanata ta yi tafiyar ta kasarsu ban sani ba, ba kuma tare da ta yi shawara dani ba. Nan ta ajiye Kausar wadda ke da shekaru biyu a lokacin.

Da dai na gane Grace ta barni saboda 'yan'uwana na qudiri aniyar nima ba za su sake ganina ba. Na yi iya cuku-cukuna na bi bayan Grace.

A gidan iyayenta na gado muka ci gaba da zama, muka koma karo karatu da hanyoyin kasuwanci kadan. Da na kare karatu na muka dawo gida Nigeria da yaranmu uku, da kwalayena na babban likitan zuciya, haka ita ma Grace. Muka sayi wannan gidan da muke ciki, muka kuma watsa takardun neman aiki. Na yi aiki da asibitoci da dama a nan Abuja, a karshe dai muka samu aiki da National Hospital wanda har yau muke a kai, to kun ji".

Mun dade muna tunanin muje mu dauko Kausar muna daga lokacin, sai yanzu da abubuwa suka yi mana dai-dai. Don haka ina godiya gare ki Hajiya Binta da iyayenki, mun gode Allah ya ji kan Sageer.

Kowa da ke falon ya ce, "Ameen". Kana ya zuki numfashi ya fesar. Mami da kanta ke sunkuye tana murzar 'yan yatsunta, ta dago a hankali ta dubi mahaifina, ta mai da kallon ta ga M.K suka qura ma juna ido tana nazarinsa, ganin yadda yake ta rama kullum a dalilin rashin kwanciyar hankalin soyayyar Kausar.

Ta ce, "A matsayina na marikiyar Kausar, idan na nemi wata alfarma za ku yi min Daddy?"

Kowa ya juyo ya dube ta, musamman M.K. Ya ce, "Wace alfarma ce Binta? Bana zaton akwai wani abu da na mallaka ko nake iko da shi da ba zan iya yi maku ba, haka nan bani da kalmar da zan yi muku godiya sai fatan Allah ya saka maku da mafificin alherinsa. Don haka ki fadi ko mene ne ina sauraron ki".

Ta yi murmushi, sannan ba tare da wani haufi ba ta ce, "So nake a aura ma M.K Kausar".

Gaba daya muka dago muka dube ta a tare, ji yake kamar ya miqe ya rungume matarsa. Doctor Naseer ya yi sakale yana kallon ta, ya ce, "Kan ki daya kuwa Binta?"

"Kaina daya Daddy, alfarma ce nake nema".

"Su suka ce miki suna son juna?"

Ta miqe a ya yin da ta sakala jakarta ta sunkuya ta dau Fatima wadda ta yi barci a jikin Hajiya, ta yi saman bane save da ita a kafada. Ta ce, "Ga su nan ka tambaye su, suna son juna ko ba sa so suke neman halaka kansu? Ita kullum a zaizaye,

shima kullum a zaizaye. Al'amarinsu ba na yau bane tun kamin aurenta na fari ne, tana kafa hujja da ni. To ni din na amince na yarda mu hadu mu rungume M.K ni da Kausar, amma ban san dalilinta na kin amincewa ba take neman hada kanta da ciwon zuciya".

To wai an ce labarin zuciya a tambayi fuska, kuma soyayya ba ta tsufa, sai dai masoyan su tsufa. To balle kuma mu da muke kan gavar ganiyar quruciyar mu.

Ba abin da za mu ce da Mami daga ni har M.K, wadda ke tsaye don nema mana farin ciki da zuciyarta daya, sai dai mu bi ta da addu'ar alheri.

A take Justice ya sanya hannu cikin aljihu ya kirgo sadaki a matsayinshi na waliyyin M.K, Baffa Lawal ya amsa. Aka ci gaba da gudanar da daurin auren kamar yadda shari'a ta tsara, bayan dukkanin mu mun bar falon.

** **

Babu kacaniyar biki, daurin aure kawai ya wadatar da daga amaryar har angon. Sai cuku-cukun neman ‘visa’ ta da M.K ya maida hankali, a karshen satin cikin qudurar Ubangiji muka daga New York.

Gida ne na hawan bene sama da kasa, a sama dakuna ne biyu da falo da toilet, to haka a kasan ma. Kicin din gidan da ya kasance guda daya makeken gaske ne a kasa yake, mun sauka birnin New York lafiya. M.K ya zava min zaman kasa Mami a sama, dakin su Nour ma a kasa yake.

Ni dai tun da muka iso aka nuna min daki, alwala na dauro bayan shower na sauke sallolin da ke kaina, na bi lafiyar gado bayan na kulle dakin, ban san halin da jama'ar gidan ke ciki ba.

Ya cimma Mami a dakin barcinsu tana kiciniyar sauya kayan jikinta zuwa nighties sanye yake cikin pyjamas masu taushi, bai taba yi mata kyau irin wannan ranar ba. Kai kayan ma bai taba sanya su ba sai yau da ya dauko sabuwar amarya (a tunaninta).

A take kumallon matan ya motsa, ko kallon shi ba ta yi ba balle ta nuna ta san Allah ya yi ruwan tsirarsa a dakin. Ta ci gaba da abin da take, tunaninta wai yau M.K ne zai hada jiki da wata mace bayan ita, macen ma wadda ta raina, ai abin da takaici. Sai hawaye shar-shar wasu na korar wasu.

"Mami ya zaki sa ni in yi abu, kuma ya zo ya dame ki? Da kin san hankalinki bai kwanta da al'amarin ba, don me za ki ce a yi?"

Ta kai hannu tana yarfe hawayenta, "Ka yi sacrifising saboda ni, ya ya ba zan yi sacrifising saboda kai ba?" Ta valle da kukan da yake girgiza masa zuciya.

Ba ya son ganin kukan mace, balle kukan Mami. Ya gigice ya rikice ya rasa inda zai sa kansa. Da zai iya sakin Kausar din a wannan daren da ya yi, amma ina, shima yasan ko bindiga za’a daura masa a makogaro ba zai taba yin hakan ba. Burin shi na shekara da shekaru yau Allah ya karba yaya zai yi sake da ni’imar da Allah yai masa?

Ganin halin da yake ciki ne ya sa ta share nata hawayen, ta ce, "Muje in raka ka wajen matarka".

Ya ce, "Ba inda za ni Mami, you are ok for me, hadama ce kurum irin tamu ta maza, amma ai kema kanki kin san kin ishe ni rayuwar duniya da lahira".

Ta dage sai ya tashi, in ba haka ba za ta fice ta bar mishi dakin. Ji ya yi kwata-kwata ba ya son Lanto, tun da hakan vacin rai ne ga Mami, to ya hakura.

"Kafin ki bar min dakin ni zan bar miki kayanki, amma na rantse Binta ba zan taba cin amanar ki ba".

Dariya ya ba ta sosai, M.K ya mai da kansa kamar wani yaron goye, sai dai kuma daga ganin shi ka san mahaukaciyar soyayyar amaryarshi na dawainiya da shi.

Ya juya ya fito ya koma nashi daki. Haka kawai ya hada ma kanshi zafi, ashe haka zama da mata biyun yake? Amma ya yarda ya amince cewa ba yin kansa ba ne yin Allah ne.

Kwanaki bakwai duk yadda Mamin ta yi don ta shirya mu abin ya ci tura, abin ma ya fi karfi daga gare ni, ko son ganin M.K bana yi, bana fitowa main parlour balle in hadu da M.K din. Na nemi duk wata soyayya da na ke mishi na rasa, kunyar Mami ta hana ni sukuni. Amma ga Muslim, Nour da Huda wannan abin farin ciki ne a wurin su, sun fada sun kara, "Daddy mun gode da dawo mana da Auntynmu, Mami ta gaya mana ba za ta sake komawagidan Hajiya ba, tun da ka aure ta".

Sai ya yi murmushi. Shi Mukhlis tuni ya koma Turkey haxo kwalin shi na biyu.

Ko abinci bana fitowa nema balle in yi arba da kwayar idon Mami, to amma ai an gudu ba a tsira ba, saboda ita da kanta take kawo mini ko Baba Larai. Ina ganin kaina as a betrayer, sai dai kuma duk da hakan koma ya ya ne na sani na hakikance, na tabbata dai-dai da rana daya ba zan iya daina son M.K ba.

Don haka har wa'adin da Daddyn ya deba a wurin aiki da sunan amarci ya cika, Mamin ta kasa qulla komi a tsakanin mu. Kuma a dai-dai lokacin ne bikin 'yar kanwar Justice ya kama a Hadejia, don haka ta samu mafaka ta yi amfani da damar ta bamu excuse na tafiya Nigeria biki ita da yara".

"Amma Mami ko Huda ce ki bar mini". Ta valla min harara. "Ba zan bar miki Huda ba, tunda kin zama mai kunnen kashi, ban isa in saki abu ba ki yi, ai sai ki yi ta yi. Ba ni kike kwasowa alhaki ba kanki ne.

Kausar aure ba abin wasa bane, duk yadda kike tunanin shi ya zarce. Kin yi watsin Allah-tsine da mijinki, ni ban yi kishin ba sai ke ce za ki yi halin tsiya. Tun da gidan kike so in bar miki ki sake da mijin ki, to ai ga shi nan zan bar miki".

"Wallahi ba haka bane Mami". Sai hawaye shar-shar!

Ta ce ba tare da ta dube ni ba, ta mai da hankalinta wajen troller da take shirya kaya. "To ya ya ne idan ba hakan bane?"

"Yanzu Mami me kike so in yi?"

"So nake ki kama mijinki, ki yi masa duka bin da mace ke yiwa mijinta. Sannan ne zan shirya da ke".

A haka ina ji ina gani suka tafi airport suka yi tafiyarsu.

** **

[1/1, 14:08] Nrs Zainab A S: Na zauna zugum ni kadai a falo ina tunane-tunane yadda za mu yi rayuwa daga ni sai M.K cikin gidan nan. Ina jiyo motsin Baba Larai a kicin tana ta kiciniyar gyare-gyare.

Na dau waya na kira Hauwa'u muka shiga hira, da yake bikinta ya matso. Baba Larai ta leko daga kicin tana tambaya ta abin da zan ci. Na ce, "Ta bari kawai zan zo yanzu da kaina in yi girkin Daddy sai in ci, ta nemi wanda za ta ci kawai".

Bayan na kare shirya tebur na fada toilet din dake makale da dakina, na shirya cikin riga da siket din versace, ina tazar gashin kaina da hand-dryer na ji shigowar motar M.K.

Ko kamin in idasa in cimmasa ya bayyana cikin dakin, hannunshi na dama rike da brief case, ya yin da na hagun ke rike da falmaran din suit din shi, ya watsar da su ya iso gare ni ya miko hannu ya rungumo ni ta baya. Kafin ya juyo ni all overya hade da jikinshi yana sauke wani irin wahalallen numfashi. Atlast! Allah ya cika mana burinmu na shekara da shekaru, me za mu ce da shi ne, ban da mu gode masa.

Mun dade cikin wani hali, cikin wata irin rayuwa da ban taba tsintar kaina a ciki ba. Cikin wata duniya da ban taba shiga ba ko da a mafarki ne.

Har lokacin sallar magariba ta wuce bamu ankara ba, da kyar na kwaci kaina a hannun M.K muka fada toilet. Wanka na taimaka mishi ya yi kafin da mu hau tebur. Muna manne da juna kamar masu tsoron kada wani abu ya ratsa a tsakaninmu.

***

Idan wannan ita ce soyayya, to ban taba jin ta a SAGEER ba, idan wannan shi ne AURE, to ban taba dandana shi a SAGEER ba, idan wannan ita ce KAUNA, to ban taba dandanata a rayuwata ba.

At last! Allah subhana ya dube mu da kyakkyawar niyyar da ke zuciyoyin mu ya mallaka mana juna. Kanwa ta kar tsami kwannafi ya kwanta, sai fatan Allah ya ba da zuri'a masu albarka.

Ya kwantar da kai a masangalin wuyana, ya ci gaba da fassara min wane ne MU'AZZAM? Kuma mce ce soyayyar??

** **

Har muka share sati biyu muna varzar amarci ba mu sa Mami a ido ba, sai dai na san koma dai yaya ne cikin juriya da dauriya take, don cikar farin cikinmu. Alas! A yanzu kam ya samu nutsuwa ta har karshen rayuwar shi, wato mata biyun nan da yake matukar so a duniya da lahira (Mami da 'yarta).

Don haka a dawowar Mami wani abu wai shi KISHI ba mu san shi ba, Allah subhana ya yaye mana tun da ya dubi zuciyoyinmu na ALHERI ne ga junan mu.

A ranar da Mukhlis ya dawo da kwalinshi na Lauya, wato (LLB) a ranar ne na haifi Mukhtar (Justice) bayan shekara guda Mai sunan Hajiya ta biyo baya.

Ko da Mukhlis ya tsinkayi aurena da mahaifinshi jinjina kai ya yi, wato abin nan da ake cewa fadan da ya fi karfinka…... Sai dai kuma shima ya so hakan, kamar yadda ya ce fiye da a ce a waje Daddy ya je ya dauko musu.

Soyayyarshi da Fa'iza diyar Yaya Hajara kanwar Hauwa'u ta yi nisa, don haka shi din yanzu cikakken mutum ne mai hankali, ya daina duk abubuwan da yake yi na quruciya.

Bikin Hauwa'u ya tashi, don haka dukkannin mu muka tattaro muka yo Kano, daga nan muka wuce Jos inda Daddy ya samu halartar daurin aure. Ba kuma tare da zaton kowa ba ya biya sadakin Mukhlis da Fa'iza, don haka muka kece da biki babu kama hannun yaro.

Kowa yana sha'awar tsarin rayuwarmu ni da Mami da maigidanmu, sai fatan Allah ya ja da rai ya kuma raya mana zuri'a, ameen

Rayuwa ta ci gaba da mika mana yadda ba mu zata ba. Da ci gaba da nasarori ta fannoni da dama. Mu'azzam Kanti Mu'azzam mutum ne da kafin a samu kamarshi cikin dubban maza sai an tona. Ga dai adalci, ga kuma soyayyar, kulawa da iya tafiyar da rayuwar iyalinshi ta yadda babu wadda ta isa ta yi complaning kan cewa ba a kyauta mata ba.

Sai kuma ya yi katari da wata irin uwargida mai rahama a gare shi, har gobe ba zai daina alfahari da FATIMA-BINTA ba. Kamar yadda nima har jibi ba zan daina alfahari da ita a matsayi guda biyu da zuciyata ta bata ba, musamman da ta hada har da Fatima cikin iyalinta. Wato UWA kuma 'YAR UWA , sannan abokiyar shawara amma ba KISHIYA BA.

Masha Allahu laquwwata illa billah.

Takori